Jeri daga cikin huɗubobin masallacin Annabi 1

# Tauhidi

## Daga cikin huɗubobin masallacin Annabi



Wallafar

**Dakta Abdulmuhsin bin Muhammad Al-ƙasim**

بلغة الهوسا

**TAUHIDI**

DAGA CIKIN HUƊUBOBIN

MASALLACIN ANNABI

**©Abdul-Muhsin ibnu Muhammad Al-Qasim, 1444h**

**Uorodheshaji wa Maktaba ya Kitaifa ya King Fahd Wakati wa uchapishaji**

**AL-QASIM, ABDUL-MUHSIN IBNU MUHAMMAD**

**Nguzo za Uislamu Kutoka Hotuba za Al-Masjid An-Nabawi : Lugha ya Kiswahili. / ABDUL-MUHSIN IBNU MUHAMMAD AL-QASIM – chapisho1. .- Al-Madina Al-Munawwarah, 1444h**

**Kurasa 167 ; ..cm**

**Redmark: 978-603-04-2803-8**

**1- Hotuba za kidini A. Anwani**

**DIWI 213 1444/1017**

**Nambari ya amana: 1444/1017**

**Redmark: 978-603-04-2803-8**

Domin sauke littafin ka bi kan wannan alamar (code)

a-alqasim.com

# TAUHIDI:
# DAGA CIKIN HUƊUBOBIN MASALLACIN ANNABI

RUBUTAWAR
DR. ABDULMUHSIN ƊAN MUHAMMAD ALƘASIM

# DA SUNAN ALLAH MAI RAHAMA MAI JIN ƘAI GABATARWA

Dukkan yabo da godiya sun tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga Annabinmu Muhammad, da iyalansa da sahabbansa baki ɗaya.

**Bayan haka:**

Lallai tauhidi shine farkon wajibi akan dukkan bayi, kuma saboda shine Allah ya hallici aljanu da mutane, kuma saboda shi ne Ya aiko ManzanninSa, kuma Ya saukar da littattafanSa kuma Ya sanya Aljannah makomar ma'abotansa, kuma saboda girman sha'aninsa ne ya zama mafi girman abinda ake kiran hallitu zuwa gare shi.

Saboda girman wannan ginshiƙin yasa na gabatar da huɗubobi akansa a masallacin Annabi, kuma na tsatstaratsu a cikin wannan littafin, kuma na sa masa suna «**TAUHIDI; DAGA HUƊUBOBIN MASSALACIN ANNABI**» kuma adadinsu ya kai huɗuba goma sha huɗu (14).

Allah nake roƙo Ya sa wannan littafi ya zama mai amfani, kuma Ya sanya shi don fuskarSa mai daraja.

tsira da amincin Allah su tabbata ga Annabinmu Muhammad da iyalansa da sahabbansa baki ɗaya.

# MUHIMMANCIN TAUHIDI(1)

Dukkan godiya sun tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman agajinSa da gafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrukan kawunanmu da miyagun ayukkanmu, wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, kuma wanda ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida cewa babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa lallai Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah yayi daɗin tsira a gare shi da iyalan gidansa da sahabbansa mai yawa da aminci cikakakke.

**Bayan haka:**

Yaku bayin Allah, kuji tsoron Allah haƙiƙanin tsoro, da tsoron Allah ne gannai da zukata suke haskaka, kuma dashi ne ake kankare kusakurai da zunnubbai.

**Ya ku Musulmai:**

Lallai ne Allah Yayi mana baiwa da addini wanda ya dace da fiɗira [tsarin da Allah Ya halicci bayinSa akai na yarda daShi da kaɗaitaShi] miƙaƙƙiya da hankula lafiyayyu, wanda ya dace da kowanne zamani da wuri, wanda ya haɗa tsakanin ilimi da ibada, kuma ya haɗa tsakanin magana, aiki da kudurcewa, kuma Allah baya karɓar wanin wannan addinin daga bayinsa:

﴿وَمَن يَبۡتَغِ غَيۡرَ ٱلۡإِسۡلَٰمِ دِينٗا فَلَن يُقۡبَلَ مِنۡهُ وَهُوَ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ﴾

((Duk wanda ya nemi wanin musulunci a matsayin addini , to lallai ba za'a karɓa daga gare shi ba, kuma a ranar lahira zai kasance cikin masu hasara)) [Aali-Imran:85].

A cikin wannan addini akwai wata kalma, duk wanda ya faɗeta alhali yana mai gasgatawa tun daga zuciyarsa kuma yayi aiki da abinda take wajabtawa yana mai neman yardar Allah, zai shiga Aljannah batareda hisabi ba ko azaba, «LAILAHA ILLALLAH» itace mafi daɗin zance, mafi falalar ayukka kuma mafi girman yanki na imani, wanda ya faɗeta da gaskiya zai ɗaukaka zuwa mafi girman mataki na addini, kuma furta ta kawai baya isa

(1) Wannnan huɗubar anyita ne a masallacin Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-, a ranar Juma'a, ashirin da huɗu ga watan Zhil-hijjah. shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da ashirin da biyu bayan Hijra.

ga shiga cikin musulunci ko wanzuwa acikinsa, banda haka yana wajaba musulmi ya kasance yasan ma'anarta kuma yayi aiki da abunda take wajabtawa; irin kore abokin tarayya da tabbatarda kaɗaitar Allah, tareda ƙudurce ingancin abinda ta ƙunsa kuma take wajabtawa.

Musulmi ya wajaba ya kasancewa mai gaskiya a cikin imaninsa da aƙidarsa, mai miƙa wuya ga Allah cikin hukunci da umurni da shari'a da ƙaddara, kuma baya kai buƙatunsa sai wurin Allah, baya neman yayewar baƙin cikinsa sai daga wurin Allah tsarki ya tabbata a gare Shi. Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَإِن يَمْسَسْكَ ٱللَّهُ بِضُرٍّ فَلَا كَاشِفَ لَهُۥٓ إِلَّا هُوَ ۖ وَإِن يَمْسَسْكَ بِخَيْرٍ فَهُوَ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ﴾

((kuma idan Allah ya shafeka da wata cuta babu mai iya yayeta sai Shi kaɗai, kuma idan ya shafeka da wani akhairi to Shi mai iko ne akan dukkan komai)) [Al-an`aam:17].

kuma roƙonSa Shi kaɗai -tsarki ya tabbata a gare Shi- ibada ce mai girma daga cikin ibadu mafiya falala; tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce:

«**Babu wani abu mai ƙima a wurin Allah kamar addu'a**»

(Ahmad ya ruwaito shi).

kuma Abdullahi ɗan Abbas -Allah Ya yarda dasu- yana cewa:

«Mafi falalar ibada itace: Addu'a».

idan bala`oi da damuwa suka same ka, kuma aka rufe mafita da hanyoyi a gareka; ka kira Mafi girma; domin yana bayarwa ga duk wanda ya kiraShi, kuma yana kare duk wanda ya fake daShi; tsira da Amicin Allah su tabbata a gare shi yake cema Ɗan Abbas -Allah ya ƙara masu yarda-:

**Idan zakayi roƙo ka roƙi Allah, idan zaka nemi taimako ka nemi taimakon Allah, kasani cewa koda dukkan al'umma zasu haɗu akan su amfaneka da wani abu, bazasu amfaneka ba sai da abinda Allah ya rubuta maka, kuma da zasu haɗu akan su cutarda kai da wani abu, bazasu cutarda kai ba saida abinda Allah ya rubuta akanka**»

(At-tirmizi ya ruwaito shi).

kada ka ƙyamaci roƙon Ubangijinka komai ƙanƙantan abu; Annabi -tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa:

«**ku roƙi Allah komai harda igiyar takalmi (idan ya tsinke); domin idan Allah bai sauƙaƙe shi ba, baya taɓa zama mai sauƙi**»

(Abu Ya'la ya ruwaito shi),

Amma shi mattace da wanda bashinan, basa iya anfanarda kansu ko

cutar da kansu ballantana sua amfanarda waninsu; kuma shi mamaci yana buƙatar wanda zai yi masa addu'a kamar yadda Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya umurcemu idan muka ziyarci kabur-buran musulmai, mu nema masu rahama kuma muyi masu addu'a ba wai mu nemi agaji daga wurinsu ba.

Ubangijinmu mai tsarki Ya siffantu da ji da gani, kuma yana daga cikin suka ga kaɗaituwarSa da halitta da raino kuma tauye kaɗaituwarSa da bauta: Ace ka sanya wasu ƴan tsakiya tsakaninka daShi a yin addu'a da roƙo alhali shine wanda yake cewa:

﴿ٱدۡعُونِيٓ أَسۡتَجِبۡ لَكُمۡۚ﴾

((Ku roƙe ni zan karɓa maku)) [Gaafir: 60]

kuma yanada cikin abunda yake warware kalmar Ikhlasi zubarda jini domin wanin Allah:

﴿قُلۡ إِنَّ صَلَاتِي وَنُسُكِي وَمَحۡيَايَ وَمَمَاتِي لِلَّهِ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ۞

لَا شَرِيكَ لَهُۥۖ وَبِذَٰلِكَ أُمِرۡتُ وَأَنَا۠ أَوَّلُ ٱلۡمُسۡلِمِينَ﴾

((Kace lallai sallata da yanka na da rayuwata da mutuwata duk na Allah ne Ubangijin talikai

bashida abokin tarayya, kuma da wannan aka umurceni kuma nine na farkon musulmai)) [Al-an`aam:162-163].

kuma ɗawafi kewayen ɗakin nan ƴantacce ibada ce wadda ta ƙunshi ƙanƙantar da kai ga Ubangijin ɗakin

﴿وَلۡيَطَّوَّفُواْ بِٱلۡبَيۡتِ ٱلۡعَتِيقِ﴾

((kuma suyi ɗawafi kewayen ɗakin nan ƴantacce)) [Al-hajj:29],

kuma yin ɗawafi don wanin Allah kamar ɗawafi ga ɗakunan ƙabari da ƙaburbura suna wajabta haramcin shiga Aljannah

kuma yin ranstuwa da Allah akan gaskiya a lokacin buƙatar yin hakan yana daga cikin girmamawa ga Ubangijin talikai, kuma yin rantsuwa da waninSa raini ne ga matsayin Mahallici Mai girma da ɗaukaka; shi yasa Annabi -tsira da amicin Allah su tabbata a gare shi- yake cewa:

«**Duk wanda yayi rantsuwa da wanin Allah haƙiƙa ya kafirta ko ya yi shirka**»

(At-tirmizi ya ruwaito shi).

kuma wanda ya riƙi wasu ababen ratayawa na tsari don tunkuɗe kanbun-baka ko jawo wani amfani ga kansa; lallai Zaɓaɓɓen Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya yi masa addu'ar kada Allah ya bashi abinda yake nema, kuma ya kamu da abinda yake tsoro, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Duk wanda ya rataya laya kada Allah ya cika masa burinsa**»

(Ahmad ya ruwaito shi),

kuma Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya kame daga yin mubayi'a ga wani mutum wanda yake rataye da laya; Uƙbatu ɗan Aamir Aljuhani -Allah Ya yarda da shi- yana cewa:

wasu mutane sunzo wurin Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-, sai ya karɓi mubayi'ar mutum tara (09) daga cikinsu amma ya kame daga karɓar mubayi'ar ɗayansu, sai suka ce: Ya Manzon Allah! ka karɓi mubayi'ar mutum tara amma ka ƙyale wannan? Sai yace: **yana rataye da laya ne**, sai mutumin ya shigar da hannunsa ya tsinketa, sai Manzon Allah ya karɓi mubayi'arsa kuma yace: **Duk wanda ya rataya laya lallai yayi shirka**»

(Ahmad ya ruwaito shi).

a lokacin tsanani da baƙin ciki, ka nemi mafaka wurin wanda yake Makaɗaici ne kuma Mai sakamako, kuma madala da kasancewarSa mai karɓawa, kuma duk wanda ya rataya rayuwarsa ga Allah kuma ya nemi biyan buƙatunsa daga gare Shi, ya fake gare Shi, ya miƙa dukkan lammurransa gare Shi; zai isar masa ga dukkan abinda ya roƙe Shi, kuma zai sauƙaƙe masa duk wata wahala, amma wanda ya dogara ga waninSa ko ya jingina zuwa ga iliminsa ko hankalinsa ko layoyinsa, kuma ya dogara ga dubararsa da ƙarfinsa; Allah zai jingina shi zuwa ga wannan abin kuma zai taɓar dashi. Ya ambata a cikin littafin "Taisirul Al-azizi Al-hamid" cewa:

«wannan abu ne sananne acikin dalilai na nassi da kuma gani a aikace»

kuma yana daga cikin makaman rosa addini: zuwa wurin masu sihiri da rufaido, da tambayar bokaye da masu tsibbu; Allah Mai girma da daukaka ya ce:

﴿وَمَا يُعَلِّمَانِ مِنْ أَحَدٍ حَتَّىٰ يَقُولَا إِنَّمَا نَحْنُ فِتْنَةٌ فَلَا تَكْفُرْ﴾

((kuma basa koyama kowa -sihiri- sai sun ce masa mu fitina ne saboda kada ka kafurta)) [Al-baƙarah:102],

yazo a cikin hadisi:

«**duk wanda yaje gun boka ko mai tsibbu kuma ya gasgata abinda yake faɗi, tabbas ya kafircewa abinda aka saukar ga Muhammad**» (Ahmad ya ruwaito shi).

kuma duk wanda ya nemi ɗan sihiri suyi mugun abu ga waninsa, lallai sharrin muguntarsa zai dawo akansa, Allah ta'ala ya ce:

﴿وَلَا يَحِيقُ ٱلْمَكْرُ ٱلسَّيِّئُ إِلَّا بِأَهْلِهِۦ﴾

((kuma lallai mugun makirci baya faɗawa sai akan ma'abotansa)) [Faaɗir:43].

kuma ba'a yaye duhu da wani duhu, ana tunkuɗe bala`in sihiri ne da hasken Alƙur'ani bada wani sihirin ba kamarsa

﴿وَنُنَزِّلُ مِنَ ٱلْقُرْءَانِ مَا هُوَ شِفَآءٌ وَرَحْمَةٌ لِّلْمُؤْمِنِينَ﴾

((Kuma muna saukewa daga Alƙur'ani abinda yake waraka ne da rahama ga muminai)) [Al-isra`:82].

ya kai musulmi ka kiyaye aƙidarka; domin itace mafi tsadar abinda ka mallaka, kuma mafi girman abunda ka tanada, kuma ita shirka tana bice hasken fiɗra, kuma sababi ce ta rashin arziki da galabar maƙiya akan mutum.

Ina neman tsarin Allah daga shaidan jefaffe.

﴿فَٱسْتَمْسِكْ بِٱلَّذِىٓ أُوحِىَ إِلَيْكَ ۖ إِنَّكَ عَلَىٰ صِرَٰطٍ مُّسْتَقِيمٍ ❁ وَإِنَّهُۥ لَذِكْرٌ لَّكَ وَلِقَوْمِكَ ۖ وَسَوْفَ تُسْـَٔلُونَ﴾

((kuma kayi riƙo da abinda aka wahayinsa zuwa gareka, lallai kai kana bisa hanya madai-daiciya, kuma shi wahayi abun ambato ne (na ɗaukaka) gareka da mutanenka kuma za'a tambayeku)) [Az-zukhruf: 43-44].

Allah yasa mani albarka tareda ku a cikin Alƙur'ani mai girma.

## HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gare Shi akan samun dacewa da kuma ni'imominSa, kuma ina shaidawa cewa babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya ina mai girmama al'amarinSa, kuma ina shaidawa cewa Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, tsira da amincin Allah mai yawa su tabbata gare shi da iyalansa da sahabbansa.

**Bayan haka, ya ku musulmai:**

Ginshiƙi na biyu bayan kalmomi biyu na shahada Sallah ce; kuma itace farkon abinda za'a fara yiwa bawa hisabi akai ranar ƙiyama. kada kayi sakaci da yinta a cikin jam'i tareda musulmai, kada ka zaɓi kasala sama ga biyayyar Ubangijin talikai, kada ka ƙyamaci abinda Allah ya tanadarma masu kiyayeta na kyaututtuka masu tarin yawa, kuma gwar-gwadon alaƙar bawa daUbangijinsa ake buɗe masa ƙofofin alheiri, ka nisanci zunubbai da laifuka; domin suna sa jin wahalar ayukkan ɗa'a.

kuma a cikin kira zuwaga Allah akwai ƙarfafawa ga addinin Allah, kuma koyi ne da Annabawa da Manzanni, kuma ita ce mafi kyawon zance kuma mafi karamci, kuma ka binciki cuta kayi amfani da maganin daya dace da ita, ka fahimci yanayin waɗanda kake kira da abinda suke buƙata, ka ɗauki damuwar mutane kada ka ɗorama mutane damuwarka.

ka yawaita yin tuba da neman gafara, domin abinda ake hukunci da shi shine samun kamala a ƙarshe ba samuwar tawaya a farko ba, kuma alamar karɓar aiki mai kyau shine yin wani aikin mai kyau bayansa. Ƙatada -Allah Ya jiƙansa- yana cewa

«Lallai wannan Alƙur'anin yana nuna maku cututtukanku da maganinku, amma cutarku itace zunubbai kuma neman gafara shine maganinku».

kuma wannan shine sababin shiga Aljannah, da kuma samun ƙarin ƙarfi da jin daɗi mai kyau, da tunkuɗe bala'i. Abul- Minhal -Allah Ya jiƙansa- yana cewa:

«Babu maƙwabci da zaiyi maƙwabtaka da bawa a ƙabarinsa mafi soyuwa a gare shi irin istigfari».

sannan ku sani cewa, lallai Allah ya umurceku da yin Salati da sallama ga AnnabinSa....

# RIƘO DA TAUHIDI(1)

Godiya ta tabbata ga Allah wanda Ya kaɗaita da cikakkiyar kamala, dawwama, buwaya da jin isa da girma, wanda Ya siffantu da mafi kyawawan sifoffi da sunaye, wanda Ya tsarkaka daga kamanceceniya da tamka, godita ta tabbata a gare Shi akan kyaututtukanSa masu yawa da abinda yake bayarwa.

kuma ina shaida cewa tabbas babu abin bauta da gaskiya sai Shi, baShida abokin tarayya, Shine masanin abinda yake a ɓoye da abinda ake tattauna.

kuma ina shaida cewa  Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, wanda aka aiko da hanya fara, da shari'a mai haske, yabon Allah ya tabbata a gare shi da iyalan gidansa da sahabbansa masu tsoron Allah, yabo tare da aminci tare dawwamammu har zuwa ranar tayarda hallitu da yin sakamako.

**Bayan haka:**

Ya ku bayin Allah kuji tsoron Allah haƙiƙanin tsoro, kuma kuyi aiki don ranar tonon asiri, ranarda za'a bayyan ababen da aka ɓoye cikin ƙiraza da zukata.

**Yaku Musulmai:**

Haƙiƙa, mutane sun kasance al'umma guda ɗaya akan gaskiya saboda abinda Allah ya saka a cikinsu na fiɗra ta Musulunci, kuma saboda abinda ya basu na shiriya da bayani, amma bayan wani lokaci mai tsawo sai abinda aka basu na alamomin musulunci suka shuɗe, wasu ababe masu muni dasuka ɓata aƙida da gurɓata tsaftarta  suka shigo masu, sai suka awka a cikin shirka kuma suka juyarda wasu nau`oin ibada zuwa ga wanin Allah, sai kawunansu suka rarrabu kuma kalmominsu suka saɓawa juna, sai Allah Ya aiko da Manzanni suna masu bushara da gargaɗi; don kada mutane su samu wata hujja da zasu gabatarma Allah bayan zuwan Manzanin, kuma aka aiko Manzonmu Muhammad -tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- zuwaga wata al'umma wadda take rayuwa cikin duhun jahilci, da makauniyar ɓata; shirka itace ginshiƙin addininta, gumaka kuma sune ababen bautarta kuma sune jagororinta, sai ya kirasu zuwaga addini

(1) Wannnan huɗubar anyita ne a masallacin Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- a ranar Juma'a, ashirin da huɗu ga watan Zhil-ƙa'ada. shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da goma sha tara bayan hijra.

miƙaƙƙe wanda dalilai da ayoyi da hujojji suka tabbatar dashi.

Ya ku bayin Allah, ana yiwa muminai zance akan aƙida ne; domin su ƙara imani sama da wanda suke dashi; kamar yadda Maɗaukakin Sarki yace:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ ءَامِنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَٱلۡكِتَٰبِ ٱلَّذِي نَزَّلَ عَلَىٰ رَسُولِهِۦ وَٱلۡكِتَٰبِ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ مِن قَبۡلُۚ﴾

((Ya ku waɗanda kukayi imani, kuyi imani da Allah da ManzonSa, da littafin daya saukar ga ManzonSa, da littattaffan daya saukar daga gabani)) [An-nisa`:136],

kuma domin su samu natsuwa da inganta addininsu kuma su nisanci tawaya ko tangarɗa a cikinsa, bandama haka Allah yayima AnnabawanSa da ManzanninSa umurni da suyi watsi da shirka kuma suyi bara'a daga gareta da ma'abotanta. -tareda cewa Allah ya tsare su daga gareta-; Allah mai girma da ɗaukaka ya ce:

﴿وَإِذۡ بَوَّأۡنَا لِإِبۡرَٰهِيمَ مَكَانَ ٱلۡبَيۡتِ أَن لَّا تُشۡرِكۡ بِي شَيۡـٔٗا وَطَهِّرۡ بَيۡتِيَ لِلطَّآئِفِينَ وَٱلۡقَآئِمِينَ وَٱلرُّكَّعِ ٱلسُّجُودِ﴾

((kuma a lokacin da muka nunama Ibrahim wurin Ɗaki, -muka ce masa- kada ka haɗani da komai wurin bauta, kuma ka tsarkake ƊakiNa don masu ɗawafi da masu tsayuwa da masu ruku'i da sujada)) [Al-hajj:26].

kuma Ubangiji mai girma da ɗaukaka yace da mafi falala kuma zaɓaɓɓe daga cikin halittarSa: Muhammad tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi:

﴿وَٱدۡعُ إِلَىٰ رَبِّكَۖ وَلَا تَكُونَنَّ مِنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ﴾

((kuma kayi kira zuwaga Ubangijinka, kuma kada ka kasance cikin masu haɗa Shi da wani)) [Al-ƙasas: 87].

kuma ya ce:

﴿فَلَا تَدۡعُ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ فَتَكُونَ مِنَ ٱلۡمُعَذَّبِينَ﴾

((kada ka kira wani abin bauta tareda Allah, don kada ka kasance cikin waɗanda ake yima azaba)) [Ash-shuara`i:213].

kuma anyima ma'abota ɓata magana akanta domin su dawo zuwa ga hanyar shiriya. Allah mai girman sha'ani ya ce:

﴿قُلۡ يَٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ تَعَالَوۡاْ إِلَىٰ كَلِمَةٖ سَوَآءِۭ بَيۡنَنَا وَبَيۡنَكُمۡ أَلَّا نَعۡبُدَ إِلَّا ٱللَّهَ وَلَا نُشۡرِكَ بِهِۦ شَيۡـٔٗا وَلَا يَتَّخِذَ بَعۡضُنَا بَعۡضًا أَرۡبَابٗا مِّن دُونِ ٱللَّهِۚ فَإِن تَوَلَّوۡاْ فَقُولُواْ ٱشۡهَدُواْ بِأَنَّا مُسۡلِمُونَ﴾

((Yaku waɗanda aka baiwa littafi, ku taho zuwa ga wata kalma mai dai-daitawa tsakaninmu daku; kada mu bautawa kowa sai Allah, kuma kada mu haɗa wani abu tareda Shi, kuma kada sashinmu ya riƙi sashi abin bauta koma bayan Allah, idan suka juya baya sai ku kuce: ku shaida lallai mu musulmai ne)) [Aali-Imran:64].

Ai babu mamaki a cikin wannan ya ku Musulmai; domin kuwa kaɗaita Allah da bauta shine ginshiƙin addini kuma shine jagoran lamarinsa, akansa ne aka kafa Alƙibla kuma akansa aka gina hanyar Musulunci, shine farkon umurni a cikin littafin Allah, kuma hani daga haɗa Allah da wani a cikin bauta shine hani na farko a cikin littafinSa; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱعۡبُدُواْ رَبَّكُمُ ٱلَّذِي خَلَقَكُمۡ وَٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَتَّقُونَ ۞ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلۡأَرۡضَ فِرَٰشٗا وَٱلسَّمَآءَ بِنَآءٗ وَأَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَأَخۡرَجَ بِهِۦ مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ رِزۡقٗا لَّكُمۡۖ فَلَا تَجۡعَلُواْ لِلَّهِ أَندَادٗا وَأَنتُمۡ تَعۡلَمُونَ﴾

((Ya ku mutane ku bautawa Ubangijinku wanda ya halicce ku kuma Ya halicci waɗanda suke kabaninku domin ku samu jin tsoronSa.

Wanda Ya sanya maku ƙasa shimfiɗa, kuma sama rufi, kuma Ya saukar da ruwa daga sama, sa'annan Ya fitar da abinci daga 'ya'yan itace don su zama arziki a gareku. Saboda haka kada ku sanya ma Allah wasu kishiyoyi, alhali kuwa kuna sane)) [Al-baƙarah: 21-22].

kuma shiga a cikin addini baya inganta saida bayyanarda kaɗaituwar Allah, kuma shine ƙarshen abinda musulmi yake fita dashi daga duniya;

Manzon Allah tsira da amicin Allah su tabbata a gare shi yana cewa: «**ku laƙƙanama matattunku: La ila ha illa Allah**».

(Muslim ya ruwaito shi),

kuma faɗawa a cikin kishiyarsa -kishiyar Tauhidi- yafi girman laifi sama da kisan `ƴa`ƴa,

Abdullahi ɗan Mas'ud -Allah ya ƙara masa yarda- yana cewa:

«Na tambayi Manzon Allah tsira da amicin Allah su tabbata a gare shi: Wane zunubi ne yafi girma a wurin Allah? Sai yace: **Ka sanyama Allah kishiya alhali kuwa shine ya halliceka**, sai nace: Sannan mene kuma? Sai yace: **Ka kashe ɗanka saboda tsoron kada yaci abinci tareda kai**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi)

wannan yasa aka ƙarfafa hani daga shirka a cikin Alƙur'ani kuma akayita maimaita umurni da Tauhidi, Ubangiji yayi bayaninsa kuma ya ƙara yin bayani, kuma ya buga misalai akan haka.

kuma umurni da bautar Allah shine farkon kiran Manzanni; da shine badaɗayin Allah Annabi Ibrahim ya fara kiran mahaifinsa zuwa gare shi.

﴿يَٰٓأَبَتِ لِمَ تَعۡبُدُ مَا لَا يَسۡمَعُ وَلَا يُبۡصِرُ وَلَا يُغۡنِي عَنكَ شَيۡـٔٗا﴾

((Ya baba na don me ka ke bautama abin da ba ya ji ba ya gani, kuma ba zai amfana maka komai ba,)) [Maryam:42],

kuma saboda girman sha'anin tauhidi, Annabinmu Muhammad -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya shafe tsawon shekaru goma yana kiran mutane zuwa gare shi kafin a farlanta sauran farillai.

kuma Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yana shiryarda masu da'awa cewa su sanya tauhidi yazamo shine farkon abinda zasu fara kira zuwa gare shi, a lokacin da Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya tura Mu'az -Allah Ya yarda dashi- zuwa Yaman sai yace masa:

«**Lallai kai zaka je wurin wasu mutane ma'abota littafi, ka kirasu zuwa shaidawa cewa babu abun bautawa da gaskiya sai Allah, kuma ni Manzon Allah ne**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

kuma jagoran masu kaɗaita Allah, Annabi Ibrahim ya roƙi UbangijinSa yace:

﴿وَٱجۡنُبۡنِي وَبَنِيَّ أَن نَّعۡبُدَ ٱلۡأَصۡنَامَ﴾

((Kuma ka nisantar dani da ƴaƴana daga bautar gumaka)) [Ibrahim:35],

Ibrahim At-taimi -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«Wanene zai iya samun natsuwar cewa bala'i bazai same shi ba bayan Ibrahim»

kuma tabbas Annabawa sunyima `ƴa`ƴansu wasiyawar tabbata akan addinin gaskiya da tsaftatacciyar aƙida har zuwa lokacin mutuwa

﴿وَوَصَّىٰ بِهَآ إِبۡرَٰهِـۧمُ بَنِيهِ وَيَعۡقُوبُ يَٰبَنِيَّ إِنَّ ٱللَّهَ ٱصۡطَفَىٰ لَكُمُ ٱلدِّينَ
فَلَا تَمُوتُنَّ إِلَّا وَأَنتُم مُّسۡلِمُونَ﴾

((Kuma lbrahim ya yi wasiyya da ita ga `ƴa`ƴansa, kuma Ya'aƙub (ya yi wasiyya, suka ce:) Ya `ƴa`ƴanmu! Lallai ne, Allah Ya zaɓa maku addini don

haka kada ku mutu, lallai, face kuna Musulmai)) [Al-baƙarah:132],

kuma akan tauhidi ne Annabawa suka tambayi `ƴa`ƴansu alhali lokacin suna akan shinfiɗar rashin lafiyar ajali

﴿أَمۡ كُنتُمۡ شُهَدَآءَ إِذۡ حَضَرَ يَعۡقُوبَ ٱلۡمَوۡتُ إِذۡ قَالَ لِبَنِيهِ مَا تَعۡبُدُونَ مِنۢ بَعۡدِيۖ
قَالُواْ نَعۡبُدُ إِلَٰهَكَ وَإِلَٰهَ ءَابَآئِكَ إِبۡرَٰهِـۧمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ إِلَٰهٗا وَٰحِدٗا وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ﴾

((Ko kun kasance halarce a lokacin da mutuwa tazowa Ya'aƙub, a lokacin da ya ce ma `ƴa`ƴansa: Mene ne zaku bautama a bayana? Suka ce: Zamu bauta wa Abin bautarka kuma Abin bautar iyayenka lbrahim da lsma'ila da Is'haƙa, Ubangiji Guda, kuma mu a gare Shi masu miƙa wuya ne)) [Al-baƙarah:133],

**Yaku musulmai:**

shiriya itace mafi girman abun nema, kuma samunta shine mafi darajar baiwa, kuma lafiyayyar aƙida itace mafaka mai aminci a lokacin tsanani

﴿ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَلَمۡ يَلۡبِسُوٓاْ إِيمَٰنَهُم بِظُلۡمٍ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلۡأَمۡنُ وَهُم مُّهۡتَدُونَ﴾

((Waɗanda suka yi imani, kuma ba su gauraya imaninsu da zalunci ba, waɗannan suna da aminci, kuma su ne shiryayyu)) [Al-an`aam:82],

kuma fakewa ga Allah Shi kaɗai a lokacin ambaliyar fitintinu da jarabawa da damuwa itace mafita; Allah mai girma da ɗaukaka ya ce:

﴿وَذَا ٱلنُّونِ إِذ ذَّهَبَ مُغَٰضِبٗا فَظَنَّ أَن لَّن نَّقۡدِرَ عَلَيۡهِ فَنَادَىٰ فِي ٱلظُّلُمَٰتِ
أَن لَّآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنتَ سُبۡحَٰنَكَ إِنِّي كُنتُ مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ *
فَٱسۡتَجَبۡنَا لَهُۥ وَنَجَّيۡنَٰهُ مِنَ ٱلۡغَمِّۚ وَكَذَٰلِكَ نُـۨجِي ٱلۡمُؤۡمِنِينَ﴾

((Kuma ma'abocin kifi a lokacinda da ya tafi yana mai fushi, sai ya yi zaton cewa ba za Mu ƙuntata masa ba. Sai ya yi kira a cikin duffai cewa, babu abin bautawa face Kai. Tsarki ya tabbata a gare Ka. Lallai ne ni, na kasance daga cikin azzalumai

Sai Muka amsa masa kuma Muka tseratar dashi daga baƙin ciki. Kamar haka ne Muke tserarda masu imani)) [Al-anbiya`:87-88].

tsaftar aƙida yana gyara niyya, kuma yana yin linzami ga son zuciya kuma yana sa albarka a cikin aiki kuma ya wanzar da ambato; ta yaya za'a haɗa labarin Abu Jahal da Abubakar? Kuma ina za`a haɗa matsayin Bilal da

Abu Lahab ta fuskar nasaba?! Ba`a karɓar fansa don asarar addini koda da zinari ne

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَمَاتُواْ وَهُمۡ كُفَّارٞ فَلَن يُقۡبَلَ مِنۡ أَحَدِهِم مِّلۡءُ ٱلۡأَرۡضِ ذَهَبٗا وَلَوِ ٱفۡتَدَىٰ بِهِۦٓۗ﴾

((Tabbas waɗanda suka kafirta kuma suka mutu suna kafirai, baza'a karɓi fansar dayansu ba koda da ya nemi yin fansa da cikin ƙasa da zinari)) [Aali-Imran:91].

**Yaku musulmai:**

Saboda tsayarda tauhidi ne aka gina ɗakin Allah `ƴantacce, mutane suna bibiyar juna wurin zuwa hajjinsa zamani bayan zamani, musulmai suna tsere da juna don isa farfajiyarsa, a cikin maƙwabataka dashi akwai imani kuma a cikin farfajiyarsa akwai aminci da natsuwa

﴿وَإِذۡ بَوَّأۡنَا لِإِبۡرَٰهِيمَ مَكَانَ ٱلۡبَيۡتِ أَن لَّا تُشۡرِكۡ بِي شَيۡـٔٗا﴾

((kuma lokacinda muka nunawa Ibrahim wurin ɗaki, aka ce mashi: kada ka haɗa ni da wani abu)) [Al-hajj:26],

kuma a cikin kalmomin shiga aikin hajji akwai kore abokin tarayya daga Allah

«**Na amsa kiranKa, baKada abokin tarayya**» kuma mafi alkhairin addu'ar ranar Arafa itace ɗaukaka tauhidi; Annabi -tsira da amicin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Mafi alherin addu'a itace addu'ar ranar Arafa, kuma mafi alkhairin abinda na faɗa ni da Annabawa kafina shine: Babu abin bauta da gaskiya sai Allah, kuma Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya, mulki naSa ne, kuma godiya taSa ce, kuma shi mai iko ne akan dukkan komai**»

(At-tirmizi ta ruwaito shi).

kuma tsantsar tauhidi shine ginshiƙin saƙonnin sama baki ɗaya, kuma shine ginshiƙin tafarkin musulunci, kuma shine haƙiƙanin abinda ya wajaba muyi kishi akai kuma mu kiyaye shi daga dukkan wata gurɓata; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَلَقَدۡ بَعَثۡنَا فِي كُلِّ أُمَّةٖ رَّسُولًا أَنِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱجۡتَنِبُواْ ٱلطَّٰغُوتَۖ﴾

((Haƙiƙa mun aika cikin kowace al'ummah da Manzo, cewa ku bautawa Allah kuma ku nisanci ɗagutu)) [An-nahl:36].

**Ya ku bayin Allah:**

Abin zaɓi: Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya kafa da'awarsa ne akan kalmar ikhlasi kuma itace Annabi Ibrahim -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya sanya kalmar ta kasance mai wanzuwa a cikin zuri'yarsa, kuma masu furuci basu taɓa yin furuci da kalmar da tafi zama abar godewa ba samada kalmar (La'ilaha illallah); aiki da ita shine abin cinikin Aljannah, da za'a aunata da sammai da ƙassai data rinjayesu, Ibn Uwaina -Allah ya jikan sa- yana cewa:

«Allah baiyi wata ni'ima ba akan wani bawa daga cikin bayi wanda take sama da sanar dasu: La'ilaha illallah»

sai dai kuma faɗinta da fatar baki baya amfani sai ga wanda yasan abinda take nunawa na korewa da tabbatarwa, kuma wanda ya tabbatarda sharuɗɗanta na ilimi da yaƙinin ma'anarta da ikhlasi, da gasgatawa ta hanyar aiki da ita, da ƙauna da miƙa wuya da karɓar duk abinda tayi nuni akai, da kuma kafircewa duk abinda ake bautawa koma bayan Allah.

**Yaku musulmai:**

kusani cewa, tauhidi da shirka kishiyoyin juna ne basa taɓa haɗuwa kamar dare da yini; duk lokacinda aka samu shirka, imani yana ƙauracewa.

kuma haƙiƙa Ubangijinka ya girmamaka, ya kiyayeka daga ƙasƙantarda zuciyarka da fuskarka ga waninSa, kuma yana kiranka zuwa ka miƙa wuya gare Shi, to, ka juyarda zuciyarka zuwa gare Shi Shi kaɗai, kada ka saukarda ganinka zuwa ga na ƙasa, kada ka roƙi wanin Ubangijin ƙasa da sama, ai babu haɗi tsakanin mai roƙon wanda yake rayayye ne wanda baya mutuwa da wanda yake rokon matacce, kuma ya dogara ga ƙasusuwa rudud-dugaggu a cikin ƙaburbura?!

**Ya kai Musulmai:**

kashedinka da yin yanka ga wanin Allah; domin shi yanka Ibada ce, ga Allah shi kaɗai, kuma yin yanka ga waninSa shirka ce, Allah shine Ubangijinka wanda ya halliceka, kuma shine wanda ya arzutaka da dabbobin dakake yankawa; don haka, kada ka yankata sai don wanda ya hallicce ka kuma ya halliccesu:

﴿فَصَلِّ لِرَبِّكَ وَٱنْحَرْ﴾

((Kayi sallah ga Ubangijinka kuma kayi soke dabba)) [Al-kauthar:2].

kuma kada kayi rantsuwa saida Allah mai girma da ɗaukaka, Allah shine wanda yabaka baiwar yin magana, don haka, ka gode maSa Shi kaɗai kada

kayi ranstuwa da waninSa; kada kayi rantsuwa da Annabi, ko waliyyi ko da wata ni'ima ko da matsayin wani hallita; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa:

«**Duk wanda yayi rantsuwa da wanin Allah lallai ya kafirta ko yayi shirka**» (At-tirmizi ya ruwaito shi).

kuma su kambu da guru da layoyi dukkansu halittu ne marasa rai; kai kuma halitta ce mai rai, ka girmama kanka kada ka zubarda matsayinka bayan Allah ya ɗaukaka ka kuma ya ɗaga darajarka, kada ka koma kana dogara ga bushashen abu wanda kake ratayashi a ƙirjinka ko kake ɗaurashi a damtsenka kana neman ya kareka daga sharri, ko ya jawo maka alheri, ko ya ture maka kanbun-baka alhali Allah Maɗaukaki yana cewa:

﴿وَإِن يَمۡسَسۡكَ ٱللَّهُ بِضُرّٖ فَلَا كَاشِفَ لَهُۥٓ إِلَّا هُوَۖ وَإِن يُرِدۡكَ بِخَيۡرٖ فَلَا رَآدَّ لِفَضۡلِهِۦۚ﴾

((Idan Allah ya shafeka da wata cuta babu mai yayema sai Shi kaɗai, kuma idan ya nufeka da wani alheri babu wanda zai iya kawarda falalarSa)) [Yunus:107],

kuma Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa:

«**Duk wanda ya rataya laya; to hakika ya yi shirka**»
(Ahmad ya ruwaito shi),

ka dogara gare Shi Shi kaɗai, kuma ka mayarda dukkan lamurranka zuwa gare Shi.

**Yaku Musulmai:**

Haƙiƙa wasu daga cikin mutane sun jahilci hikimar datasa aka hallicesu, sai son zuciya yayita jifa dasu, kuma fitintinu da cututtuka suka mamayesu, wasu daga cikinsu an fitine su da masu sihiri da ƴan rufa-ido da maƙaryata, da sunan sanin ilimin gaibi da sanin abinda zai faru a gaba, amma hakan bai tsinana masu komai ba sai awkawa cikin ɓata da halakarda dukiya a cikin ɓarna, kuma haƙiƙa Allah ya bayyana gaskiya gameda wannan yace:

﴿قُل لَّا يَعۡلَمُ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ ٱلۡغَيۡبَ إِلَّا ٱللَّهُۚ﴾

((Kace masu, babu wanda yasan gaibin dayake cikin sammai da ƙassai sai Allah)) [An-naml:65], kuma Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa:

«**duk wanda yaje gun boka ko ɗan duba kuma ya gasgata abinda yake faɗi, tabbas ya kafircewa abunda aka saukarma Muhammad**»

(Ahmad ya ruwaito shi).

kuma an fitini wasu mutane da abinda suke kira da fitar taurari da buruji, da zane akan ƙasa da halarto da rayuka, da sihirin duba tafin hannaye, saboda sai haka sai suka awka cikin tekun wahami da rashin yarda da ƙaddara. kuma Allah Mai girma da ɗaukaka Yana cewa:

﴿أَمۡ عِندَهُمُ ٱلۡغَيۡبُ فَهُمۡ يَكۡتُبُونَ﴾

((Ko kuma suna da ilimin gaibu ne, wanda suke rubutawa)) [Aɗ-ɗuur:41].

**Ya ku bayin Allah:**

Ikhlasi shine jagoran aiki, kuma duk wanda ya haɗa wani tareda Allah, to lallai Allah shine mafi wadatar masu wadata kuma baya yardarma bayinSa su yi shirka, kaicon masu aikin riya, basu abin Duniyar ba kuma basu yi aiki don neman Lahira ba, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa:

«**Wanda ya nemi ya nuna isa (kankanba) da abinda ba'a bashi ba kamar wanda ya sanya fufafi biyu na ƙarya ne**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

Haƙiƙa burace-buracen masu aikin riya sun tozarta, kuma ayukkansu sun lalace, an kunyatasu a gidan duniya kuma a Lahira bazasu sami wani rabo mai kyau ba, ka kiyayi aikata riya da ji-da-jiyarwa; domin na farkon waɗanda za'a hura wuta dasu a ranar ƙiyama sune masu yin riya a ayukkansu.

Ina neman tsarin Allah daga shaidan jefaffe.

﴿وَمَآ أُمِرُوٓاْ إِلَّا لِيَعۡبُدُواْ ٱللَّهَ مُخۡلِصِينَ لَهُ ٱلدِّينَ حُنَفَآءَ وَيُقِيمُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤۡتُواْ ٱلزَّكَوٰةَۚ وَذَٰلِكَ دِينُ ٱلۡقَيِّمَةِ﴾

((Kuma ba'a Umurce su ba sai da cewa su bautawa Allah suna masu tsarkake Addini a gare shi Suna masu bijirewa dukkan ɓata kuma su tsaida Sallah kuma su bada zakkah kuma wannan shi ne Addini tsayayye)) [Al-bayyinah: 5].

Allah Yasa min albarka daku a cikin Alƙur'ani mai girma.

# HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah, da ni'imarSa ne shiryayyu suka samu shiriya, kuma da adalcinSa ne ɓatattu suka ɓace, ina gode masa irin godiyar bawan daya tsarkake UbangijinSa daga abinda azzalumai sauke faɗe akanSa.

kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah Shi kaɗai baShida abokin tarayya, kuma tsarki ya tabbata ga Allah Ubangijin Al-arshi daga abinda maɓarnata suke siffanta Shi dashi.

kuma ina shaida cewa Annabinmu Muhammad bawanSa ne, ManzonSa ne kuma badaɗayinSa ne, mai gaskiya kuma amintacce, ya Allah kayi yabo da aminci a gare shi da iyalan gidansa da sahabbansa waɗanda sukayi riko da shiriyarsa, kuma akan hanyarsa ne suka kasance suna tafiya.

**Bayan haka, ya ku musulmai:**

Shi imani fa ba wata haja ce mara ƙima ba kuma ba tsurar faɗe bane da baki kuma ba sanya laƙubba bane, amma dai imanin gaskiya shine; aƙida lafiyayya, da aiki ingantacce, jiɓinta da bara'a, a fili da aiki, kyauta da karamci, da kuma kamewa daga cutarwa.

Cikar tauhidi yana buƙatar zuciya wacce take a farke a koda yaushe, wacce take korewa rai duk wani tunani dake gittowa kuma ya kawo tawaya a cikin bautar Allah.

kuma duk wanda ya faɗa a cikin ramin shirka babba; sai ya nemi yayewar talauci ko cuta daga matattu, ko ya nemi samun wani amfani daga garesu kamar neman dukiya ko haihuwa, ko ya nemi taimakon ma'abota ƙabari da waɗanda ke cikin ƙabari, ko yayi ɗawafi ko yanka ko alwashi ga ƙabarin, haƙiƙa ya rusa tauhidin Allah a cikin ayukkanSa, kuma yayi tawaya a cikin bautar Allah, kuma ya munana zato ga Ubangijin hallitu, kuma ya awka cikin mafi girman laifi a wurin Allah, kuma an haramta masa Aljannah kuma za'a dawwamar dashi a cikin wuta. Ubangiji Mai girma da ɗaukaka yana cewa:

﴿إِنَّهُۥ مَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَقَدۡ حَرَّمَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِ ٱلۡجَنَّةَ وَمَأۡوَىٰهُ ٱلنَّارُۖ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنۡ أَنصَارٖ﴾

((Tabbas wanda ke haɗa Allah da wani, Allah ya haramta masa Aljannah kuma makomarsa ita ce wuta kuma azzalumai ba su da wani mataimaki)) [Al-maaidah:72].

Saboda haka, kabi hanya ta gaskiya kuma kabi tafarki na shiriya, dage wajen kiyaye aƙidarka; domin babu wanda yake tseratarwa daga azabar

Allah sai Shi Allah, kuma ba'a samun abinda yake wurin Allah saida kaɗaita Shi da kuma bautarSa da abinda ya shar'antawa bayinSa na neman kusanci zawa gare Shi dashi.

kuma tauhidi ƙofa ce ta sa rai na samun mafita a lokacin ƙuncin rayuwa, kuma bazaka taɓa samun cimma burinka ba sai idan ka kaɗaita wanda Yake Shi kaɗai kuma Tilo da dukkan zantukanka da ayukkanka; domin Shine wanda zai tasheka kuma zai Yi maka hisabi akan ayukkanka:

﴿أَلَآ إِلَى ٱللَّهِ تَصِيرُ ٱلۡأُمُورُ﴾

((ku saurara, zuwaga Allah ne al'amura suke komawa)) [Ash-shuraa:53],

kuma dukkan mutane zasu koma zuwa ga Ubangijinsu

sannan ku sani cewa, lallai Allah ya umurceku da yin salati ga AnnabinSa....

# AMFANIN DAKE A CIKIN TAUHIDI[1]

Dukkan godiya sun tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman agajinSa da gafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrukan kawunanmu da munanan ayukkanmu, wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, kuma wanda ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, tsira da amincin Allah masu tarin yawa su tabbata a gare shi da iyalan gidansa da sahabbansa baki ɗaya.

**Bayan haka:**

Ya ku bayin Allah kuji tsoron Allah haƙiƙanin tsoro, domin tsoron Allah ita ce hanyar shiriya, kuma saɓa mata hanya ce ta rashin arziki.

**Ya ku musulmi:**

Ubangiji Allah ya kaɗaita da kasancewarSa Shi kaɗai Tilo, kuma Ya tsarkake kanSa daga abokin tarayya da tamka da tsara, kuma Ya umurci bayinSa dasu bauta maSa Shi kaɗai, kuma Ya shar'anta masu ibadodi kala-kala, kuma Ya sanya kaɗaita Shi da ibada shine asalin addini kuma ginshiƙinsa kuma farkon rukuninsa, kuma shine matattarar alkhairai, ba'a karɓar wani aiki mai kyau sai tareda shi, ana ruɓunya ƙaramin aiki idan yana tareda tauhidi, kuma ayukkan ƙwarai idan babu tauhidi suna rushewa koda sun kai kwatankwacin girman manyan duwatsu.

shine farkon da'awar Manzanni kuma shine saƙonsu kuma shine abinda saƙon ya tattaro, kuma saboda shi ne aka aiko su; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ مِن رَّسُولٍ إِلَّا نُوحِيٓ إِلَيۡهِ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱعۡبُدُونِ﴾

((Kuma ba Mu aika wani Manzo ba a gabaninka face Muna yi wahayi zuwa gare shi, cawa Lallai ne, babu abin bautawa face Ni, sai ku bauta Mini)) [Al-anbiya`:25].

kuma kowace aya a cikin litaffin Allah tana magana akansa ne ƙarara ko tana nuni zuwa gare shi ko zuwa ga wasu wajibansa, ko ladarsa ko kishiyarsa, kuma umurnin farko a cikin litaffin Allah shine umurni akansa;

(1) Wannan huɗubar anyita ne a masallacin Manzon Allah -tsira da aminci su tabbata a gare shi- a ranar Juma'a, tara ga watan Jumadal akhar, shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da talatin da huɗu bayan Hijra.

Allah Mai girma da ɗaukaka ya ce:

﴿يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱعۡبُدُواْ رَبَّكُمُ﴾

(Ya ku mutane ku bautama Ubangijinku)) [Al-baƙarah:21].

Ma'ana: Ku kaɗaita shi.

kuma a cikin kowace sallah musulmi yana ƙara daukan alƙawari tsakaninsa da UbangijinSa akan tauhidi

﴿إِيَّاكَ نَعۡبُدُ﴾

((Kai kaɗai muke bautaMa)) Ma'ana: bama bautar waninKa.

﴿وَإِيَّاكَ نَسۡتَعِينُ﴾

((kuma Kai kaɗai muke neman taimakonKa)) [Al-fatihah:5].

kuma shine haƙƙin Allah akan bayinSa, kuma shine farkon wajibin da aka ɗora akansu; Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya cema da Mu'az -Allah Ya yarda dashi-:

«**Ya kasance farkon abinda zaka fara kiransu zuwa gare shi shine; kaɗaita Allah da bauta**».

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi),

kuma farkon abinda za'a fara tambayar bawa akansa cikin ƙabarinsa shine: «**Wanene Ubangijinka?**» Ma'ana: wanene abin bautarka.

kuma saboda muhimmancinsa da kasancewarsa babu wata hanyar samun yardar Allah sai dashi, yasa jagoran masu kaɗaita Allah ya roƙama kansa da zuri'yarsa tabbata akan tauhidi, sai yace:

﴿رَبَّنَا وَٱجۡعَلۡنَا مُسۡلِمَيۡنِ لَكَ وَمِن ذُرِّيَّتِنَآ أُمَّةً مُّسۡلِمَةً لَّكَ﴾

((Ya Ubangijinmu ka sanya mu masu miƙa wuya gareka kuma ka sanya daga zur'yarmu al'umma masu miƙa wuya gareka)) [Al-baƙarah:128],

kuma Annabi Yusuf -aminci ya tabbata a gare shi- ya roƙi Ubangijinsa yace:

﴿تَوَفَّنِي مُسۡلِمًا وَأَلۡحِقۡنِي بِٱلصَّـٰلِحِينَ﴾

((Ka ɗauki raina ina musulmi kuma ka riskar dani da mutane managarta)) [Yusuf:101].

kuma yana daga cikin addu'ar Annabinmu -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-:

«**ya Mai jujjuya zukata, Ka tabbatarda zuciyata a kan addininka**»
(Ahmad ya ruwaito shi).
kuma shine wasiyyar Manzanni:

﴿وَوَصَّىٰ بِهَآ إِبْرَٰهِـۧمُ بَنِيهِ وَيَعْقُوبُ يَٰبَنِىَّ إِنَّ ٱللَّهَ ٱصْطَفَىٰ لَكُمُ ٱلدِّينَ
فَلَا تَمُوتُنَّ إِلَّا وَأَنتُم مُّسْلِمُونَ﴾

((Kuma lbrahim ya yi wasiyya da ita ga `ƴa`ƴansa, shima Ya'ƙuba (ya yi wasiyya) cewa:Ya `ƴa`ƴana! Lallai ne, Allah Ya zaɓa maku addini don haka kada kuyarda mutu face kuna Musulmai)) [Al-baƙarah:132].

kuma tafarkin Manzanni shine koyarda shi ga `ƴa`ƴansu, da tambayarsu agamedashi a lokacin magagin mutuwa; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿أَمْ كُنتُمْ شُهَدَآءَ إِذْ حَضَرَ يَعْقُوبَ ٱلْمَوْتُ إِذْ قَالَ لِبَنِيهِ مَا تَعْبُدُونَ مِنۢ بَعْدِى ۖ
قَالُوا۟ نَعْبُدُ إِلَٰهَكَ وَإِلَٰهَ ءَابَآئِكَ إِبْرَٰهِـۧمَ وَإِسْمَٰعِيلَ وَإِسْحَٰقَ إِلَٰهًا وَٰحِدًا وَنَحْنُ لَهُۥ مُسْلِمُونَ﴾

((Ko kun kasance halarce a lokacin da mutuwa tazo wa Ya'ƙuba, a lokacin da yacema `ƴa`ƴansa: Menene ze ku bautama a bayan mutuwata? Suka ce: Zamu bautama Abin bautarka kuma Abin bautar iyayenka lbrahima da lsma'ila da Is'haƙa, Ubangiji Guda, kuma mu a gare Shi masu miƙa wuya ne)) [Al-baƙarah:133].

kuma Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya kasance yana koyama ƙananan sahabbai dogara ga Allah Shi kaɗai koma bayan waninSa; yacema Ɗan Abbas -Allah Ya yarda dasu-:

«**Ya kai ƙaramin yaro, zan Sanar da kai wasu Kalmomi, Ka kiyaye Allah sai Allah ya kiyaye ka, ka kiyaye Allah sai ka same Shi a gabanka, kuma idan zakayi roƙo, to, ka roƙi Allah, kuma idan zaka nemi taimako to ka nemi taimakon Allah**».
(At-tirmizi ya ruwaito shi)
kuma Allah ya umurcemu da kada mu mutu face muna akansa:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ ٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ حَقَّ تُقَاتِهِۦ وَلَا تَمُوتُنَّ إِلَّا وَأَنتُم مُّسْلِمُونَ﴾

((Ya ku waɗanda kuka yi imani Ku ji tsoron Allah haƙiƙanin tsoronSa, kuma kada ku mutu face kuna Musulmai)) [Aali-Imran:102].

da kaɗaita Allah da ibada ne ƙirji yake samun yalwa, kuma zukata suke samu natsuwa, kuma su samu kuɓuta daga bautar halittu:

﴿فَمَن يُرِدِ ٱللَّهُ أَن يَهۡدِيَهُۥ يَشۡرَحۡ صَدۡرَهُۥ لِلۡإِسۡلَٰمِۖ﴾

((duk wanda Allah yaso shiryar dashi, sai ya yalwata ƙirjinsa ga musulunci)) [Al-an`aam:125]

kuma dashi ne ake samun yayewar damuwa da baƙin ciki

﴿فَنَادَىٰ فِي ٱلظُّلُمَٰتِ أَن لَّآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنتَ سُبۡحَٰنَكَ إِنِّي كُنتُ مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ﴾

((Sai ya yi addu'a a cikin duffai yana cewa: Babu wani abin bauta da gaskiya sai Kai, tsarki ya tabbata a gareKa Lallai ni na kasance daga cikin azzulumai)) [Al-anbiya`:87],

Ibnul-Ƙayyim -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«ba'a taɓa tunkuɗe tsananin duniya ba da wani abu da yakai tauhidi»

yana yaye ƙulli kuma yana gyara zuciya; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Zuciyar mumini bata samun wani ƙulli akan ababe guda uku har abada: Tsarkake aiki ga Allah, da yin nasiha ga jagorori, da lizimtar jama'ar musulmai; domin addu'arsu tana zagaye ne dasu da wanda ke tare dasu**»

(Ahmad ya ruwaito shi).

kuma shine sanadin samun rayuwa mai daɗi; hasali babu cin nasara a rayuwa sai dashi; Allah Mai tsarƙi ya ce:

﴿مَنۡ عَمِلَ صَٰلِحٗا مِّن ذَكَرٍ أَوۡ أُنثَىٰ وَهُوَ مُؤۡمِنٞ فَلَنُحۡيِيَنَّهُۥ حَيَوٰةٗ طَيِّبَةٗۖ﴾

((Duk wanda yayi aiki na ƙwarai daga cikin maza ko mata, zamu rayar dashi rayuwa mai kyawu)) [An-nahli:97].

kuma shine abinda rayuwa ta tsayu akai wanda kowace rai take buƙata:

﴿فَمَنِ ٱتَّبَعَ هُدَايَ فَلَا يَضِلُّ وَلَا يَشۡقَىٰ﴾

((wanda yabi shiriyata ba zai ɓace ba kuma ba zai taɓe ba)) [Ɗaha:123]

kuma shine yake haɗa kan musulmai -larabawansu da waɗanda ba larabawa ba, gabashinsu ya yammacinsu-

﴿إِنَّ هَٰذِهِۦٓ أُمَّتُكُمۡ أُمَّةٗ وَٰحِدَةٗ وَأَنَا۠ رَبُّكُمۡ فَٱعۡبُدُونِ﴾

((Lallai wannan itace al'ummarku addininta guda ɗaya, kuma Ni ne

Ubangijinku don haka ku bauta maNi Ni kadai)) [Al-anbiya`:92].

Kalmar tauhidi kalma ce mai kyau maɗaukakiya, tushenta yana tabbace a ƙasa kuma reshenta yana sama, ita ce kalmar Allah maɗaukakiya, kuma da itace Allah yayi magana da Musa kai tsaye ba tare da wani a tsakaninsu ba:

﴿إِنَّنِيٓ أَنَا ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱعۡبُدۡنِي﴾

((Kuma tabbas Nine Allah ba wani abin bauta da gaskiya sai Ni, don haka ka bautata Mani)) [Ɗaha:14].

kuma babu wani yanki na imani wanda yafita ɗaukaka; Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- yana cewa:

«**Imani yanki saba'in da ɗoriya ne** - ko: **sittin da ɗoriya ne-; mafi falalarsa shine faɗin La'ila ha illallah**»

(Muslim ya ruwaito shi)

itace mafi tsarkin zance kuma mafi nauyi a cikin ma'auni, tana matsayin `ƴanta wuya, kuma kariya ce daga shaidan a kullum; Annabi - tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Duk wanda yace: La'ilaha illallah, wahdahu la sharikalah, lahul mulku, walahul hamdu, wahuwa ala kulli shai'in ƙadeer, sau ɗari a rana; kamar ya `ƴanta wuyayi goma ne, kuma za'a rubuta masa aiki na ƙwarai guda ɗari, kuma a kankare masa munanan ayukka guda ɗari, kuma zata zame masa kariya daga shaiɗan a wannan ranar har zuwa yammaci, kuma babu wanda zaizo da abinda yafi falala sama da shi sai dai wanda yayi fiye da haka**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

«La'ilaha illallah» bakuna basu taɓa yin ƙamshi kuma laɓɓa basu taɓa motsawa ba da abinda yafita kyawu; Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«Mafi alherin abinda na faɗa ni da Annabawa kafina shine: La'ilaha illallah, wahdahu la sharikalah, lahul mulku, walahul hamdu, wahuwa ala kulli shai'in ƙadeer,»

(At-tirmizi ya ruwaito shi)

kalma ce dawwamammiya, Allah yayi alƙawarin samuwar wanda zai riƙa faɗinta da daga cikin mutane kuma da kira zuwa gareta; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَجَعَلَهَا كَلِمَةَۢ بَاقِيَةٗ فِي عَقِبِهِۦ﴾

((Kuma ya sanyata kalma dawwamammiya a bayansa cikin zuriyarsa)) [Az-zukhruf:28].

itace zance tabbatacce, wanda yayi riƙo da ita, Allah zai tabbatar dashi a duniya da lahira; Ubangiji Mai girma da ɗaukaka ya ce:

﴿يُثَبِّتُ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱلۡقَوۡلِ ٱلثَّابِتِ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَفِي ٱلۡأٓخِرَةِۖ﴾

((Allah yana tabbatar da waɗanda sukayi Imani da magana matabbaciya a rayuwar duniya da kuma a lahira)) [Ibrahim:27],

kuma mafi cikan bayi shine wanda yafi cikar bautuwa ga Allah, kuma gwar-gwadon yadda bawa ya tsayarda tauhidi yake samun cika da ɗaukakar matsayi, kuma Allah yana yin kariya ga ma'abota tauhidi a cikin addini da rayuwar duniya, kuma mafi kusanci ga samun gafarar Allah shine mai kaɗaita Shi, yazo a cikin hadisi ƙudusi Allah ya ce:

«**Da zaka zo min da cikin ƙasa na zunubbai amma kuma ka haɗu daNi baka haɗa Ni da komai ba, tabbas, zan zo maka da cikin ƙasar na gafara**» (At-tirmizi ya ruwaito shi),

Ɗan Rajab -Allah -ya masa rahama- ya ce:

«tauhidi shine sababi mafi girma; duk wanda ya rasa shi tabbas ya rasa samun gafara, kuma duk wanda yazo dashi haƙiƙa yazo da mafi girman sababin samun gafara».

kuma shaiɗan bashida iko akan masu tauhidi:

﴿إِنَّهُۥ لَيۡسَ لَهُۥ سُلۡطَٰنٌ عَلَى ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَلَىٰ رَبِّهِمۡ يَتَوَكَّلُونَ﴾

((Lallai ne shi, ba shi da wani iko a kan waɗanda suka yi imani, kuma suna dogara ga Ubangijinsu)) [An-nahl:99],

kuma gwargwadon tauhidin bawa, kariyar Allah take ƙaruwa a gare shi; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ يُدَٰفِعُ عَنِ ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْۗ﴾

((Lallai Allah yana kariya ga waɗanda sukayi imani)) [Al-hajj:38],

kuma duk wanda ya tsayarda tauhidin Allah, Allah zai kare shi daga laifuka masu halakarwa da miyagun ayukka, Allah ya faɗa gameda Annabi Yusuf -tsira da aminci su tabbata a gare shi:

﴿كَذَٰلِكَ لِنَصۡرِفَ عَنۡهُ ٱلسُّوٓءَ وَٱلۡفَحۡشَآءَۚ إِنَّهُۥ مِنۡ عِبَادِنَا ٱلۡمُخۡلَصِينَ﴾

((kamar hakane, dan mu kawar masa da ayukka munana da kuma alfasha, lallai shi yana daga cikin bayin mu tsarkakakku)) [Yusuf:24].

Ibnul-Ƙayyim -Allah Ya yi masa Rahama- ya ce:

«duk lokacin zuciya ta kasance mai raunin tauhidi kuma da girman shirka da Allah, zata kasance mai yawan aikata mafiya munin ayukka».

kuma mai tauhidi yanada natsuwa a rayuwar duniya, kuma yanada aminci a cikinta gwargwadon imaninsa

﴿ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَلَمۡ يَلۡبِسُوٓاْ إِيمَٰنَهُم بِظُلۡمٍ أُوْلَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلۡأَمۡنُ وَهُم مُّهۡتَدُونَ﴾

((Waɗanda suka yi imani, kuma ba su gauraya imaninsu da zalunci ba, waɗannan sukeda aminci, kuma sune shiryayyu)) [Al-an`aam:82].

kuma mamata suna amfanuwa da addu'ar masu tauhidi, kuma ba'a karɓar addu'ar kowa a sallar gawa sai tasu; Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Babu wani mutum musulmi wanda zai mutu, kuma asamu mutum arba'in da basa haɗa Allah da wani su tsaya akan gawarsa face sai Allah yabasu cetonsa**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma idan mutuwar mai tauhidi ta kusanto, Allah yana masa bishara da gidan Aljannah; tsira da aminci su tabbata a gare shi ya ce:

«**Duk wanda ƙarshen maganarsa itace: La'ila ha illallah; zai shiga Aljannah**» (Abu Dawuda ya ruwaito shi).

kuma kamar yadda Allah ya ɗaukaka mai tauhidi a nan duniya, haka nan kuma ya karrama shi a lahira kuma ya ɗaukaka matsayinsa, kuma ya saka masa da mafi kyawun sakamakon masu aiki,; duk wanda ya mutu akan tauhidi za'a bashi Aljannah a farkon al'amari ko a ƙarshe, kuma koda ya shiga wuta saboda wasu zunubbansa ba zai dawwama a cikinta ba; tsira da aminci su tabbata a gare shi ya ce:

«**Duk wanda ya mutu alhali baya haɗa Allah da wani abu, zai shiga Aljannah**» (Bukhari da Muslim suka ruwaito shi)

kuma babu masu samun ceton Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- sai masu tauhidi;

Abu Huraira -Allah Ya yarda dashi- ya ce: «Ya Manzon Allah! waye yafi can-cantar rabauta da cetonka a ranar ƙiyama? Sai yace: **Wanda yafi dacewa da samun cetona a ranar ƙiyama shine wanda yace: La'ila ha illallah; yana mai faɗen ta da gaskiya cikin zuciyarsa**»

(Bukhari ya ruwaito shi).

kuma wanda ya tsayarda tauhidi matuƙar tsayarwa zai shiga Aljannah ta kowace ƙofa yake so daga cikin ƙofofinta guda takwas; Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Babu wani ɗaya daga cikinku da zaiyi Alwala kuma ya cika alwalar, sannan yace: Ash'hadu alla ilaha illallah, wahdahu la sharika lahu, wa'anna Muhammad abduhu warasulu; face sai an buɗe masa ƙofofin Aljannah guda takwas, ya shiga ta kowacce yaga dama daga cikinsu**»

(Muslim ya ruwaito shi),

Dan Ƙayyim -Allah ya yi masa rahama- ya ce:

«duk yayinda tauhidin bawa ya kasance mai girma, a lokacin gafarar Allah a gare shi take ƙara cika; don haka, duk wanda ya haɗu daShi alhali baya haɗaShi da waninSa ko kaɗan, zai gafarta masa zunubbansa baki ɗaya».

Kuma akwai mutum dubu saba'in dazasu shiga Aljannah batareda hisabi ba, kuma dukkansu daga ma'abota tauhidi ne, Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi ya ce:

«**Sune waɗanda basa neman ayi masu ruƙuya** (tofi), **kuma basa camfi, kuma basa lalas da wuta, kuma suna dogara ne kaɗai ga Ubangijinsu**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

**Bayan haka, ya ku Musulmai:**

Tauhidi shine mafi tsadar abinda musulmi ya mallaka, kuma duk wanda Allah ya shiryar zuwa gare Shi lallai yayi riƙo da shi da turamen haƙora (da ƙarfin gaske) kuma ya kareshi daga duk abinda yake warwareshi ko yake zama wata suka a cikinsa ko yake zama tawaya ne a gare shi, kuma duk wanda ya roƙi wannin Allah ko yayi ɗawafi ga ƙabari ko yayi yanka ga ƙabari, haƙiƙa yayi hasarar hasken tauhidi da falalarsa, kuma ba'a taɓa karɓar wani aikin biyayya daga gare shi, kuma ya miƙa kansa ga dalilan nassoshi na alƙawarin dawamma a cikin wuta

Ina neman tsarin Allah daga shaidan jefaffe.

﴿قُلْ إِنَّمَآ أَنَا۠ بَشَرٌ مِّثْلُكُمْ يُوحَىٰٓ إِلَىَّ أَنَّمَآ إِلَٰهُكُمْ إِلَٰهٌ وَٰحِدٌ ۖ فَمَن كَانَ يَرْجُوا۟ لِقَآءَ رَبِّهِۦ فَلْيَعْمَلْ عَمَلًا صَٰلِحًا
وَلَا يُشْرِكْ بِعِبَادَةِ رَبِّهِۦٓ أَحَدًۢا﴾

((Ka ce: Ni, mutum ne kamarku, ana yin wahayi zuwa gare ni cewa: Lallai ne, Abin bautawarku, Abin bautawa ne Guda ɗaya, saboda haka wanda ya kasance yana fatan haɗuwa da Ubangijinsa, to, sai yayi aiki na ƙwarai. Kuma kada ya haɗa kowa cikin bautama Ubangijinsa)) [Al-kahf:110].

Allah Yasa min albarka tareda ku a cikin Alƙur'ani mai girma...

# HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gare Shi akan samun dacewa da kuma ni'imominSa, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya ina mai girmama al'amarinSa, kuma ina shaida cewa Muhammad bawanSa ne kuma manzonSa ne, Allah yayi daɗin tsira da aminci a gare shi da iyalansa da sahabbansa.

**Yaku Musulmai:**

Tauhidi baiwa ce mai girma daga Allah, yana bada kyautarsa ga wanda yaso daga cikin bayinSa, kuma wajibin musulmi ne yayita ƙoƙarin tsayarda shi da tabbatar dashi akansa da zuriyarsa da makusantansa na danginsa da ɗaukacin mutane.

kuma yana daga cikin godiya ga ni'imar tauhidi: kiran halittu zuwa gare shi, da tsorotarwa daga kowanne abu mara kyau wanda zai iya kore tushensa ko ya hana cikansa.

Kuma yana daga cikin hanyoyin tabbata akansa: Roƙon Allah tabbatuwa akansa, da nisantar bidi'o'i da ababe masu ruɗarwa da sha'awoyi, da kuma yawan yin aikin ɗa'a, da guzurin ilimin addni, da tambayar malamai na Allah akan duk abinda yayi wahalar ganewa daga cikinsa.

sannan ku sani cewa, lallai Allah ya umurceku da yin salati da sallam ga AnnabinSa....

# FALALAR KALMAR TAUHIDI[1]

Dukkan godiya sun tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa da gafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrukan kawunanmu da munanan ayukkanmu, wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, kuma wanda ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida cewa babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma manzonSa ne, tsira da amincin Allah masu tarin yawa su tabbata a gare shi da iyalan gidansa da sahabbansa baki ɗaya.

**Bayan haka:**

Ya ku bayin Allah, kuji tsoron Allah haƙiƙanin tsoro, kuma kuyi riƙo da igiya mai ƙarfi acikin musulunci.

**Ya ku Musulmi:**

Darajar halitta tana cikin fuskantar Allah da biyayya ga Allah da lizimtar bautarSa, kuma wannan sababin yin halitta da bayarda umurni, kuma da ita ne ake rabauta da samum nasara a duniya da lahira:

﴿وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ فَقَدۡ فَازَ فَوۡزًا عَظِيمًا ﴾

((kuma duk wanda yabi Allah da ManzonSa, haƙiƙa ya samu rabo mai girma)) [Al-ahzaab:71].

kuma samun farin ciki, murna, jin daɗi, da daɗaɗan lokaci da ni'imomi dukkan su suna cikin sanin Allah da kaɗaita Shi da imani daShi.

kuma mafi falalar zance kuma mafi soyuwa ga Allah shine yin yabo a gare Shi da kirari, kuma mafi alkhairin yabo ga Allah itace kalmar tauhidi (La'ilaha illallah), kalma ce wacce akanta ƙassai da sammai suka tsayu, kuma saboda ita ne aka halicci komai, kuma da ita ne Allah ya saukar da littafanSa kuma ya aiko da ManzanninSa; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَمَآ أَرۡسَلۡنَا مِن قَبۡلِكَ مِن رَّسُولٍ إِلَّا نُوحِيٓ إِلَيۡهِ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱعۡبُدُونِ ﴾

(1) Wannan huɗubar anyita ne a masallacin Manzon Allah -tsira da aminci su tabbata a gare shi- a ranar Juma'a bakwai ga watan Jumada Al-ula, shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da talatin da takwas bayan Hijra.

((kuma baMu aika wani Manzo gabaninka ba face mun yi masa wahayi cewa babu wani abin bauta da gaskiya face Ni; don haka ku bauta mani)) [Al-anbiya`:25].

kuma da itace Manzanni sukayima mutanensu gargaɗi; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿أَنْ أَنذِرُوٓاْ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنَا۠ فَٱتَّقُونِ﴾

((domin kuyi gargaɗi cewa lallai babbu abin bauta da gaskiya sai Ni kuma kuji tsoroNa)) [An-nahl:2].

Allah ya shaidawa kanSa ita, kuma ya sanya mafiya falalar halittunSa shedu akanta; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿شَهِدَ ٱللَّهُ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ وَٱلْمَلَٰٓئِكَةُ وَأُوْلُواْ ٱلْعِلْمِ قَآئِمًۢا بِٱلْقِسْطِۚ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ﴾

((Allah Ya shaida cewa: Lallai ne babu abin bautawa da gaskiya face Shi kuma mala'iku da ma'abota ilmi sun shaida hakan, yana tsaye da adalci, babu abin bauta da gaskiya sai Shi, Mabuwayi, Mai hikima)) [Aali-Imran:18].

Ibnul-Ƙayyim -Allah Ya yi masa rahama- ya ce:

«Wannan itace mafi ɗaukakar shaida, mafi girma, mafi adalci kuma mafi gaskiyarta, daga mafi girman masu shaida akan mafi girman abin shaida».

Dukkan shari'o'i an ginasu akan wannan kalmar, kuma addini dukkansa haƙƙinta ne, kuma akanta dukkan lada a game da itane, kuma dukkan wata uƙuba tana kasancewa ne akan barinta ko tawaya a cikin ta, kalma ce mai maɗaukakan matsayi, mai yawan falala, itace ƙololuwar musulunci baki daya, kuma itace ta farkon rukunnansa kuma mafi girman ginshiƙansa, akanta ne sauran rukunnai suka tsayu, kuma itace rukunin imani kuma sashinsa mafi girma, imani baya inganta sai da ita, kuma baya tsayuwa sai akanta.

akanta ne aka gina musulunci kuma aka kafa Alƙibla, kuma ita ce tsantsar haƙƙin Allah ce akan dukkan bayi, itace kalmar musulunci, kuma mabuɗin gidan Aljannah, kuma da ita ne mutane suka rarrabu zuwa ƴan wuta da Aljannah, da kuma karɓaɓaɓɓu da korarru, itace mai rarrabewa tsaknin musulunci ka kafirci, masu magana basu taɓa furta abunda yafita kyau ba, kuma masu aiki basuyi aiki da sama da abunda yafi kyawon

abunda ta ƙunsa ba, Annabi tsira da aminci su tabbata a gare shi ya ce:

«**Mafi soyuwar zance a wurin Allah guda hudu ne: Faɗin Subhanallah, da Alhamdulillah, da La'ilaha illallah da Allahu Akbar**»

(Muslim ya ruwaito shi)

kuma itace kalmar taƙawa wacce Allah ya keɓance masoyanSa da ita; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَأَلْزَمَهُمْ كَلِمَةَ ٱلتَّقْوَىٰ﴾

((kuma ya lizimta masu kalmar taƙawa)) [Al-fat`h:26],

kuma itace igiya mai ƙarfi wadda duk wanda yayi riƙo da ita ya samu tsira; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿فَمَن يَكْفُرْ بِٱلطَّٰغُوتِ وَيُؤْمِنۢ بِٱللَّهِ فَقَدِ ٱسْتَمْسَكَ بِٱلْعُرْوَةِ ٱلْوُثْقَىٰ لَا ٱنفِصَامَ لَهَا﴾

((kuma duk wanda ya kafurcema ɗagutu kuma ya yi imani da Allah to tabbas ya yi riƙo da igiya ƙwaƙwƙwara wacce ba ta tsinkewa)) [Al-baƙarah:256].

ɗaukaka itace siffarta kuma tana tareda wanzuwa; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَكَلِمَةُ ٱللَّهِ هِىَ ٱلْعُلْيَا﴾

((kuma kalmar Allah itace maɗaukakiya)) [At-taubah:40].

kalma ce mai kyau, Allah ya buga misalinta a cikin litattafinSa; yace:

﴿أَلَمْ تَرَ كَيْفَ ضَرَبَ ٱللَّهُ مَثَلًا كَلِمَةً طَيِّبَةً كَشَجَرَةٍ طَيِّبَةٍ أَصْلُهَا ثَابِتٌ وَفَرْعُهَا فِى ٱلسَّمَآءِ﴾

((Shin, ba ka gani ba, yadda Allah Ya buga wani misalin kalma mai kyau kamar itaciya ce mai kyau, asalinta yana tabbatacce aƙasa, kuma reshenta yana cikin sama?)) [Ibrahim:24],

da ita ake samun yalwar ƙirji

﴿فَمَن يُرِدِ ٱللَّهُ أَن يَهْدِيَهُۥ يَشْرَحْ صَدْرَهُۥ لِلْإِسْلَٰمِ﴾

((duk wanda Allah ya yi nufin ya shiryar dashi, sai ya yalwata ƙirjinsa da musulunci)) [Al-an`aam:125],

Ibn Juraij -Allah Ya jiƙansa- ya ce-:

ma'ana sai ya yalwata ƙirjinsa da (La'ilaha illallah»,

kuma da ita ne zuciya take samun aminci

﴿يَوۡمَ لَا يَنفَعُ مَالٞ وَلَا بَنُونَ * إِلَّا مَنۡ أَتَى ٱللَّهَ بِقَلۡبٖ سَلِيمٖ﴾

((A ranar da dukiya da `ya`ya ba sa amfani. sai wanda ya isa wurin Allah da zuciya mai tsarki)) [Ash-shuara`:88-89],

kuma Ibnu-Abbas -Allah Ya yarda da su- ya ce:

«Tsarkakakkiyar zuciya itace: Ya shaida babu abin bauta da gaskiya sai Allah».

kuma itace da'awa ta gaskiya wacce babu ɓarna a ciki, kuma itace zance madai-daici wanda babu kar-kata a cikinsa, kuma itace shaida ta gaskiya wacce ba ƙarya a cikinta, kuma itace siffa maɗaukakiya wacce Allah ya kaɗaita da ita koma bayan halittunSa, kuma itace kalmar data wanzu a zuriyar Annabi Ibrahim -tsira da aminci su tabbata a gare shi-; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَجَعَلَهَا كَلِمَةَۢ بَاقِيَةٗ فِي عَقِبِهِۦ لَعَلَّهُمۡ يَرۡجِعُونَ﴾

((Kuma (Ibrahim) ya sanya (ita wannan) kalmar mai wanzuwa a cikin zuriyarsa, domin su dawo daga ɓata)) [Az-zukhruf:28]

Dan Katheer -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«itace La'ilaha illallah; ya sakata dawwamamiyya a cikin zuriyarsa duk wanda Allah ya shiryar daga cikin zuriyar Ibrahim yana koyi dashi a cikinta»

«La'ilaha illallah» itace mafi girman ni'ima ga bayi; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَأَسۡبَغَ عَلَيۡكُمۡ نِعَمَهُۥ ظَٰهِرَةٗ وَبَاطِنَةٗۗ﴾

((kuma ya cika ni'imominSa na bayyane dana ɓoye akanku)) [Luƙman:20],

Sufyanu ɗan Uwaina -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«Allah bai yi wata ni'ima ba akan bayi wadda take sama da sanar dasu: La'ilaha illallah»

kalma ce wacce take tafi duniya da abinda yake cikinta; Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**ace infadi: Subhanallah, walhamdu lillah, wa La'ila illallah wallahu akbar yafi soyuwa a gareni fiye da duk abinda rana ta fito akansa**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma itace farkon wajibin da ya wajaba akan bayi su sani kuma suyi aiki

ita; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿فَٱعۡلَمۡ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ﴾

((To ka sani, cewa babu abin bautawa da gaskiya face Allah)) [Muhammad:19],

Shehun Musulunci -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«Magabata da Jagororin addini sun haɗu akan cewa farkon abinda ake umurtar bayi dashi; su ne kalmomin shahada guda biyu»,

kuma shine wajibi na ƙarshe; Manzon Allah -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Duk wanda ƙarshen maganarsa ya kasance: La'ila ha illallah; ya shiga Aljannah**»

(Abu Dawuda ya ruwaito shi).

wanda ya santa kuma yake aiki da ita shine wanda yake tsayayye akan hanya madai-daiciya da gaske, Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ قَالُواْ رَبُّنَا ٱللَّهُ ثُمَّ ٱسۡتَقَٰمُواْ﴾

((Lallai waɗanda suka ce Ubangijinmu shi ne Allah sannan suka tsaya akan hakan))

Ɗan Abbas -Allah Ya yarda da su- ya ce:

(Ma'ana: akan shahadar La'ilaha illallah)

﴿فَلَا خَوۡفٌ عَلَيۡهِمۡ وَلَا هُمۡ يَحۡزَنُونَ﴾

((Basuda tsoro kuma basuda baƙin ciki)) [Al-ahƙaaf:13],.

idan aka faɗi wannan kalma da gaskiya; zuciya zata tsarkaka daga wanin Allah, kuma wanda yake akanta da gaskiya ba zai so wanin Allah ba, ba zai yi fata ga wanin Shi ba, ba zai tsoraci waninSa ba, baya dogaro sai a gare Shi kuma ba wani tasiri na son kai ko bin son zuciya da zai yi saura tareda shi.

itace mai bada kariya ga dukiya da jini; Manzon Allah - tsira da aminci su tabbata a gare shi - ya ce:

«**Duk wanda ya fadi "La'ilaha illallah", kuma ya kafircema abin da ake bautama komabayan Allah, dukiyarsa da jininsa sun sami alfarma, kuma sakamakonsa yana ga Allah mai girma da ɗaukaka**».

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma itace farkon abinda ake fara da`awah, kuma da ita ce farkon abinda

Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya fara kirza zuwa gare shi, kuma akanta yake karɓar mubaya'ar sahabbansa, kuma da itace Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya aika masu kira zuwa garuruwa, a lokacin da ya aika Mu'az -Allah Ya yarda dashi- zuwa Yaman sai yace masa:

«**Lallai kai zaka je wurin wasu mutane ma'abota littafi, ka kirasu zuwa shaidawa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, kuma ni Manzon Allah ne**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

kalmar tauhidi itace kalma mai dai-daitawa, akanta ne halittu suke haɗuwa, kuma da rashinta ne ake samuwan rarrabuwa da saɓani, Allah mai tsalki yace:

﴿قُلۡ يَٰٓأَهۡلَ ٱلۡكِتَٰبِ تَعَالَوۡاْ إِلَىٰ كَلِمَةٖ سَوَآءِۭ بَيۡنَنَا وَبَيۡنَكُمۡ أَلَّا نَعۡبُدَ إِلَّا ٱللَّهَ﴾

((kace masu: yaku ma'abota littafi, kuzo ga wata kalma wadda take dai-dai tsakanin mu daku, kada mu bautawa kowa sai Allah, kuma kada mu haɗa Shi da komai)) [Aali-Imran:64],

duk wanda ya faɗeta da gaskiya zai samu rabauta; Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Yaku mutane! kuce: La'ila illa Allah; zaku rabauta**»

(Ahmad ya ruwaito shi).

Wanda yayi riƙo da ita yana riƙe da mafi ɗaukakar yanki na imani; Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Imani yanki saba'in da ɗoriya ne, kuma mafi falalarsa shine faɗin: La'ila ha illallah**»

(Muslim ya ruwaito shi),

kuma ayarda take ƙunshe da ita, itace mafi girman ayoyi a cikin Alƙur'ani, kuma mafi girman addu'ar neman gafara yana ƙunshe da ita,

itace mafi girman ayukka ta fuskar ruɓunyuwa da kuma lada;

domin «**duk wanda a cikin rana yace: La'ilaha illallah, wahdahu la sharikalahu, lahul mulku walahul hamdu, wa huwa ala kulli shai'in ƙadeer, yanada kwatan-kwacin ƴanta wuyayi goma, kuma za'a rubuta masa ayukka na ƙwarai guda ɗari, kuma a shafe masa laifuka ɗari, kuma zai kasance a wannan yini cikin tsari daga shaiɗan har zuwa yamma, kuma babu wanda zai zo da abinda yafi nasa sai wanda yayi abinda yafi wannan yawa**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi)

kuma «**Duk wanda ya ce La'ilaha illallah, wahdahu la sharikalahu, lahul mulku walahul hamdu, wa huwa ala kulli shai'in ƙadeer sau goma zai kasance Kamar wanda ya ƴanta rayuka huɗu daga `ƴa`ƴan Annabi Isma'il**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma itace mafi girman sadaka wacce bata kuɗi ba; Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**kuma kowa ce Hailala wato faɗen La'ila ha illallah sadaka ce**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma itace matsera ga bawa a cikin ƙabarinsa, kuma akanta ake tabbatar dashi a lokacin tambaya; Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Idan aka tambayi Musulmi a cikin ƙabari akan: Shin ya shaida cewa babu wani abin bauta da gaskiya sai Allah, kuma Muhammadu Manzon Allah ne? To wannan shine ma'anar faɗin Allah Madaukak:**

﴿يُثَبِّتُ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱلْقَوْلِ ٱلثَّابِتِ فِي ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَا وَفِي ٱلْأَخِرَةِۖ﴾

((**Allah Yana tabbatar da waɗanda suka yi imani da magana tabbatacciya a rayuwar duniya da lahira**))» [Ibrahim:27].

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

cikin falalar Allah littattaffan rubuta zunubbai suna zama marasa nauyi saboda nauyin wannan kalmar; Manzon Allah -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Za'a zo da wani mutum, sai a buɗe masa takardun laifi guda casa'in da tara, kowane littafi daga cikinsu girmansa iya gani, sai a fito masa da wani masa wani kati wanda a cikinsa akwai: Ina shaida ba abin bautawa da gaskiya sai Allah kuma Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, sai a ɗora manyan littattafan a cikin hannu ɗaya na ma'auni, sai su zama marasa nauyi kuma wannan katin yafi su nauhi**»

(Ahmad ya ruwaito shi),

«**da za'a zuba sammai bakwai da ƙassai bakwai a ɓangare ɗaya na ma'auni kuma a ɗora La'ilaha illallah a ɗayan ɓangaren, tabbas, La'ila ha illallah zata rinjayesu, da ace sammai da ƙassai guda bakwai zasu kasance tamkar zobe kullalle; face sai kalmar La'ilaha illallah ta tsinka su**».

(Ahmad ya ruwaito shi).

ma'abotanta sune masu yin ceto, kuma sunada alƙawari a wurin Allah mai rahama; Allah -mai tsalki- ya ce:

﴿لَّا يَمۡلِكُونَ ٱلشَّفَٰعَةَ إِلَّا مَنِ ٱتَّخَذَ عِندَ ٱلرَّحۡمَٰنِ عَهۡدٗا﴾

((Ba su mallakar ceto sai wanda ya riƙi alƙawari a wurin Mai rahmah)) [Maryam:87].

kuma waɗanda suka fi can-cantar samun rabo na ceton Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-: Sune masu tsarkakewa kuma masu gaskiya a cikin faɗinta, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Wanda suka fi can-cantar samun cetona gobe ƙiyama shine wanda ya faɗi: La'ila ha illallah; yana mai tsantsar tsarkakewa har zuciyarsa**»

(Bukhari ya ruwaito shi)

kuma Aljannah itace sakamakon wanda ya faɗeta da gaskiya, yana mai tsarkake hakan har zuciyarsa, yana mai yaƙini da ita ba shakka, kuma yana mai aiki da ita, kuma ya nisanci duk abinda yake war-wareta; Manzon Allah -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Ba wani bawa da zai ce: La'ilaha illallah, sannan kuma ya mutu akan hakan; face sai ya shiga Aljannah**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi),

kuma ana buɗe wa wanda ya faɗeta dukkan ƙofofin Aljannah guda takwas, ya shiga ta kowace ƙofa yake so; kuma wanda ya kasance mai gaskiya a cikinta kuma mai aiki da abinda take wajabtawa wuta bazata shafesa ba; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Babu wani da zai shaida babu abin bautawa da gaskiya sai Allah kuma tabbas Muhammad Manzon Allah ne yana mai faɗin haka da gaskiya har zuciyarsa face sai Allah ya haramta masa wuta**»

«Bukhari da Muslim suka ruwaito shi»,

kuma Allah yana fitarwa daga wuta duk wanda ya faɗeta kuma yanada kwatan-kwacin ƙwayar zarra na imani; Allah Mai girma da ɗaukaka ya ce:

«**Na rantse da buwayata ɗaukakata, da jin isana da girmana, zan fitar daga cikinta -wuta- duk wanda ya ce: La'ilaha illallah**»

(Bukhari ya ruwaito shi).

Kuma saboda muhimmancin kalmar tauhidi a kowane lokaci a rayuwar bawa; shari'a tazo da kwaɗaitarwa akan lizimtarta cikin kowane hali da sha'ani;

don haka, «**duk wanda ya wayi gari yace: La'ilaha illallah, wahdahu la sharikallhu, lahul mulku, walahul hamdu, wa huwa ala kulli shai'in ƙadeer; za'a bashi -lada- kamar wanda ya `ƴanta bawa daga cikin**

**`ƴa`ƴan Ismael, kuma a rubuta masa ayukka na ƙwarai guda goma, kuma a shafe masa zunubbai guda goma, kuma a ɗaukaka masa daraja goma, kuma zai kasance a cikin tsaro daga shaiɗan har zuwa yamma, kuma idan ya faɗeta da yamma za'a bashi irin hakan har zuwa safiya**».

(Abu Dawuda ya ruwaito shi),

kuma idan mutum ya gama alwala sai ya faɗeta, za'a buɗe masa ƙofofin Aljannah guda takwas; Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Babu wani daya daga cikinku da zaiyi alwala kuma ya cika alwalarsa sannan yace: Ashhadu alla ilaha illallah, wa anna Muhammadan abduhu warasuluhu; face sai an bude masa ƙofofin Aljannah guda takwas**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma da ita ce ake fara bude kiran sallah kuma da ita ake rufe shi, tsira da aminci su tabbata a gare shi ya ce:

«**Idan mai kiran sallah yace: Allahu akbar Allahu akbar, sai ɗayanku yace: Allahu akbar Allahu akbar, sannan yace: Ashhadu alla ilaha illallah, kuma shima yace: Ash'hadu alla ilaha illallah, sannan yace: Ashhadu anna Muhammadan rasulullah, kuma shima yace: Ashhadu anna Muhammadan rasulullah, sannan yace: Hayya alassallah, sai shi kuma yace: La haula wala ƙuwwata illa billah, sannan kuma yace: Hayya alal falah, sai shi kuma yace: La haula wala ƙuwwata illa billah, sannan yace: Allahu akbar Allahu akbar, kuma shima yace: Allahu akbar Allahu akbar, sannan yace: La'ilaha illallah, kuma shima yace: La'ilaha illa Allah. -ya faɗi hakan- har zuciyarsa zai shiga Aljannah**»

(Muslim ya ruwaito shi),

kuma «**Duk wanda bayan ya ji kiran Salla yace: Ash'hadu alla ilaha illallah, wahdahu la sharikallahu wa anna muhammadan abduhu warasuluh, radhitu billahi rabban, wabi Muhammadin rasulullah, wabil Islami dinan; za'a gafarta masa zunubansa**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma idan musulmi ya miƙe zuwa salla yana buɗeta ne da tauhidi, kuma ita salla bata inganta saida karatun tahiya (tashahhud), kuma kafin mai salla ya fita daga cikinta zai yi addu'a yana mai neman tawasulli da ita - wato kalmar tauhidi-

«**Allah kayi min gafarar abinda na gabatar da wanda na jinkirta, da abinda na ɓoye da wanda na bayyana, da ɓarnar da nayi, da kuma abinda Kai ne mafi sani game da shi sama da ni, Kai ne mai gabatarwa**

**kuma Kaine mai jinkirtarwa, Babu wani abun bauta da gaskiya sai Kai**»

(Muslim ya ruwaito shi),

kuma bayan kowace sallah yana cewa:

«**La'ila ha illallah, wahdahu la sharikallahu, lahul mulku walahul hamdu wahuwa ala kulli shai'in ƙadeer**»

«Bukhari da Muslim suka ruwaito shi».

kuma da ita yake rufe tasbihi, da tahmidi, da takbiri sai «**a yafe masa zunubbansa koda sun kai yawan kumfan teku**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma bawa yana lizimtarta a lokacin ayukkan Hajji;

«Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- **ya kasance idan ya hau kan dutsen Safa da Marwa, yana ya fuskantar Alƙibla; sai ya kaɗaita Allah kuma ya girmama shi**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma a Muzdalifa:

«Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- **yazo a muzdalifa, sannan ya hau kan dutse, ya godema Allah ya kaɗaita Shi kuma ya girmama shi kuma yayi hailala**»

(An-nasa'i ya ruwaito shi).

kuma «idan ya dawo daga yaƙi ko hajji ko umra, **yana yin kabbara sau uku akan dukkan wani tudu akan hanya sannan yace: La'ila ha illallah, wahdahu la sharikallah, lahul mulku walahul hamdu wahuwa ala kulli shai'in ƙadeer**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

a lokacin ayukkan alkhairi -kamar kwanaki goma na zhil-hijja:- ana son yawaita faɗin kalmar tauhidi, kuma ana buɗe farkon huɗubobi ne da tauhidi, kuma a yayin mu'amalarsa da mutane, idan kuma bawa ya zauna a majalisin da magan-ganu sukayi yawa sai kafin ya tashi daga wurin ya ce:

«**Subhanakallahumma wabi hamdika, ash'hadu alla ilaha illa Anta, Astagfiruka wa atubu ilaika; za'a gafarta masa abinda ya kasance akansa a wannan majilisin nasa**»

(At-tirmizi ya ruwaito shi),

kuma «**wanda ya farka a cikin dare ya faɗeta sannan kuma yayi addu'a za'a karɓa masa, kuma idan yayi alwala yayi salla za'a karɓi sallarsa**»

(Bukhari ya ruwaito shi).

a lokacin damuwa da baƙin ciki, bawa yana cewa:

«**La'ila ha illallah Al-azhimu Al-halim, La'ila ha illallah Rabbul Al-arshil Al-adheem, La'ilaha illallah Rabbu Al-samawaati wa Rabbul Al-arshil kareem**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

kuma yabon Allah da ita kafin roƙonSa sanadi ne na karɓar addu'a; Allah -Mai tsarki- ya ce:

﴿وَذَا ٱلنُّونِ إِذ ذَّهَبَ مُغَٰضِبٗا فَظَنَّ أَن لَّن نَّقۡدِرَ عَلَيۡهِ فَنَادَىٰ فِي ٱلظُّلُمَٰتِ
أَن لَّآ إِلَٰهَ إِلَّآ أَنتَ سُبۡحَٰنَكَ إِنِّي كُنتُ مِنَ ٱلظَّٰلِمِينَ ۞
فَٱسۡتَجَبۡنَا لَهُۥ وَنَجَّيۡنَٰهُ مِنَ ٱلۡغَمِّۚ﴾

((Kuma ma'abocin kifi a lokacin da ya tafi yana mai fushi, sai ya yi zaton cewa ba za Mu ƙuƙunta masa ba. Sai ya yi kira a cikin duffai cewa: Babu abin bautawa da gaskiya face Kai. tsarki ya tabbata a gare Ka. Lallai na kasance daga azzalumai sai muka karɓa masa kuma muka tsreratar dashi daga baƙin ciki)) [Al-anbiya`:87-88],

Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Babu wani mutum musulmi da zai yi roƙo da ita a neman wani abu; face sai Allah ya karɓa masa**»

(At-tirmizi ya ruwaito shi).

kuma itace kaffarar yin rantsuwa da wanin Allah; Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Duk wanda yayi rantsuwa yace: Na rantse da Lata da Uzza; to, yace: La'ilaha illallah**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

kuma anso a laƙƙanata ga wanda mutuwa ta zo masa; Manzo Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Ku laƙƙanawa mamatanku: La'ila ha illallah**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma zuwa gareta ne ake kiran wanda ba musulmi ba koda yana ƙarshen rayuwarsa ne; a yayinda mutuwa tazowa Abu Ɗalib sai Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Ya Baffa na, kace: La'ilaha illallah, kalma ce wacce zan maka shaida da ita a wurin Allah**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

**Bayan haka, ya ku Musulmai:**

Samun ɗaukaka yana a cikin tauhidi; Umar -Allah Ya yarda dashi- yace:

«Mu mutane ne da Allah ya ɗaukaka mu da Musulunci», kuma kalmar shahada itace adireshin musulunci kuma alamarsa, kuma maganar da aiki yake war-wareta batada amfani, kuma duk wanda bai faɗeta ba haƙiƙa ya rasa samun daɗin duniya da lahira, kuma karfin musulmai da rauninsu yana da alaƙa da tsayarda wannan kalmar a zance da aiki, itace mizaninsu a wurin Allah da mutane, idan tayi ƙarfi a wurinsu, Allah zai yarda dasu kuma su samu ƙarfi da ɗaukaka, kuma idan tayi rauni zasu yi nesa daga Allah, sannan su yi rauni kuma su sukur-kunce (rauni).

Ina neman tsarin Allah daga shaidan jefaffe.

﴿فَٱعۡلَمۡ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ وَٱسۡتَغۡفِرۡ لِذَنۢبِكَ وَلِلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِۗ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ مُتَقَلَّبَكُمۡ وَمَثۡوَىٰكُمۡ﴾

((Saboda haka ka sani cewa, babu abin bautawa da gaskiya face Allah, kuma ka nemi gafarar zunubinka, dana muminai maza da muminai mata kuma Allah Ya san jujjuyarku (da rana) da kuma makomarku (cikin dare)) [Annamli:19].

Allah Yasa min albarka tareda a cikin Alƙur'ani mai girma.

# HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gare Shi akan samun dacewa da kuma ni'imominSa, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya ina mai girmama al'amarinSa, kuma ina shaida cewa Muhammad bawanSa ne kuma manzonSa ne, Allah yayi daɗin tsira da aminci a gare shi da iyalansa da sahabbansa.

**Yaku musulmai:**

Sanin ma'anar kalmar tauhidi da aiki da ita da kuma nisantar abinda yake kishiyantarta ko kuma yake warwareta sharaɗi ne na samun abinda take gadarwa waɗanda suka zo a cikin dalilai na addini, ma'anarta shine: Kore bauta ta gaskiya daga duk wanin Allah, da kuma tabbatarda ita ga Allah Shi kaɗai, kuma wannan shine abinda kafiran Ƙuraishawa sukayi inkari, Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿إِنَّهُمْ كَانُوٓاْ إِذَا قِيلَ لَهُمْ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ يَسْتَكْبِرُونَ﴾

((Lallai su, sun kasance idan akace masu: Babu abin bautawa da gaskiya face Allah, sai suyi girman kai)) [As-saffaat:35],

kuma yardarsu da tauhidin rububiyyah (kaɗaita Allah wajen halitta da gudanarwa) shi kaɗai bai amfanesu ba.

kuma duk wanda yafi sanin ma'anarta, to zai fi tsayuwa kan abinda take nunarwa, mizaninsa zai fi nauyi, kuma mutane suna banbanta da juna ne gwargwadon yanda suka tsayar da sharuɗɗanta, kuma ruhin wannan kalma da sirrinta shine kaɗaita Allah da bauta, duk wanda ya haɗa wani abin halitta a cikin haƙƙin Allah da bautarSa to ya warware faɗinsa ga «La'ilaha illallah».

kuma mai arziki shine wanda ya kiyaye tauhidinsa kuma ya mutu akansa, bai gurɓatashi ba da wani abu dake warwareshi ba, ko abinda ke sukarsa, ko abinda ke tauye shi, kuma wannan shine burin bayin Allah masu gaskiya:

﴿تَوَفَّنِي مُسْلِمًا وَأَلْحِقْنِي بِٱلصَّٰلِحِينَ﴾

((ka kashe ni ina musulmi kuma ka riskar dani da mutane na gari)) [Yusuf:101].

sannan ku sani cewa, lallai Allah ya umurceku da yin salati da sallama ga AnnabinSa....

# MAFI SOYUWAR AIKI A WURIN ALLAH(1)

Dukkan godiya sun tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa da gafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrukan kawunanmu da zunubban ayukkanmu, wanda Allah Ya shiryar babu mai ɓatar dashi, kuma wanda Ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma manzonSa ne, Allah yayi dadin tsira da amincin a gare shi da iyalan gidansa da sahabbansa.

**Bayan haka:**

Ya ku bayin Allah, kuji tsoron Allah haƙiƙanin jin tsoro, kuma kuyi riƙo da igiyarnan mai ƙarfi daga cikin musulunci.

**Ya ku Musulmai:**

Allah Ya hallici bayinSa, kuma Ya hore masu duk abinda yake cikin sammai da ƙasa, kuma Ya cika masu ni'imominSa na zahiri dana ɓoye; don kawai su kaɗaita shi da bauta, sai mutane suka kasance bayan Annabi Adam har tsawon ƙarni goma suna bautar Allah Shi kaɗai, sai kuma shaiɗan ya ƙawatama wasu mutane bautar gumaka, kuma suka bauta masu; sai Allah Ya aiko da Manzanni kuma Ya saukar masu da littattafai; domin mutane su koma zuwaga bautar Allah Shi kaɗai, kuma yana daga cikin tausayawarSa ga halittunSa, Ya sanya fiɗirarsu dai-dai da abinda ya hallicesu domin shi, dukkan wani abin haihuwa ana haihuwarsa ne akan tsarin kaɗaita Allah da bauta, kuma akan cewa Shine abin bauta Shi kaɗai koma bayan waninSa, Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿فِطْرَتَ ٱللَّهِ ٱلَّتِى فَطَرَ ٱلنَّاسَ عَلَيْهَا﴾

((Halittar Allah wacce Ya halicci mutane akanta)) [Ar-ruum:30].

kuma shaiɗan yana ta ƙoƙari don ɓata abinda aka halicci mutane akansa; domin Ya haramtama bayi samun yardar Ubangijinsu a garesu, kuma daga samun ni'ima tabbatatta wacce aka tanada masu acikin Aljannah dawwamamma, wata rana a cikin wata huɗuba, Manzon Allah -tsira da

(1) Anyi wannan huɗubar ne a masallacin Manzon Allah tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi a ranar Juma'a, ashirin da tara ga watan Shawwal, shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da talatin da ɗaya bayan Hijra.

aminci su tabbata a gare shi ya ce:

«**Ku saurara, lallai Ubangiji na Ya Umarceni da in sanar da ku abinda baku sani ba daga cikin abinda Ya sanar da ni a wannan rana, lallai Ni na hallici bayiNa akan addini miƙaƙƙe, amma shaiɗanu suka zo masu suka karkatar dasu daga addininsu. kuma suka haramta masu abinda na halatta masu, suka umurce su da suyi shirka da ni ga abinda ban saukar masu da wani dalili ba akai**»

(Muslim ya ruwaito shi).

Iblis yana kiran hallitu zuwa faɗawa a cikin mafi girman zunubi da ake saɓama Allah dashi;

an tambayi Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-: «Wane zunubi ne mafi girma? Sai yace: **ka haɗa Allah da kishiya alhali kuwa shine ya halicce ka**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi);

sai mutane da yawa suka bautama wanin Allah; kamar yadda Allah Mai tsarki yace:

﴿وَلَٰكِنَّ أَكۡثَرَ ٱلنَّاسِ لَا يُؤۡمِنُونَ﴾

((Sai dai mafi yawan mutane basa imani)) [Ar-ra`ad:1].

kuma yana daga cikin munin sakamakon rashin yin imani; dukkan wani aiki -koda na ƙwarai ne- ba'a sakama bawa akansa; saboda rashin samuwar asalin Addini;

Aishah -Allah Ya yarda da ita- ta ce: «Ya Manzon Allah! Dan Jud'aan ya kasance a zamanin Jahiliya yana sada zumunci, yana ciyarda mabuƙata; shin wannan kuwa zai amfane shi? sai yace: **ba zai amfane shi ba; domin babu ranar daya taɓa cewa: Ya Ubangiji ka yafe min kusakurai na a ranar sakamako**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma wannan laifin sanadi ne na fushin Allah, da saukar ƙasƙanci da wulaƙanci ga wanda ya aikata shi; Allah Mai girma da ɗaukaka ya ce:

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ ٱلۡعِجۡلَ سَيَنَالُهُمۡ غَضَبٞ مِّن رَّبِّهِمۡ وَذِلَّةٞ فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَاۚ﴾

((Lallai ne waɗanda suka riƙi wannan maraƙin, wani fushi daga Ubangijinsu da wani wulaƙanci a cikin rayuwar duniya, zasu same su)) [Al-a`raaf:152].

kuma ma'abocinsa yana jujjuyawa ne a cikin baƙin ciki da damuwa, da

ɓacin rai; Allah Mai girman al'amari ya ce:

﴿وَمَن يُرِدۡ أَن يُضِلَّهُۥ يَجۡعَلۡ صَدۡرَهُۥ ضَيِّقًا حَرَجٗا كَأَنَّمَا يَصَّعَّدُ فِي ٱلسَّمَآءِۚ﴾

((kuma wanda ya nufi ya ɓatar sai ya sanya ƙirjinsa ya kasance cikin ƙunci da damuwa tamkar mai ƙokarin hawa sama amma baya iyawa)) [Al-an`aam:125].

kuma yana hana shi shiga Aljannah kuma ya dawwammar dashi a cikin wuta; Allah Mai girman al'amari ya ce:

﴿إِنَّهُۥ مَن يُشۡرِكۡ بِٱللَّهِ فَقَدۡ حَرَّمَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِ ٱلۡجَنَّةَ وَمَأۡوَىٰهُ ٱلنَّارُۖ وَمَا لِلظَّٰلِمِينَ مِنۡ أَنصَارٖ﴾

((Tabbas, wanda ya haɗa Allah da wani, to haƙiƙa Allah ya haramta Aljannah a gare shi kuma makomarsa itace wuta)) [Al-maaidah:72].

kuma don kada bayi su faɗa a cikin tarkon shaiɗan, su fusata Ubangijinsu, kuma a dawwamar dasu a cikin wuta; Allah Ya aikama kowace al'umma da Manzo domin yayi masu gargaɗi daga karɓar kiran shaiɗan kuma ya umurce su da bautawa Allah Mai Rahma, kuma ya saukar da littattafai, kuma yayi kira zuwa gare shi a cikin mafi yawan ayoyin Al-ƙur'ani, kuma dukkan abinda yake cikin Al-ƙur'ani yana nuni zuwa gare shi, kuma umurni na farko a cikin littafin Allah shine umurni da shi, Allah Mai girma da ɗaukaka ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱعۡبُدُواْ رَبَّكُمُ ٱلَّذِي خَلَقَكُمۡ﴾

((Ya ku mutane, ku bautawa Ubangijinku wanda ya halicce ku)) [Al-baƙarah:21].

Ma'ana: ku kaɗaita Ubangijinku, kuma hani na farko da mai karatun Al-ƙur'ani zai riska shine hani daga kishiyar tauhidi:

﴿فَلَا تَجۡعَلُواْ لِلَّهِ أَندَادٗا وَأَنتُمۡ تَعۡلَمُونَ﴾

((Kada ku sanyama Allah kishiyoyi, alhali kuma kuna sane)) [Al-baƙarah:22].

Kuma suratul-Ikhlas tana matsayin ɗaya bisa uku na Al-ƙur'ani; saboda tana ƙunshe ne da tauhidi, kuma mafi girman aya a cikin littafin Allah itace ayar datake ƙunshe da bayanin kaɗaita Shi: Wato Ayatul-kursiyy

kuma Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya shafe shekara goma yana kiran mutane zuwa ga tauhidi, baya kira zuwa wani abu bayansa, sannan daga baya hukunce-hukuncen shari'a suka biyo bayansa, sannan ya kasance yana kira zuwa garesu tareda da tauhidin har zuwa

mutuwarsa, kuma ya kasance da safe da kuma yamma yana cewa:

«**Mun wayi gari akan hanyar musulunci, akan kalmar Ikhlasi, akan Addinin Annabinmu Muhammad -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- kuma akan hanyar Ibrahim miƙaƙƙiya wanda ya kasance bisa miƙaƙƙiyar hanya kuma musulmi kuma bai kasance daga cikin masu shirka ba**».

(Ahmad ya ruwaito shi),

kuma ya kasance yana buɗe wuninsa da tauhidi, a cikin raka'o'i biyu na nafila bayan ketowar alfijir yana karanta suratu (Al-kafirun) da suratu (Al-ikhlas), kuma ya rufe wuninsa da kataun suratu (Al-kafirun) a cikin shafa'i da suratu (Al-ikhlas) a cikin wutiri.

kuma yayiwa al'ummarsa wasiyya da shi, wani balaraben ƙauye yazo wurin Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-, sai yace:

«**Ka nuna min wani aiki wanda idan nayi shi zan shiga Aljannah? yace: ka bautama Allah kada ka haɗa shi da wani abu, kuma ka tsayar da Sallar da aka wajabta maka, kuma ka bada zakka wadda aka wajabta, kuma kayi azumin Ramadan**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi),

kuma ya kasance yana umurtar sahabbansa dasuyi masa muba'yi'a akan bautama Allah Shi kaɗai; Auf ɗan Malik -Allah Ya yarda dashi- ya ce:

«Mun kasance a wurin Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- mu tara ko takwas ko bakwai, sai yace: **Shin bazaku yima Manzon Allah mubayi'a ba? sai muka ce: Ai munyi maka mubayi'a ya Manzon Allah! akan mene ne kuma zamu yi maka wata mubayi'ar? Sai yace: Akan zaku bautama Allah kuma kada ku haɗa Shi da komai, kuma akan salloli guda biyar**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma idan ya aika masu kira zuwa garuruwa: Yana umurtarsu dasu fara kira zuwa ga tauhidi; ya aika Mu'az zuwa Yaman kuma yace mashi:

«**Lallai kai zaka je wurin wasu mutane ma'abota littafi, ka kirasu zuwa shaidawa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, kuma ni Manzon Allah ne**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi),

kuma idan tawagar wasu mutane suka zo masa yana sanar dasu tauhidi; tawagar mutanen Abdu Ƙais sunzo masa sai yace masu:

«**Shin ko kun san mene ne imani da Allah Shi kaɗai kuwa? Suka ce: Allah da ManzonSa sukafi sani, sai yace: Shaida cewa lallai babu abin**

**bauta da gaskiya sai Allah kuma Muhammad Manzon Allah ne...**» har zuwa karshen hadisin.

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

kuma Annabawa sunjima ƴaƴansu tsoron bin shaiɗan ta hanyar bautar gumaka; Badaɗayin Allah -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

﴿وَٱجْنُبْنِي وَبَنِيَّ أَن نَّعْبُدَ ٱلْأَصْنَامَ﴾

((Kuma ka nisantar dani da ƴaƴana daga bautar gumaka)) [Ibrahim:35]

kuma Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yajiwa al'ummarsa tsoron faɗawa a cikin shirka, yace:

«**Mafi tsoron abinda nake ji maku tsoro akansa shine; ƙaramar shirka, sai aka tambaye shi mece ce ita, sai yace: Riya**»

(Ahmad ya ruwaito shi),

kuma shi tauhidi yana daga cikin haƙƙin Allah akan bayi, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Ya kai Mu'az! shin ko kasan menene haƙƙin Allah akan bayi? Yace: Allah da ManzonSa ne sukafi sani, yace: Lallai haƙƙin Allah akan bayi: su bautata maSa kuma kada su haɗa Shi da komai**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

kuma yana kusanto da bawa ga Aljannah kuma ya nisanta shi daga Wuta; wani balaraben ƙauye yazo wurin Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-, sai yace:

«**Ka bani labarin abunda zai kusantar dani ga Aljannah kuma ya nisantar dani daga Wuta, sai Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya kame daga bashi amsa sannan ya dubi sahabbansa yace: lallai yasamu dacewa -**ko tabbas an shiryar dashi**- sai yace: shin ya kace:** sai ya maimaita -tambayarsa- sai Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce**: Ka bautawa Allah kada ka haɗa shi da komai, ka tsayarda Sallah, ka bada Zakka, kuma ka sada zumunci**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

kuma babu cin nasara a duniya da lahira sai dashi; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce: «**Kuce: La'ilaha illallah; zaku samu rabauta**» (Ahmad ya ruwaito shi),

kuma duk wanda ya cika da shahada zai shiga Aljannah; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Duk wanda ƙarshen maganarsa itace: La'ila ha illallah; zai**

**shiga Aljannah**»

(Abu Dawuda ya ruwaito shi),

kuma duk wanda ya mutu akansa zai shiga Aljannah kuma ya tsira daga Wuta; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Duk wanda ya haɗu da Allah baya haɗa Shi da komai, to zai shiga Aljannah, kuma duk wanda ya haɗu da Shi alhalin yana yin maSa shirka to zai shiga Wuta**».

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma ayukkan masu tauhidi suna banbanta a daraja ne gwargwadon abinda yake cikin zukatansu na imani da Ikhlasi. kuma mafi girman abinda musulmi ya mallaka shine tauhidinsa ga Ubangijinsa, kuma mafi muhimmancin abinda yake akansa shine; kiyayeshi daga lalacewa, ko samun wata suka, ko wata tawaya dake iya bijiro masa; Ibnul-Ƙayyim -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«Tauhidi shine mafi ɓoyuwar abu kuma mafi tsaftar abu kuma shine mafi kyawun abu, ɗan ƙanƙanin abu yana illata shi ya ɓata shi, kuma yayi tasiri a cikinsa, kamar fararen tufafi yake, ɗan ƙanƙanin abu yana bayyana a ckikinsa, kuma kamar tsabtattaccen madubi ne: ɗan ƙanƙanin abu yana tasiri a cikinsa».

Kuma Allah Mai girma da ɗaukaka yayima ManzanninSa wahayi cewa idan suka haɗa Shi da wani ayukkansu zasu lalace, ina ga waninsu?! Allah Mai girma da ɗaukaka ya ce:

﴿وَلَقَدۡ أُوحِيَ إِلَيۡكَ وَإِلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكَ
لَئِنۡ أَشۡرَكۡتَ لَيَحۡبَطَنَّ عَمَلُكَ وَلَتَكُونَنَّ مِنَ ٱلۡخَٰسِرِينَ﴾

((Lallai Mun yi wahayi a gare ka da kuma waɗanda suka gabace ka cewar in ka yi shirka tabbas aikinka zai ɓaci kuma za ka kasance daga cikin taɓaɓɓu)) [Az-zumar:65],

wannan yasa Annabi Ibrahim -aminci ya tabbata a gare shi- yaji tsoron shirka, sai ya roƙi UbangijinSa -a lokacinda yake gina Kaaba-:

﴿وَٱجۡنُبۡنِي وَبَنِيَّ أَن نَّعۡبُدَ ٱلۡأَصۡنَامَ﴾

((Kuma ka nisantar dani da ƴaƴana daga bautar gumaka)) [Ibrahim:35].

kuma idan badaɗayin Allah yana tsoron shirka ga kansa; tabbasa, waninsa yafi can-canta dayaji tsoro.

kuma koyarda ƴaƴa ginshiƙin addininsu da tambayarsu akansa shine tafarkin Annabwa; Annabi Ya'aƙub -aminci ya tabbata a gare shi- ya kasance a lokacin fitar ransa yana tambayar ƴaƴansa gameda tauhidi:

﴿أَمۡ كُنتُمۡ شُهَدَآءَ إِذۡ حَضَرَ يَعۡقُوبَ ٱلۡمَوۡتُ إِذۡ قَالَ لِبَنِيهِ مَا تَعۡبُدُونَ مِنۢ بَعۡدِيۖ قَالُواْ نَعۡبُدُ إِلَٰهَكَ وَإِلَٰهَ ءَابَآئِكَ إِبۡرَٰهِـۧمَ وَإِسۡمَٰعِيلَ وَإِسۡحَٰقَ إِلَٰهٗا وَٰحِدٗا وَنَحۡنُ لَهُۥ مُسۡلِمُونَ﴾

((Ko kun kasance halarce a lokacin da mutuwa ta zo ma Ya'aƙub, a lokacin da ya ce wa ƴaƴansa: Mene ne za ku bautama a bayana? Suka ce: Muna bauta wa Abin bautawarka kuma Abin bautawar iyayenka lbrahim da lsma'ila da Is'haƙa, Ubangiji Guda, kuma mu a gare Shi masu miƙa wuya ne)) [Al-baƙarah:133].

kuma Annabinmu Muhammad yana tambayar ƙaramar kuyanga: «**Ina Allah yake? tace: yana sama**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma karatun littattafan aƙida ta ƙwarai da lizimtar halƙoƙin ma'abota ilimi na daga cikin hanyoyin samun tabbata; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Na bar maku ababe guda biyu waɗanda bazaku ɓace ba dasu: Littafin Allah da Sunnah ta**»

(Hakim ya ruwaito shi),

Shehu Muhammad Dan Abdul-Wahhab -Allah ya jikansa- ya ce:

«Mafi muhimmancin abinda yake akanka: Shine sanin tauhidi kafin sanin Ibada dukkanta har Sallah»,

kuma yin addu'a ta samun tabbatuwa akan addini hanyar Annabawa ce; Annabi Yusuf -aminci ya tabbata a gare shi- ya ce:

﴿تَوَفَّنِي مُسۡلِمٗا وَأَلۡحِقۡنِي بِٱلصَّٰلِحِينَ﴾

((Ka kashe ni ina musulmi kuma ka riskar dani da mutane managarta)) [Yusuf:101].

kuma girmama tauhidin Mahallici, da sanin muhimmancinsa, da nisantar ababe masu rikitarwa yana daga cikin sabbubban samun shiriya.

Ina neman tsarin Allah daga shaidan jefaffe.

﴿فَٱعۡلَمۡ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ وَٱسۡتَغۡفِرۡ لِذَنۢبِكَ وَلِلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِۗ

﴿وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ مُتَقَلَّبَكُمۡ وَمَثۡوَىٰكُمۡ﴾

((Saboda haka ka sani, cewa babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, kuma ka nemi gafara ga zunubin ka dana muminai maza da muminai mata kuma Allah Ya san jujjuyawarku da makomarku -cikin dare-)) [Muhammad:19].

Allah Yasa min albarka tareda daku a cikin Alƙur'ani mai girma...

# HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gare Shi akan samun dacewa da kuma ni'imominSa, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya ina mai girmamawa ga al'amarinSa, kuma ina shaida cewa Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah yayi daɗin tsira da amincin Allah a gare shi da iyalansa da sahabbansa.

**Ya ku Musulmi:**

Tauhidi shine mafi girman abinda rayuka suke tsarkaka dashi, kuma baya tabbata sai da kafircewa dukkan abinda ake bauta koma bayan Allah, kuma wannan shine ma'anar kalmar Shahada; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

Duk wanda yace "La'ilaha illallah", kuma ya kafircewa duk wani abin da ake bauta koma bayan Allah, an haramta taɓa dukiyarsa da jininsa, kuma hisabinsa yana ga Allah Maɗaukaki.

(Muslim ya ruwaito shi),

kuma duk wanda ya tsayarda tauhidi baƙin cikinsa ya yaye, kuma ya samu yarda Ubangijinsa, kuma an karɓi ayukkansa, an ruɓunya ladarsa, kuma rayuwarsa zata kasance rayuwa mai daɗi, kuma an yafe masa zunubbansa, kuma zai shiga Aljannah ba tareda hisabi ba ko azaba, kuma babu wata ni'ima wadda tafi girma sama da ni'imar Addini da tabbata akansa.

sannan ku sani cewa, lallai Allah Ya umurceku da yin salati da sallama ga AnnabinSa....

# GIRMAN ALLAH[1]

Dukkan godiya sun tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa da gafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrukan kawunanmu da zunubban ayukkanmu, wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, kuma wanda ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina sheda cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya, kuma ina sheda cewa tabbas Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, yabon Allah mai yawa da aminci su tabbata a gare shi da iyalan gidansa da sahabbansa.

**Bayan haka:**

Ya ku bayin Allah, kuji tsoron Allah haƙiƙanin tsoro, kuma kuyi riƙo acikin addini da igiya mai ƙarfi.

**Ya ku Musulmi:**

Allah Ya samarda bayi daga rashi, kuma Ya ƙarfafe su da ni'imomi, kuma Ya yaye masu damuwowi da musibu, kuma lafiyayyar fiɗira tana son wanda Yayi ni'ima da kyautatawa a gareta, kuma buƙatar rayuka ga sanin Ubangijinta yafi girama sama da buƙatuwarta zuwa ga abinci, da abin sha, da nunfashi, kuma ba'a samun nasara a gidan duniya da lahira sai da sanin Allah da ƙaunarSa da bautarSa, kuma duk wanda yafi mutane saninSa shine yafi tsananin girmamaSa da imani da Shi.

kuma ibadar zuciya tafi girma da yawa da dawwama akan ibadar gaɓɓai, domin ita wajiba ce a kowane lokaci, kuma ayukan gaɓɓai ana yinsu ne don gyaran zuciya; Ibnul-Ƙayyim -Allah Ya jiƙansa- yana cewa:

«kuma Allah yana ajiye bawa a matsayin da bawa ya ajiye Allah ga kansa», kuma idan bawa yasan Ubangijinsa; rayuwarsa da zuciyarsa zasu samu natsuwa zuwa gare Shi, kuma duk wanda yafi sanin Allah da siffofinSa, dogaronsa ga Allah zaifi kasancewa ingantacce kuma mai ƙarfi, kuma mafi kamalar masu bautar daga cikin mutane; shine mai girmama Allah, mai bautarSa da dukkan sunayenSa da siffofinSa.

Kuma Allah Mai tsarki yanada mafi kyawawan sunaye, kuma sunayenSa yabo ne da girmamawa, kuma yanada mafi ɗaukakan siffofi -Kuma siffofinSa siffofi ne na kamala- Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya kasance yana cewa a cikin ruku'insa:

(1) Anyi wannan huɗubar ce a masallacin Manzon Allah, a ranar Juma'a, goma sha takwas ga watan Jumada Al-ula, shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu talatin da biyu bayan Hijra.

«**Tsarki ya tabbata a gareKa, ya ma'abocin ji-ji da kai, da mulkin komai da komai, da jin isa, da girma**»

(Al-nasa'i ya ruwaito shi),

Allah yanada kamala cikakkiya a cikin komai; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa:

«**Bana iya ƙidanye yabo agareKa, kamar yadda Kai Ka yabi kanKa**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma dukkan wanda yake a cikin sammai da ƙasa suna tsarkake Allah daga kowane aibu da tawaya; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿سَبَّحَ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۖ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ﴾

((Abin da ke cikin sammai da abin da ke cikin ƙasa suna tsarkake Allah, kuma Shine Mabuwayi Mai hikima)) [Al-hashr:1].

kuma dukkansu suna yin sujada a gare shi; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَلِلَّهِ يَسۡجُدُ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِ مِن دَآبَّةٖ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ وَهُمۡ لَا يَسۡتَكۡبِرُونَ﴾

((Kuma ga Allah ne, abin da yake a cikin sammai da ƙasa na dabba da Mala'iku, suke yin sujjada, kuma basu girman kai)) [An-nahl:49].

halitta da umurni duka na Allah ne Mai tsarki, gwani a cikin duk abinda yayi, ya kyautata duk abinda ya halitta, kuma ya ƙaddara duk ƙaddarorin halittu tun kafin ya hallici sammai da ƙasa da shekaru dubu hamsin, kuma hukunci naSa ne, babu mai tarayya daShi a cikin wannan, babu mai iya mayarda abinda ya ƙaddara, kuma ba mai iya cin gyara a hukuncinSa, rayayye ne baya mutuwa, dukkan hallitu suna ƙarƙashin buwayarSa da damƙarsa, shi ke kashe su kuma ya raya dasu, yasa su dariya kuma yasa su kuka, ya azurta su kuma ya talauta su, kuma shine ke surantasu a cikin mahaifa kamar yadda yaso.

﴿مَّا مِن دَآبَّةٍ إِلَّا هُوَ ءَاخِذُۢ بِنَاصِيَتِهَآۚ﴾

((kuma babu wata dabba face shi ne yake rike da ƙoƙuwar kanta)) [Huud:56]

Yana gudanar da ita yadda yake so, kuma zukatan bayi suna tsakanin ƴan yatsunSa yana juyasu yadda yake so, kuma makwarkwaɗar kansu tana a hannunSa, kuma gudanar al'amurra yana ƙulle ne ga tsarawarSa da ƙaddarawarSa.

ba wani mai iya masa jayayya, kuma ba wanda zai iya rinjayarSa, da dukkan al'umma zasu haɗu akan su cutar da wani kuma Allah bai rubuta hakan ba, ba zasu iya cutar dashi ba, kuma da zasu haɗu don su amfanar dashi kuma Allah bai yi nufin hakan ba, babu mai iya amfanar dashi.

babu mai iya tunkuɗe azabarSa idan ta sauka, kuma ba mai iya ɗauketa idan ta faru bayan shi, yana halittar abinda yaso, kuma yana aikata abinda yayi nufi

﴿لَا يُسۡـَٔلُ عَمَّا يَفۡعَلُ﴾

((Ba'a tambayarSa akan abinda Yake aikatawa)) [Al-anbiya`:21]

su kuma hallittu ana tambayarsu, tsayayye ne da kanSa, ya wadata daga halittunSa, yana kiyaye dasu baki ɗayansu, kuma makullan gaibi suna wurinSa babu wanda ya sansu sai shi, ya ɓoye saninsu har ga mala'iku; basu san wanda zai mutu a gobe ba ko abinda zai faru a duniya kafin faruwarsa.

Sarki ne wanda yake gudanar da al'amurran bayinSa, yana umurni da hani, yana badawa kuma yana hanawa, yana saukarwa kuma ɗaukakawa, umurninSa suna bibiyar juna lokaci bayan lokaci, kuma suna gudana ne gwargwadon nufinSa da sonSa, duk abinda yaso shi yake kasancewa, kuma abinda bai so ba bazai kasance ba

﴿يَسۡـَٔلُهُۥ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ كُلَّ يَوۡمٍ هُوَ فِي شَأۡنٖ﴾

((duk wanda ke a cikin sammai da ƙasa yana roƙon Sa, a kullum Yana a cikin wani sha'ani)) [Ar-rahman:29].

kuma yana daga cikin sha'aninSa: Yaye damuwa, ya ƙarfafi wanda ya samu karayar zuci, ya azurta talaka, ya karɓa roƙon mai addu'a, Allah Mai tsarki yace gameda kanSa:

﴿وَمَا كُنَّا عَنِ ٱلۡخَلۡقِ غَٰفِلِينَ﴾

((kuma bamu kasance masu gafala ba daga hallitu ba)) [Al-mu`minuun:17].

IliminSa ya yalwaci komai, ya san duk abinda ya faru, da abinda zai faru da abinda ba zai faru ba, ƙwayar zarra ko abinda yafita girma da ba zatayi motsi ba sai da izininSa, kuma ba wani ganye da zai faɗo sai da izininSa, ba wani abu ɓoyayye da zai ɓoyu a gare Shi, ɓoye da bayyane duka ɗaya ne a wurinSa, Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿سَوَآءٞ مِّنكُم مَّنۡ أَسَرَّ ٱلۡقَوۡلَ وَمَن جَهَرَ بِهِۦ وَمَنۡ هُوَ مُسۡتَخۡفِۭ بِٱلَّيۡلِ وَسَارِبُۢ بِٱلنَّهَارِ﴾

((Daidai ne daga gare ku, wanda ya asirta magana da wanda ya bayyana ta, da wanda yake shi mai neman ɓoyewa ne cikin dare, da mai bayyanawa a cikin tafiyarsa a hanya da rana)) [Ar-ra`ad:10].

yana jin sautukkan halittu alhali kuma yana akan Al'arshinSa, Aishah -Allah Ya yarda da ita- ta ce:

«Godiya ta tabbata ga Allah wanda jinSa ya yalwaci dukkan sautuka, mai jayayya -game da mijinta- tazo wurin Annabi -tsira da amincin Allah su tabba a gare shi- tana masa magana, kuma ni ina a gefe a cikin ɗakin amma bana jin abunda take faɗi, sai Allah Mai girma da ɗaukaka ya saukar da:

﴿قَدْ سَمِعَ ٱللَّهُ قَوْلَ ٱلَّتِي تُجَٰدِلُكَ فِي زَوْجِهَا وَتَشْتَكِيٓ إِلَى ٱللَّهِ وَٱللَّهُ يَسْمَعُ تَحَاوُرَكُمَآۚ
إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعُۢ بَصِيرٌ﴾

((Lallai Alla Ya ji maganar wacce ke yi maka jayayya game da mijinta, tana kai ƙara ga Allah, kuma Allah yana jin tattaunawarku. Lallai Allah Mai ji ne, Mai gani)) [Al-mujadalah:1].

(Ahmad ya ruwaito shi),

Kuma ayukkan bayi a cikin baƙin duhun dare basa ɓoyuwa a gare Shi, Allah Maɗaukakin sha'ani ya ce:

﴿ٱلَّذِي يَرَىٰكَ حِينَ تَقُومُ ۝ وَتَقَلُّبَكَ فِي ٱلسَّٰجِدِينَ﴾

((Wanda Yake ganin ka a lokacin da kake tashi tsaye.

Da jujjuyawarka a cikin masu yin sujada)) [Ash-shu`ara`:218-219].

yana can a saman sammanSa amma yana ganin tafiyar baƙar tururuwa akan kurman dutse a cikin duhun dare.

taskokinSa a cike suke cikin sammai da ƙasa, kuma hannayenSa a shinfiɗe suke da karamci «**mai kyauta da yawa dare da wuni**», yana ciyarwa yadda yake so, mai yawan kyauta, mai yalwar baiwa, yana badawa kafin a roƙe Shi da bayan roƙonSa, kuma yana saukowa «**cikin kowane dare zuwa saman duniya lokacin da ɗayan ukun dare na ƙarshe yayi saura, yana cewa: Wa zai roƙe Ni in amsa masa?, Wa zai tambayeni in bashi?**», kuma yana fushi da wanda baya roƙonSa.

ya buɗe ƙofofin kyautarSa ga bayinSa, shine wanda ya hore tekuna, ya gudanar da gulabe, ya zuba arzuka, yaba hallitu arzukansu; ya arzuta tururuwa dake can cikin ƙasa, da tsuntsaye a cikin sararin samaniya, da kifaye a cikin ruwa:

﴿وَمَا مِن دَآبَّةٖ فِي ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِ رِزۡقُهَا﴾

((kuma babu wata dabba a cikin ƙasa face arzikinta yana ga Allah)) [Huud:6]

ArzikinSa ya yalwaci komai; Ya kaiwa jinjiri arzikinsa alhali yana a cikin mahaifa, da mai ƙarfi dake kan mulki. Allah mai karamci ne yana son kyauta da karamci, idan aka roƙe Shi yana badawa, kuma baya yarda a kai wata buƙata ga waninSa, kuma duk wani alkairi daga wurinSa yake.

﴿وَمَا بِكُم مِّن نِّعۡمَةٖ فَمِنَ ٱللَّهِۖ﴾

((kuma duk wata ni'ima da kuka samu daga Allah take)) [An-nahl:53].

ArzikinSa baya ƙarewa; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Shin baku ganin abinda ya ciyar tun lokacinda Ya halicci sama da ƙasa? tabbas, ba abinda yin hakan ya rage daga abinda yake cikin damarSa**»

(Muslim ya ruwaito shi),

da dukkan bayi zasu roƙe Shi kuma yaba kowa duk abinda ya roƙe Shi; hakan ba zai ya rage komai daga cikin mulkinSa ba; a ciki hadisin da Annabi -tsira da amincin Allah su tabba a gare shi- yake ruwaitowa daga Allah, ya ce:

«**Yaku bayiNa, da ace na farkonku dana ƙarshenku, da mutanen ku da aljanun ku, zasu tasaya a fili ɗaya su roƙe ni, kuma inbiyama kowa buƙatarsa, da hakan bazai rage komai daga abinda yake wurina ba sai kamar yadda allura take rage wani abu idan aka shigar da ita a cikin teku**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma Yana rubunya ladar ayukka; aiki na ƙwarai a wurinSa yana matsayin nunki goma har zuwa sau ɗari bakwai zuwa nunki mai yawa, kuma yana mayarda ɗan kaɗan acikin lokatan ibada zuwa mai yawa, daren Lailatul -ƙadr yafi watanni dubu alkhairi, kuma azumin kwana uku cikin kowace wata yana matsayin azumin shekara, kuma idan bawa ya ciyarda dukiya don neman yardar Allah zai mayar masa dashi nunki mai yawa, yana bada kyauta sama da abinda ake buri, yaba ƴan Aljannah abinda ido bai taɓa gani ba, kuma kunne bai taɓa ji ba, kuma zuciyar wani mutum bata taɓa tunanin hakan ba, kuma idan bawa yabar wani abu saboda Shi, sai Ya canza masa da wanda yafi shi alkhairi.

Mawadaci ne daga dukkan hallitunSa, kuma komai yanada buƙata zuwa gare Shi.

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ أَنتُمُ ٱلْفُقَرَآءُ إِلَى ٱللَّهِ ۖ وَٱللَّهُ هُوَ ٱلْغَنِىُّ ٱلْحَمِيدُ﴾

((Ya ku mutane! Ku ne masu buƙata zuwa ga Allah, kuma Allah, Shi ne Mawadaci, abin godewa)) [Faaɗir:15],

bayi basa iya kaiwa matsayin amfanar daShi balle su amfane Shi, kuma basa iya kaiwa matsayin cutar daShi balle su ctar daShi, Maɗaukaki ne Mai girma, Alkursiyu shine bagiren kafafunSa, kuma Alkursiyu yafi sammai da ƙasa yalwa, kuma idan aka haɗa sammai guda bakwai da Alkursiyu kamar dirhamomi ne guda bakwai da aka jefa a cikin wata garkuwa, ita Alkursiyyu girmanta a cikin Al'arshi kamar zoben ƙarfe ne wanda aka jefa shi cikin wani falalar daji, kuma Al'arshenSa shine mafi girman hallitunSa, kuma a ƙarƙashin Al'arshi akwai wani teku, kuma nisan dake tsakanin fatar kunnen ɗaya daga cikin mala'ikun dake ɗauke da Al'arshi zuwa kafaɗarsa ya kai tafiyar shekara ɗari bakwai, kuma Ubangijinmu ya daidaita akan Al'arshinSa -irin daidaiton daya dace da ɗaukakarSa da girmanSa- kuma ya wadata daga Al'arshin da duk abinda yake a ƙasa dashi.

Ya kewaye komai da ilminSa amma Shi ba abinda ya kewaye Shi da sani, yana riskar gannai, amma Shi gannai basa riskarSa, kuma ikonSa ya lulluɓe duk hallitunSa, kuma dukan hallitun masu rauni ne a wurinSa koda su hallitun suna ganin girman yadda aka haliccesu, kuma Allah Mai tsarki zai naɗe sammai a ranar ƙiyama, sannan Ya riƙe su da hannunSa na dama sannan ya ce:

«**Ni ne mai mulki, ina masu jiji da kai suke? ina masu girman kai? sannan kuma ya naɗe ƙassai da ɗayan hannunSa, sannan yace: Ni ne mai mulki? ina masu jiji da kai, ina masu girman kai?**»

(Muslim ya ruwaito shi),

kuma zai ɗora «**Sammai akan yatsa ɗaya, ƙassai akan yatsa ɗaya, ruwa da ƙasa akan ɗan yatsa, hallittu akan ɗan yatsa, sannan ya girgiza su, sannan yace: Ni ne mai mulki, Ni ne mai mulki**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi),

idan yayi magana na wahayi, girgiza tana kama sammai, kuma mazauna sama suna sumewa, farkon wanda zai fara farkawa shine Jibril, kuma sammai suna jintsoronSa, Allah Mai girma da ɗaukaka ya ce:

﴿تَكَادُ ٱلسَّمَٰوَٰتُ يَتَفَطَّرۡنَ مِن فَوۡقِهِنَّۚ﴾

((Sammai sun kusa su tsats-tsage daga samansu)) [Ash-shuuraa:5],

Adh-dhahhaak -Allah Ya masa rahama- yace:

«Ma'ana: su tsats-tsagewa saboda girman Allah -wato domin tsoronSa-».

«**Tsayayye ne baya barci, kuma barci bai dace da shi ba, yana rage yawan arziki ga wasu kuma yana ƙarawa yawansa ga wasu, ana ɗaga masa ayukkan dare kafin ayukkan rana, kuma a ɗaga masa ayukkan rana kafin na dare, haske ne shamakinSa, da zai yaye shi da hasken fuskarSa ya ƙone duk abinda ganinSa ya isa zuwa gare shi daga cikin hallittunSa**»

(Muslim ya ruwaito shi).

Yana gudanar da al'amura

﴿مِنَ ٱلسَّمَآءِ إِلَى ٱلۡأَرۡضِ ثُمَّ يَعۡرُجُ إِلَيۡهِ فِي يَوۡمٖ كَانَ مِقۡدَارُهُۥٓ أَلۡفَ سَنَةٖ مِّمَّا تَعُدُّونَ﴾

((daga sama zuwa ga ƙasa, sa'an nan ya hau zuwa gare Shi (Jibril aminci ya tabbata a gare shi) a cikin wani wuni, wanda ya kai gwargwadon shekaru dubu a lissafinku)) [As-sajda:5].

﴿وَلَوۡ أَنَّمَا فِي ٱلۡأَرۡضِ مِن شَجَرَةٍ أَقۡلَٰمٞ وَٱلۡبَحۡرُ يَمُدُّهُۥ مِنۢ بَعۡدِهِۦ سَبۡعَةُ أَبۡحُرٖ مَّا نَفِدَتۡ كَلِمَٰتُ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٞ﴾

((Kuma da ace duk abinda ke cikin ƙasa na itace alƙalumma ne, kuma dukkan tekuna suzama tawada, kuma a ƙaro waɗansu daɗin tekuna bakwai, kalmomin Allah ba za su ƙare ba. Lallai, Allah Mabuwayi ne, Mai hikima)) [Luƙman:27].

Mai ƙarfi ne ba abinda ke gagararSa, idan Ya nufi yin wani abu zai ce mashi: Kasance, sai nan take ya kasance, al'amarinSa kamar kyaftawar ido ne kai yama fi hakan sauri, kuma yanada rundunoni babu wanda yasansu sai Shi, ya kifar da garuruwan mutanen Annabi Luɗu, ya maida samanta ya dawo ƙasa, kuma lokacinda Banu Israela suka ƙi karɓar abinda ke cikin littafin Attaura, sai ya ɗaga wani babban dutse akansu kamar wata inuwa har suka tabbatarda cewa lallai zai faɗo akansu, kuma Allah Mai tsarki ya bayyana ga dutse sai dutsen ya rugurguje, a lokacin da Annabi Musa yaga hakan sai ya faɗi yana sumamme.

kuma zai girgiza ƙasa idan duniya ta ƙare wani irin girgizawa, kuma ya

niƙeta niƙewa, kuma zai sheƙe duwatsu sheƙewa, kuma da huri ɗaya a cikin ƙaho wanda mala'iki Israfeelu zaiyi hallittu zasu firgita, kuma da wata hurawar ta biyu zasu sume sannan data uku zasu tashi don taron ƙiyama. kuma idan Allah mai tsalki ya sauko domin yin hukunci; sama zata tsats-tsage don saukarSa saboda girmamwa a gare Shi da jin tsoronSa.

kuma Allah Mai tsarki ya wuce duk yadda masu siffantawa suke siffanta Shi, kuma yana sama da yadda dukkan masu yabo suke yabonSa, baShi da kishiya ko tamka ko kama ko misali, Manzanni sun san Ubangijinsu sai suka yawaita ƙanƙantar da kai, da bauta da saduda a gare Shi. Annabi Dawud -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya kasance yana azumi rana ɗaya, ya sha ruwa rana ɗaya, kuma Annabinmu Muhammad -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yana sallar dare har kafafunSa suka tsage, kuma Ibrahim -tsira da aminci su tabbata a gare shi ya kasance mai yawan kuka saboda UbangijinSa, kuma mai komawa ne ga Allah, kuma duk wanda yabi tafarkin Annabwa ya samu tsira da jin daɗi.

Ina neman tsarin Allah daga shaidan jefaffe.

﴿وَمَا قَدَرُواْ ٱللَّهَ حَقَّ قَدۡرِهِۦ وَٱلۡأَرۡضُ جَمِيعٗا قَبۡضَتُهُۥ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَٱلسَّمَٰوَٰتُ مَطۡوِيَّٰتُۢ بِيَمِينِهِۦۚ سُبۡحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشۡرِكُونَ﴾

((Kuma ba su girmama Allah ba gaskiyar girmamawa, alhali kuwa ƙasa duka damƙarSa ce a Ranar ƙiyama, kuma sammai abubuwan naɗewa ne da damanSa. Tsarki ya tabbata a gare Shi, kuma Ya ɗaukakarSa ta fi ƙarfin abin da suke haɗa Shi da shi)) [Az-zumar:67].

Allah Yasa min albarka tare daku a cikin Alƙur'ani mai girma.

# HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gare Shi akan samun dacewa da kuma ni'imominSa, kuma ina shaida cewa babu abun bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya ina mai girmama al'amarinSa, kuma ina shaida cewa Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, tsira da amincin Allah masu tarin su tabbata a gare shi da iyalansa da sahabbansa.

**Ya ku Musulmi:**

Babu wanda yakai Allah son yabo; shi yasa ya yabi kanSa da kanSa, kuma ginshiƙin samun fifiko tsakanin mutane yana kasancewa ne da sanin Allah da ƙaunarSa, da yabo a gare Shi, kuma duk wanda yasan Allah alhali zuciyarsa tana lafiyayya; zai so Allah kuma zai girmamaShi, kuma duk lokacin da bawa ya ƙara sanin Allah zai ƙara yin biyayya a gare Shi.

kuma zunubbai suna raunana ganin girman Allah da matsayinSa, inda ace matsayin Allah da girmanSa zasu sami mazauni a zuciyar bawa, da ba wani ɗaya daga cin bayi da zaiyi ƙarfinhalin ya saɓa maSa, kuma duk wani saɓo yana daga cikin jahiltar Allah.

kuma girman Allah yana ƙaruwa dayi maSa biyayya, kuma mafi girman ibadar da bawa zai kusanci Allah da ita; itace kaɗaita Shi da bauta, ba'a roƙon kowa sai Shi, ba'a neman agajin kowa sai nasa, kuma ba'a juyar da kowace ibada sai zuwa gare Shi Shi kaɗai.

kuma duk wanda ya bautawa wani tareda Allah, lallai bai girmama Allah ba haƙiƙanin girmama Shi ba, kuma ya cutar da kansa ta hanyar afkawa cikin shirka, kuma duk wanda Allah ya shiryar dashi zuwa girmama Ubangiji da kaɗaita Shi da bauta; ya wajaba a gare shi ya kira waninsa zuwa Tauhidin Allah da girmama Shi.

Sannan kuma ku sani, Lallai Allah ya umurceku da yin salati da sallama ga AnnabinSa....

# GIRMAMA ALLAH[1]

Dukkan godiya sun tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa da gafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrukan kawunanmu da zunubban ayukkanmu, wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, kuma wanda ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai yake baShida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne,tsira da amincin Allah masu tarin yawa su tabbata a gare shi da iyalan gidansa baki ɗaya.

**Bayan haka:**

Ya yaku bayin Allah, kuji tsoron Allah haƙiƙanin tsoro, kuma kuyi riƙo da igiya mai ƙarfi acikin musulunci.

**Ya ku Musulmai:**

Matsayin kowane ilimi yana bayyana ne cikin abinda ake sani a cikinsa, kuma mafi ɗaukakar ilimi kuma mafi tsarkinsa shine; sanin Allah, kuma buƙatar sanin Allah da girmamaSa tana sama dukkan buƙatu, shine ginshiƙin duk wata buƙata ta dole.

kuma Allah ya hallici bayinSa abisa ƙaunarSa da saninSa, kuma an hallici zuciya ne akan haka:

﴿فِطۡرَتَ ٱللَّهِ ٱلَّتِي فَطَرَ ٱلنَّاسَ عَلَيۡهَاۚ لَا تَبۡدِيلَ لِخَلۡقِ ٱللَّهِۚ﴾

((Hallitar Allah wacce ya hallici bayinSa akai, kada ku musanya halittar Allah)) [Ar-ruum:30], kuma itace miƙaƙiyar hanyar da ake haihuwar kowane abin hallita akai, kuma shaiɗanun aljanu da mutane sunata ƙoƙari wajen juyarda asalin abinda aka hallici hallitu akansa, a cikin hadisin Al-ƙudusi Allah ya ce:

«**Na hallici bayina dukansu akan hanya miƙaƙiya, kuma shaiɗanu suka zo masu sai suka kawar dasu daga Addininsu**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma kowane musulmi abin umurta ne da ya kiyaye asalin halittarsa domin wacce ta karkace daga cikinsu ta dawo zuwa ga asalinta, kuma masu

---

(1) Wannan huɓubar anyita ne a Masallacin Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-, a ranar Juma'a, Ashirin da huɗu ga watan Jimada Al-ula, shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da talatin da bakwai bayan Hijra.

imani su ƙara yawan imani.

kuma Allah ya kafa ayoyinSa domin su zama dalilai akan kaɗaitarSa a cikin ayukkanSa da kuma bautarSa, da ruwan teku zasu koma tawada kuma azo da wasu tekunan daɗi akanta ana rubutun kalmomin Allah da ayoyinSa masu nuni zuwa gare Shi lallai bazasu ƙare ba.

Kuma an aiko Manzanni ne; don tabbatarda asalin fiɗira da cikata, kuma tauhidin kaɗaita Allah a cikin ayukkanSa yana daga cikin mafi girman abinda zuka zo dashi, kuma ginshiƙi ne daga cikin ginshiƙan imani, kuma ɗaya ne daga cikin nau'ukan tauhidi waɗanda Allah ya hallici bayinSa domin su, kuma dalili ne akan kaɗaitar Allah a cikin bauta maSa, kuma dashi ne Allah ya kaffa hujjar kaɗaitaShi cikin bauta, kuma yin shirka a cikinsa itace mafi girma da munin na'ukan shirka, kuma babu mai kuskurewa a cikin kaɗaita Allah da bauta sai wanda bai ba tauhidin ayukkan Allah haƙinsa ba.

kuma Allah Mai tsarki kammalalle ne a cikin zatinSa da siffofinSa da ayukkanSa, kuma daga cikin siffofin Allah mai girman sha'ani akwai: Kaɗaitarsa a cikin halitta; baShida abokin taraya a cikin wannan, kamar yadda baShida abokin tarayya a bautarSa, Allah Mai ɗaukaka ya ce:

﴿قُلْ أَغَيْرَ ٱللَّهِ أَبْغِى رَبًّا وَهُوَ رَبُّ كُلِّ شَىْءٍ﴾

((Kace shin wanin Allah zan nema matsayin Ubangiji, alhali kuma Shine Ubangijin komai)) [Al-an`aam:164].

kuma shi Allah Mai tsalki Ya kaɗaita da hallita, mulki, arzutawa, da kuma gudanar da al'amurra, shine mai halitta kuma ba wani mai halitta tare daShi, wanda ya ƙirƙiri sammai da ƙasa, yayi halitta kuma ya daidaita hallitar, kuma ya kyautata halittar komai, kuma Shine mai yawan hallita kuma masani, kuma kamar yadda ya fara hallita, haka nan zai sake dawowa da ita a ranar Al-ƙiyama kuma yin haka yafi sauƙi a gare Shi, kuma duk wanda ba Allah ba bai cancanta a bauta masa ba, kuma Allah ne ya cancanta a bauta maSa; domin Shine Mahalicci.

﴿أَفَمَن يَخْلُقُ كَمَن لَّا يَخْلُقُ ۗ أَفَلَا تَذَكَّرُونَ﴾

((Shin, wanda Yake yin halitta yana zama ɗaya da wanda ba ya yin halitta? Shin ba ku tunawa?)) [An-nahl:17].

kuma Shi Allah, shine Sarki kuma mulki naSa ne:

﴿ذَٰلِكُمُ ٱللَّهُ رَبُّكُمۡ لَهُ ٱلۡمُلۡكُۚ وَٱلَّذِينَ تَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦ مَا يَمۡلِكُونَ مِن قِطۡمِيرٍ﴾

((Wannan shine Ubangijinku, a gare Shi mulki yake, kuma ababen dakuke kira koma bayanSa basa mallakar koda fatar gurtsun dabino)) [Faaɗir:13].

kuma shine mamallakin halittarSa, abinda yake a cikin sammai da ƙasa naSa ne, kuma dukkan halittu masu ƙanƙantar da kai da tasbihi a gare Shi, kuma dukkansu suna sujada a gare Shi.

Shine shugaba jagora wanda bashida abokin tarayya, kuma kowa bawanSa ne:

﴿إِن كُلُّ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ إِلَّآ ءَاتِي ٱلرَّحۡمَٰنِ عَبۡدٗا﴾

((dukkan wanda yake a cikin sammai da ƙasa sai yazoma Allah Al-rahman a matsayin bawa)) [Maryam:93], Shi yakeda cikakken mulki dawwamamme, mamallakin duniya da ranar sakamako, kuma a ranar Lahira zai bayyana ya ce:

﴿لِّمَنِ ٱلۡمُلۡكُ ٱلۡيَوۡمَۖ﴾

((wanene yau keda mulki));

sai ya amsama kanSa da faɗinSa

﴿لِلَّهِ ٱلۡوَٰحِدِ ٱلۡقَهَّارِ﴾

((Na Allah ne Makaɗaici, Mai tilastawa)) [Gaafir:16].

Allah Mai tsarki Ya kaɗaita da gudanar da al'amurran halittunSa da mulkinSa, dukkan umurni yana hannunSa Shi kaɗai:

﴿أَلَا لَهُ ٱلۡخَلۡقُ وَٱلۡأَمۡرُۗ﴾

((ku saurara, a gare Shi ne hallita da umurni suke)) [Al-a`raaf:54],

yana umurni yana hanawa, yana halitta yana arzurtawa, yana bayarwa yana hanawa, yana saukarwa kuma yana ɗagewa, yana ɗaukakawa yana ƙasƙantarwa, kuma yana rayawa yana kashewa:

﴿يُكَوِّرُ ٱلَّيۡلَ عَلَى ٱلنَّهَارِ وَيُكَوِّرُ ٱلنَّهَارَ عَلَى ٱلَّيۡلِۖ وَسَخَّرَ ٱلشَّمۡسَ وَٱلۡقَمَرَۖ﴾

((yana shigar da dare a cikin rana kuma yana shigar da rana a cikin dare,

kuma ya hore rana da wata)) [Az-zumar:5],

﴿يُخۡرِجُ ٱلۡحَيَّ مِنَ ٱلۡمَيِّتِ وَيُخۡرِجُ ٱلۡمَيِّتَ مِنَ ٱلۡحَيِّ وَيُحۡيِ ٱلۡأَرۡضَ بَعۡدَ مَوۡتِهَاۚ﴾

((Yana fitarda rayayye daga matacce kuma yana fitarda matacce daga rayayye, kuma yana rayarda ƙasa bayan mutuwarta)) [Ar-ruum:19],

dukkan halittu suna ƙarƙashin buwayarSa da ganindamanSa, kuma zukatan bayi da makwarkwaɗan kansu suna a hannunSa, kuma gudanar al'amurra suna ƙulle ne da tsarawarSa da ƙaddarawarSa, yana kiyaye da duk abinda kowace rai ta aikata, kuma sama da ƙasa sun tsayu ne da umurninSa,

﴿وَيُمۡسِكُ ٱلسَّمَآءَ أَن تَقَعَ عَلَى ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا بِإِذۡنِهِۦٓۚ﴾

kuma ((yana riƙe da sama don kada ta faɗo akan ƙasa saida izininSa)) [Al-hajj:65].

Kuma

﴿يُمۡسِكُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ أَن تَزُولَاۚ﴾

((yana riƙe da sammai da ƙasa kada su gushe daga bagirensu)) [Faaɗir:41],

kuma duk wanɗanda ke a cikin sammai da ƙasa suna roƙonSa

﴿كُلَّ يَوۡمٍ هُوَ فِي شَأۡنٖ﴾

((kullum Allah yana cikin wani sha’ani)) [Ar-rahman:29],

kuma yana daga cikin sha'anoninSa: yana gafarta zunubi, yana shiryarda ɓatacce, yana yaye damuwa, yana ƙarfafar wanda zuciyarsa ta kare, yana arzurta matalauci, yana karɓa addu'a, Allah Mai ɗaukaka Ya ce:

﴿وَمَا كُنَّا عَنِ ٱلۡخَلۡقِ غَٰفِلِينَ﴾

((kuma bamu kasance masu shagala daga hallitu ba)) [Al-mu`minuun:17].

UmurninSa wani yana biye da wani, kuma abinda yaso yana gudana, ba wata ƙwayar zarra dazata motsa a cikin duniya sai da izininSa, abinda yaso shi yake kasancewa, abinda bai so ba baya kasancewa, yana halittar abinda yaso, yana yin abinda yake so, kuma al'amarinSa ƙaddara ce daya ƙaddara, ba mai badawa ga abinda ya hana, kuma ba mai hanawa ga abinda ya bada, ba mai cin gyara ga hukunciSa, kuma ba mai mayarda abinda ya ƙaddara, ba mai ture abinda yayi nufi, kuma ba mai canza

kalmominSa, ya ƙaddara komai na hallittu tun kafin ya hallicci sammai da ƙasa da shekara dubu hamsin, da dukkan halittu zasu haɗu akan samarda wani abun wanda Allah bai rubuta samuwarsa ba bazasu iya samar dashi ba, kuma da zasu haɗu akan su hana samuwar abinda Allah ƙaddara samuwarsa da bazasu iya ba, kuma da dukkan al'umma zasu haɗu akan cutarda wani bawa wanda Allah baiyi nufin cutar dashi ba, bazasu iya cutar dashi ba, kuma da zasu haɗu akan su amfanar dashi, bazasu iyawa ba idan Allah bai bada izinin hakan ba, yana shiryarda wanda yaso da falalarSa, kuma yana ɓatarda wanda yaso da adalcinSa, idan yayi nufin yin wani abu, zai ce mashi: kasance; sai ya kasance.

﴿لَا يُسْـَٔلُ عَمَّا يَفْعَلُ وَهُمْ يُسْـَٔلُونَ﴾

((Ba a tambayar Sa akan abin da Yake aikatawa, alhali kuwa su ana tambayar su)) [Al-anbiya`:23].

maganarSa itace mafi kyawon magana, kalmominSa basuda farko kuma basuda ƙarshe:

﴿وَلَوْ أَنَّمَا فِى ٱلْأَرْضِ مِن شَجَرَةٍ أَقْلَٰمٌ وَٱلْبَحْرُ يَمُدُّهُۥ مِنۢ بَعْدِهِۦ سَبْعَةُ أَبْحُرٍ مَّا نَفِدَتْ كَلِمَٰتُ ٱللَّهِ ۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٌ﴾

((Da za'a ce duk abinda yake a cikin ƙasa na bishiya Alƙalumma ne, kuma duk wani teku ya zama tawada da ƙarin wasu tekuna guda bakwai -ana rubuta- Kalmomin Allah, da ba zasu ƙare ba, lallai Allah Mabiwayi ne Mai cikan hikima)) [Luƙmaan:27],

kuma Ilimin Allah Maɗaukaki ya yalwaci komai, yasan abinda ya kasance, da wanda zai kasance da wanda ba zai taɓa kasancewa ba, kuma yasan abinda hallitu suka aikata da abinda zasu aikata, yasan abinda yake tudu da ruwa, ba wani ganye da zai faɗo a ƙasa face ya sanshi,

﴿لَا يَعْزُبُ عَنْهُ مِثْقَالُ ذَرَّةٍ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَلَا فِى ٱلْأَرْضِ﴾

((ba wani abu da yake ɓoye maSa koda kwatankwacin ƙwayar zarra a cikin sammai ko a cikin ƙasa)) [Saba`:3], yasan duk abinda yake ɓoye da wanda yake bayyane a garemu, yasan abin da zukata suke waswasi akai, da abinda ƙiraza suke kunshe da shi, kuma yasan abinda mace take ɗauke dashi a cikin ciki, kuma ba wanda yasan mabuɗan gaibi sai Shi, kuma dukkan ilimin bayi baki ɗaya kamar ɗigo ne daga cikin tekun iliminSa,

kuma shima ilimin nasu bai samu ba sai da yardarSa, wani kanari -tsuntsu-ya tsosti ruwa sau ɗaya daga cikin teku, sai Ƙhidir yace ma Musa -Aminci ya tabbata garesu su-:

«**Ilimina da naka bai rage komai ba daga ilimin Allah, sai kamar yadda wannan tsuntsun ya rage wani abu daga ruwan wannan kogin**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

jinSa ya yalwaci dukkan sautuka, basa rikice maSa kuma basa maSa kama da juna, wata mata ta kai kukan mijinta gun Annabi -tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi, kuma a lokacin Aishah -Allah Ya yarda da ita-tana a gefe a cikin ɗakin, amma wani sashin maganar matar yana ɓoyuwa gareta, amma Allah yaji maganarta tun daga saman sammai guda bakwai, kuma ya saukar da faɗinSa:

﴿قَدۡ سَمِعَ ٱللَّهُ قَوۡلَ ٱلَّتِي تُجَٰدِلُكَ فِي زَوۡجِهَا وَتَشۡتَكِيٓ إِلَى ٱللَّهِ وَٱللَّهُ يَسۡمَعُ تَحَاوُرَكُمَآۚ إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعُۢ بَصِيرٌ﴾

((Lallai Allah Ya ji maganar wacce ke yi maka jayayya game da mijinta, tana kai kuka ga Allah, kuma Allah yana jin tattaunawarku)) [Al-mujadalah:1].

kuma ganinSa ya kewaye dukkan abin gani, don haka ayukkan bayi dasuke yi a cikin duhun dare basu ɓoyuwa a gare Shi, kuma yana madakata gameda dukkan ayukkansu.

kuma saboda dukkan halittu halittarSa ne, don haka, hukunci naSa ne Shi kaɗai; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿إِنِ ٱلۡحُكۡمُ إِلَّا لِلَّهِۖ﴾

((Tabbas, lallai hukunci na Allah ne)) [Al-an`aam:51],

kuma hukunce-hukuncenSa, da iyakokinSa, da duk abinda ya shar'anta sune mafi kyawon hukunce-hukunce, kuma ba wanda yafi Shi kyawun hukunci

﴿وَهُوَ خَيۡرُ ٱلۡحَٰكِمِينَ﴾

((kuma Shine mafi alkhairin masu hukunci)) [Al-a`raaf:87],

yana hukunci kuma ba mai cin gyara ga hukuncinSa

﴿وَلَا يَظۡلِمُ رَبُّكَ أَحَدٗا﴾

((Kuma Ubangijinka baya zaluntar kowa)) [Al-kahf:49],

ba wanda yakaiShi rahama, shine mafi rahamar masu rahama kuma mafi

alkhairinsu, yafi tausayi sama da uwa ga ɗanta, rahamarSa ta yalwaci komai, Allah Mai tsarki yanada rahama ɗari; ya saukar da ɗaya wacce da itace halittu suke tausayawa junansu, ya rike casa'in da tara a wurinSa.

Allah mai karamci ne ba wanda yafiShi karamci, yana son kyautatwa da yin kyauta ga bayinSa, yana arzurtasu ta samansu da ƙasansu, falalarSa mai yawa ce, kuma taskokinSa basa ƙarewa.

﴿قُلۡ مَن يَرۡزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ﴾

((kace, wa yake arzurtaku daga sammai da ƙasa)) [Saba`:24],

kuma hannunSa a ciki yake, ciyarwa bata rage Shi, «Mai kyauta dare da rana»

Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Shin baku ganin abinda ya ciyar tun lokacinda ya hallici sammai da ƙasa? tabbas, ba abinda ya rage daga abinda yake a hannunSa**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi),

Yana karɓa roƙon bayinSa, Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَإِذَا سَأَلَكَ عِبَادِي عَنِّي فَإِنِّي قَرِيبٌۖ أُجِيبُ دَعۡوَةَ ٱلدَّاعِ إِذَا دَعَانِۖ﴾

((kuma idan bayinNa suka tambayeka game daNi, lallai Ni ina kusa, Ina karɓa kiran mai kira idan ya kiraye Ni)) [Al-baƙarah:186],

kuma ba wata buƙata datayima Allah girma wacce ba zai iya badawa ba, da dukkan bayi na farkonsu, dana ƙarshensu, mutanensu da aljanunsu zasu tsaya a cikin fili ɗaya, kowa ya roƙeShi buƙatarsa, kuma ya ba kowa abinda ya roƙa, hakan ba zai rage komai dake wurinSa ba sai kamar yadda allura take rage wani abu idan aka tsomata cikin teku.

kuma Allah Mai tsarki ya ɗauki nauyin arzikin duk hallitu -mutane da aljanu, musulmansu da kafiransu-

﴿وَمَا مِن دَآبَّةٖ فِي ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِ رِزۡقُهَا﴾

((Kuma ba wata dabba -hallita- a cikin ƙasa face arzikinta yana ga Allah)) [Huud:6].

kuma shine mafi alkhairin masu arzurtawa, ya buɗe ƙofofin alkhairi ga bayinSa, ya hore gulabe, ya gudanarda koguna, ya zuba arzuka, kuma ya bawa bayinSa ni'imomi masu tarin yawa waɗanda basu roƙeShi ba, kuma yabasu duk abinda suka roƙeShi, kuma cikin kowane dare yana bijirowa

bayi dasu roƙeShi, yana cewa:

«**Wa zai roƙe Ni in bashi?**»

«Bukhari da Muslim suka ruwaito shi».

duk wani alkhairi daga wurinSa yake:

﴿وَمَا بِكُم مِّن نِّعۡمَةٖ فَمِنَ ٱللَّهِۖ﴾

((kuma duk wata ni'ima dakuke da ita daga Allah take)) [An-nahl:53],

kuma ya sada kowace halitta da arzikinta, ya arzurta jinjiri a cikin mahaifiyarsa, da tururuwa a cikin raminta, da tsuntsaye a sararin samaniya, da kifaye a cikin ruwa:

﴿وَكَأَيِّن مِّن دَآبَّةٖ لَّا تَحۡمِلُ رِزۡقَهَا ٱللَّهُ يَرۡزُقُهَا وَإِيَّاكُمۡۚ﴾

((Kuma nawa-nawa ne daga cikin dabbobi waɗanda basu iya ɗaukar abincinsu, Allah ne Yake ciyar da su tare da ku)) [Al-ankabuut:60].

Makusanci ne Mai karɓawa, yana fushi da duk wanda baya roƙonSa, wanda yayi hasara shine wanda yake kwaɗayi daga wanin UbangijinSa, kuma ba wanda ya kai hakurin cutarwa da yakeji ana yi masa kamar Allah, suna haɗaShi da wani cikin bauta, suna raya cewa yanada ɗa, sannan kuma dukda haka ya basu lafiya kuma ya arzurta su.

cikin falalarSa da karamcinSa ya datarda ma'abota yi masa biyayya, kuma yabasu lada bayan datar dasu da yayi, Mai godewa ne, yana sakawa akan aiki ɗan kaɗan kuma ya biya aiki mai yawa, aiki na kwarai yana ruɓunyaShi a wurinSa har sau goma zuwa nunki mai yawa, kuma ya tanadama bayinSa a cikin Aljannah abinda ido bai taɓa gani ba, kuma kunne basu taɓa ji ba, kuma tunaninsu bai taɓa zuwa ɗarsuwa ba a zuciyar wani mutum ba, kuma ba zai gushe yana gamsar dasu ba, sai yace dasu:

«**shin kun gamsu? Sai suce: mi zai hana mu gamsu, alhali kuwa Ka bamu abinda baka taɓa bawa wani ba daga cikin bayinKa, sai yace: To zan baku abinda yafi haka falala, sai suce ya Ubangiji! mene ne yafi wannan falala? sai yace: Na saukar da yardata a garesku, ba zan taɓa fushi daku ba har abada**»

«Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

Allah Mawadaci ne da zatinSa, Mai biyan buƙata wanda hallittu suke ɗagawa buƙatocinsu, kuma shugaba ne mai cikar kamala wanda baShida ciki:

﴿لَمۡ يَلِدۡ وَلَمۡ يُولَدۡ ۝ وَلَمۡ يَكُن لَّهُۥ كُفُوًا أَحَدُۢ﴾

((Bai haifa ba, kuma ba a haife Shi ba
kuma babu wanda ya kasance tamka a gare Shi)) [Al-ikhlaas: 3-4],

﴿مَا ٱتَّخَذَ صَٰحِبَةً وَلَا وَلَدًا﴾

((bai riƙi mata ba ko ɗa)) [Al-jinn:3],

﴿وَلَمْ يَكُن لَّهُۥ شَرِيكٌ فِى ٱلْمُلْكِ وَلَمْ يَكُن لَّهُۥ وَلِىٌّ مِّنَ ٱلذُّلِّ﴾

((kuma bashida abokin tarayya a cikin mulkinSa, kuma bai riƙi wani masoyi ba -don ya ƙarfafa dashi- saboda ƙasƙanci)) [Al-isra`:111],

﴿وَمَا كَانَ مَعَهُۥ مِنْ إِلَٰهٍ﴾

((kuma wani abin bauta da gaskiya bai kasance tare daShi ba)) [Al-mu`minuun:91].

ba'a iya masa biyayya sai da izininSa, kuma ba'a iya saɓa maSa sai da saninSa, ya wadata daga hallitunSa, tsayayye ne da kanSa, kuma komai daShi ne ya tsayu kuma yanada buƙata zuwa gare Shi.

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ أَنتُمُ ٱلْفُقَرَآءُ إِلَى ٱللَّهِ وَٱللَّهُ هُوَ ٱلْغَنِىُّ ٱلْحَمِيدُ﴾

((Ya ku mutane! Kune mabuƙata zuwa ga Allah, kuma Shi Allah Mawadaci ne, Abin godewa)) [Faaɗir:15],

biyayyar masu biyayya bata amfanarSa, kuma saɓon masu saɓo baya cutar daShi, da mutane da aljanu zasu kasance akan zuciyar mafi taƙawar cikinsu, hakan bazai ƙara komai a cikin mulkinSa ba, kuma da zasu kasance akan zuciyar mafi fajirci cikinsu, hakan ba zai rage wani abu daga mulkinSa ba, bayi basa iya kaiwa matsayin amfanar da Shi balle su amfaneShi, kuma basa iya kaiwa matsayin cutar da Shi balle su cutar daShi.

Rayayye ne kuma tsayayye, gyan-gyaɗi baya kamaShi balle bacci, yana saukar da arziki kuma yana ɗauke shi:

«**Ana ɗaga masa aikin dare kafin aikin rana, kuma an ɗaga masa na rana kuma kafin na dare, haske ne shamakinSa, da zai yaye sa da hasken fuskarSa ya ƙone duk inda ganinSa ya kai**».

«**Mai girma ne Maɗaukaki, Mabuwayi Mai tsananin ƙarfi, buwaya ita ce gyautonSa, kuma jin girma da isa sune mayafinSa, Mai ƙarfi ne ba Mai iya rinjayarSa, kuma Maɗaukaki wanda baShida misali, komai zai halaka sai zatinSa**».

yana kewaye da komai, amma ba abinda ya kewaye da Shi:

﴿لَّا تُدۡرِكُهُ ٱلۡأَبۡصَٰرُ وَهُوَ يُدۡرِكُ ٱلۡأَبۡصَٰرَۖ﴾

((Gannai basa riskarSa, amma Shi yana riskar gannai)) [Al-an`aam:103],

﴿وَٱلۡأَرۡضُ جَمِيعٗا قَبۡضَتُهُۥ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَٱلسَّمَٰوَٰتُ مَطۡوِيَّٰتُۢ بِيَمِينِهِۦۚ سُبۡحَٰنَهُۥ وَتَعَٰلَىٰ عَمَّا يُشۡرِكُونَ﴾

((ƙasa baki dayanta damƙarSa ce a ranar ƙiyama kuma sammai suna naɗe a damarSa)) [Az-zumar:57],

ba'a neman daShi akan wani daga cikin hallitunSa, kuma ba mai iya ceto a wurinSa sai da izininSa, KursiyunSa -wurin aza ƙafafunSa- yafi sammai da ƙasa faɗi,

kuma «**girman kursiyu a cikin Al'arshi kamar wani zoben ƙarfe ne wanda aka jefa shi cikin wani falalar daji**».

kuma Al'arshi shine mafi girman hallittu, tsakanin fatar kunne da kafaɗar ɗaya daga cikin mala'ikun dake ɗauke dashi, ya kai tafiyar shekara ɗari bakwai.

kuma Allah ya daidaita akan Al'arshinSa -kamar yadda ya dace da girmanSa- kuma ya wadata daga Al'arshi da duk abinda yake ƙasa da Al'arshin:

﴿تَكَادُ ٱلسَّمَٰوَٰتُ يَتَفَطَّرۡنَ مِن فَوۡقِهِنَّۚ﴾

((Sammai sun kusa su tsatsage daga samansu)) [Ash-shuuraa:5].

Ma'ana: su kece; saboda ganin girman Allah, kuma idan Allah yayi magana da wahayi sai sama tayi girgiza mai tsanani saboda maganarSa, kuma mazauna sammai su faɗi sumammu kuma su faɗi suna masu sujada ga Allah.

Shine Na farko wanda babu kowa kafinSa, kuma Na ƙarshe wanda ba komai a bayanSa, kuma Shine Maɗaukaki wanda ba komai a samanSa, kuma Shine Ɓoyayye wanda ba abinda ya kai shi ɓoyuwa, Mai iko ne akan dukkan komai kuma Shine Mai karfi baki ɗaya, ba abinda ke gagararSa cikin ƙasa da sama, umurninSa kamar ƙyaftawar ido ne bal yafi hakan sauri, kuma yanada rundunoni babu wanda ya sansu sai Shi kaɗai, kuma idan duniya tazo ƙarshe, sai girgiza ƙasa girgizawa, ya niƙeta niƙewa, ya tafiyarda duwatsu tafiyarwa, kuma ya sheƙeta sheƙewa, kuma da busa ɗaya ne halittu zasu ɗimauce idan akayi na biyu duk zasu sume kuma idan akayi na ukku zasu tashi zuwa filin sakamako.

Shine tsarkakke, abin tsarkakewa daga dukkan wani aibu da tawaya, yanada kamala maɗaukakiya, da mafi girman cika da kyau, bashida kishiya kuma bashida misali, kuma baShi da takwara kuma ba mai kama daShi:

﴿لَيۡسَ كَمِثۡلِهِۦ شَيۡءٞۖ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡبَصِيرُ﴾

((Babu abinda yayi kama da Allah kuma Shine Mai ji kuma Mai gani)) [Ash-shuuraa:11].

**Bayan haka, ya ku Musulmai:**

Ashe bai wajaba a garemu ba mu so Ubangijinmu wanda waɗannan ne siffofinSa da ayuukkanSa, kuma mu gode maSa, muyi maSa yabo, kuma mu tsarkake ibada a gare Shi.

kuma duk wanda yasan Allah zai nemi kusanci zuwa gare Shi, ya ƙanƙantar da kai a gare Shi, ya ɗebe kewa daShi, kuma zai samu natsuwa, kuma zai yi kwaɗayin samun sakamakonSa, zai ji tsoron uƙubarSa, zai kai buƙatarSa a gare Shi, kuma zai dogara agare Shi.

kuma duk wanda yake yabon Allah, ya dage da yi masa kirari sossai zai samu ɗaukaka, ba wanda yakai Allah son yabo, saboda haka ne ya yabi kanSa da kanSa, kuma duk wanda yaso Allah ya bauta maSa, Allah zai so shi kuma zai yarda da shi kuma zai shigar dashi Aljannah.

Ina neman tsarin Allah daga shaidan jefaffe.

﴿وَإِنَّ ٱللَّهَ رَبِّي وَرَبُّكُمۡ فَٱعۡبُدُوهُۚ هَٰذَا صِرَٰطٞ مُّسۡتَقِيمٞ﴾

((Lallai Allah Shi ne Ubangijina, kuma Ubangijinku, sai ku bauta Masa. Wannan ce hanya madaidaiciya)) [Maryam:36].

Allah Yasa min albarka tare daku a cikin Alƙur'ani mai girma....

# HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gare Shi akan samun dacewa da kuma ni'imominSa, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya ina mai girmama al'amarinSa, kuma ina shaida cewa Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah yayi daɗin tsira da amincin Allah a gare shi da iyalansa da sahabbansa.

**Ya ku Musulmai:**

Duk wanda ya haɗa Allah da wani daga cikin hallitunSa; haƙiƙa ya yi tawaya ga Ubangijin talikai, kuma ya munana zato a gare Shi, kuma ya daidaita waninSa da Shi.

kuma ita Shirka tana rusa dukkan ayukka, kuma Allah baya yafema ma'abocinta, kuma baya shigar dashi Aljannah, kuma zai kasance cikin masu dawwama a wuta, kuma Shirka itace mafi girman canji daya samu asalin hallita, kuma itace mafi girman ɓarna a cikin ƙasa, kuma itace ginshiƙin kowane bala'i, kuma itace matattarar kowace cuta, illarta mai girma ce, kuma haɗarinta mai matuƙar muni ne.

kuma shu'umcin saɓo yanada girma, yana taruwa akan bawa har ya halakar dashi, kuma yana katangance bawa tsakaninsa da zuciyarsa, kuma gwargwadon ake raina zunubi ne zunubin yake ƙara girma a wurin Allah; don haka, kada ka dubi ƙarancin laifi, ka dubi girman wanda ka saɓama.

sannan ku sani cewa, lallai Allah ya umurceku da yin Salati da sallama ga AnnabinSa....

## BAWA YASAN UBANGIJINSA[1]

Dukkan godiya sun tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman agajinSa da gafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrukan kawunanmu da zunubban ayukkanmu, wanda Allah Ya shiryar babu mai ɓatar dashi, kuma wanda Ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa lallai Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, tsira da amincin Allah masu tarin yawa su tabbata a gare shi da iyalan gidansa da sahabbansa.

**Bayan haka:**

Ya ku bayin Allah, kuji tsoron Allah haƙiƙanin jin tsoro; lallai ni'ima tana cikin bin shiriya, kuma taɓewa tana cikin bin son zuciya.

**Ya ku Musulmai:**

Allah ya hallici hallita; don biyayya da ƙasƙantar da kaita su kasance a gare Shi, kuma cikar samun nasara tana a cikin sanin Allah da imani da Shi, kuma farkon abinda ya wajaba ga mutum shine ya san UbangijinSa, kuma shine farkon abinda za'a tambayi bawa akansa a cikin ƙabarinsa, Allah Ya samarda halittu daga rashi, kuma Ya cikasu daga ni'imominSa, kuma Ya ɗauki nauyin arzikinsu:

﴿وَمَا مِن دَآبَّةٍ فِي ٱلۡأَرۡضِ إِلَّا عَلَى ٱللَّهِ رِزۡقُهَا﴾

((kuma babu wata dabba a cikin ƙasa face arzikinta yana ga Allah)) [Huud:6].

Shi ya samarda talikai bayan sun kasance ba komai ba

﴿هَلۡ أَتَىٰ عَلَى ٱلۡإِنسَٰنِ حِينٞ مِّنَ ٱلدَّهۡرِ لَمۡ يَكُن شَيۡـٔٗا مَّذۡكُورًا﴾

«Lallai ne, wani lokaci na zamani yazo a kan mutum, bai kasance abin ambato ba» [Al-insaan:1].

Ubangiji ne wanda ya kaɗaita da halitta, arzurtawa da gudanar da al'amura:

﴿أَلَا لَهُ ٱلۡخَلۡقُ وَٱلۡأَمۡرُۗ تَبَارَكَ ٱللَّهُ رَبُّ ٱلۡعَٰلَمِينَ﴾

---

(1) Wannan huɗubar anyita ne a Masallacin Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- a ranar Juma'a, sha biyar ga watan Safar, shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da ashirin da shidda bayan Hijra.

((ku saurara! Shine da halitta dakuma umurni, tsarki ya tabbata ga Allah Ubangijin talikai)) [Al-a`raaf:54].

Shi ne wanda ya kaɗaita da kasancewarSa Shi kaɗai, Ya siffanta da girma da buwaya, kuma tafiyar da al'amura duka suna hannuSa, Shi ne Mai tsananin ƙarfi, mabuwayi wanda yake a saman bayinSa, baya yarda a juyarda ibada sai zuwa gare Shi:

﴿إِن تَكْفُرُوا۟ فَإِنَّ ٱللَّهَ غَنِىٌّ عَنكُمْ ۖ وَلَا يَرْضَىٰ لِعِبَادِهِ ٱلْكُفْرَ ۖ وَإِن تَشْكُرُوا۟ يَرْضَهُ لَكُمْ ۗ﴾

((Idan kuka kafirce, tabbas Allah mawadaci ne daga gareku, kuma baya yardarwa bayinSa yin kafurci, kuma idan kuka gode sai ya yarda da godiyar taku)) [Az-zumar:7].

a cikin kowace halitta ya kafa alamar dake nuni ga kaɗaituwarSa; domin zukata su ƙara alaƙantuwa daShi, akwai ayoyi guda biyu dake kai komo a cikin mu suna tuna mana kaɗaitar Allah; dare wanda yake lulluɓe komai, da yini wanda yake yaye komai, kowane ɗaya daga cikinsu yana bin ɗan uwansa da gaggawa:

﴿يُغْشِى ٱلَّيْلَ ٱلنَّهَارَ يَطْلُبُهُۥ حَثِيثًا﴾

((Dare yana rufe yini yana binsa da gaggawa)) [Al-a`raaf:54],

kuma rana da wata suna gudana a cikin wata hanya mai matuƙar tsari, wanda ya zarce tunanin masu hankali, wancan tana ɓullowa wannan yana juyawa, tafiya mai tsari, babu gaggawa ko jinkiri a ciki.

﴿لَا ٱلشَّمْسُ يَنۢبَغِى لَهَآ أَن تُدْرِكَ ٱلْقَمَرَ وَلَا ٱلَّيْلُ سَابِقُ ٱلنَّهَارِ ۚ وَكُلٌّ فِى فَلَكٍ يَسْبَحُونَ﴾

((Rana baza ta riski wata ba. Kuma dare ba zai riga wuni ba, kuma dukkansu a cikin sarari ɗaya suke yin iyo)) [Yaasin:40].

Ga ƙasa wadda take ɗauke damu, ga sama wadda ta mana inuwa, kuma bama iya wadatuwa daga ɗayansu, wannan wasu halittu ne da aka kyautata, waɗanda kuma gudanar dasu yake daga wanda ya kasance Ƙwararre ne a komai:

﴿هَٰذَا خَلْقُ ٱللَّهِ فَأَرُونِى مَاذَا خَلَقَ ٱلَّذِينَ مِن دُونِهِۦ ۚ﴾

((Wannan shi ne halittar Allah. To ku nuna mani, mene ne waɗanda ba shi ba suka halitta?)) [Luƙman:11],

kuma Musulmi yana alfahari da kasancewarsa bawan wanda ke gudanar

da wannan duniya mai girma:

﴿قُلۡ إِنَّنِي هَدَىٰنِي رَبِّيٓ إِلَىٰ صِرَٰطٖ مُّسۡتَقِيمٖ﴾

((kace tabbas, ni Ubangijina ya shirya dani zuwa ga hanya madai-daiciya)) [Al-an`aam:161],

baya bautawa kowa sai Ubangijin wannan duniyar Allah Mai girma da ɗaukaka, kuma baya juyar da wani abu na nau'in ibada zuwa ga waninSa, yana komawa zuwa gare Shi a lokacin manya musibu, kuma Shi kaɗai Yake tsoro a bayyane da ɓoye:

﴿وَإِن يَمۡسَسۡكَ ٱللَّهُ بِضُرّٖ فَلَا كَاشِفَ لَهُۥٓ إِلَّا هُوَۖ﴾

((kuma idan Allah ya shafeka da wata cuta babu mai iya yaye maka sai Shi)) [Al-an`aam:17].

baya tsoron wani matacce ya cutar dashi da wata cuta, ko yayi ƙaunar wata kyautatawa daga gare shi.

kuma komawa ga Allah Shi kaɗai shine cikar hankali, kuma shine aminci a zuciya, da natsuwar ruhi, kuma duk wanda yake jin tsoron UbangijinSa ba wanda zai bashi tsoro; zaka same shi mai ƙarfin zuciya mai natsuwar kaɓoɓi, kuma madalla da rayuwar da bata samun natsuwa sai tareda Allah:

﴿فَلَا تَخَافُوهُمۡ وَخَافُونِ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ﴾

((Kada ku ji tsoransu kuma ku ji tsorona in kun kasance muminai)) [Aali-Imran:175].

Abu Sulaiman Ad-daaraaniy -Allah yayi masa rahama- ya ce:

«Tsoron Allah ba zai bar zuciya ba face sai ta rushe».

Kuma mafi kusancin bawa ga Allah shine mafi jin tsoronSa, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce

«**lallai ni ne nafisu sanin Allah kuma nafi su tsananin tsoronSa**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi),

kuma tsoron Allah yana daga cikin lazimin imani da wajibcinsa, kuma duk wanda yaji tsoron UbangijinSa Shi kaɗai za'a buɗe masa ƙofofin Aljannoni; Allah Mai tsarki Ya ce

﴿وَلِمَنۡ خَافَ مَقَامَ رَبِّهِۦ جَنَّتَانِ﴾

((Kuma wanda ya ji tsoron tsayawa a gaban Ubangijinsa yana da Aljannah biyu)) [Ar-rahman:46],

Ma'abota ilimi sun ce:

«Allah baya haɗawa bawanSa tsoro guda biyu, duk wanda yaji tsoronSa a duniya zai amintar dashi a ranar ƙiyama, kuma wanda ya amintar dashi a duniya amma baiji tsoron UbangijinSa ba, to zai tsortar dashi a ranar ƙiyama»;

ka kiyaye UbangijinKa kuma kaji tsoron mahallicinka, zaka zamo mafi samun tsirar halittu a wurin Allah.

kuma kada kayi kwaɗayin samun wani abin dakake kwaɗayin samu ko samun amincin abin tsoro daga wanin Allah -kamar yaye wata cuta, ko warakar ciwo, ko neman arziki, ko samun lafiya-, ka tabbatar da ɗora kwaɗayinka ga Allah ba waninSa ba; domin hallitu an halicce su masu rauni, masu kasa jawowa kansu amfani ko tunkuɗewa kansu cuta, don haka sunfi rauni wurin yayewa waninsu, kuma babu wanda zai yi tsammanin amfani daga abokin halitta face sai ya samu taɓewa don haka, kada ka rataya kwaɗayinka da fatanka ga wanin Allah, domin bazaka girbi komai ba sai rashi da ƙasƙancin roƙo, ka ƙaunaci karamcin Allah da kyautarSa, da baiwarSa mai tarin yawa, domin kwaɗayin abinda yake hannun Allah ibada ce, kuma a cikin ƙasƙantarda zuciya ga Allah akwai samun izza da ɗaukakar matsayi da samun cimma buri.

Kuma samun natsuwar rai yana a cikin mayarda al'amarinta ga Mahaliccinta, kuma tana ƙara ratayewa ga maƙaginta idan ta tuna cewa Shi Ubangiji masani ne ga halinta, mai tausayawa ne ga al'amarinta, mai iko ne akan yaye cutarta, don me zata dogara ga abin halitta, kasashshe daga yaye cuta, mai rowa a cikin kyauta?! kuma Ubangijinka ya isar maka a cikindukkan lammuranka; shine majiɓicinka idan ka kai buƙatarka zuawa gare Shi kuma ka miƙa masa jagorancin al'amuranka

﴿وَمَن يَتَوَكَّلْ عَلَى ٱللَّهِ فَهُوَ حَسْبُهُۥٓ﴾

((kuma Wanda duk ya dogara ga Allah Shi kuma zai isar masa)) [Aɗ-ɗalaaƙ:3].

mai arziki; shine mai kwaɗayin rahamar Allah, mai tsoron azabarSa, mai tsoro da ƙanƙantar da kai a cikin ibadar Mai jiɓintar lamarinsa, kuma wannan shine hali mai girma wanda gidajen Annabta suka siffantu da shi; Allah Mai tsarki yace gameda Annabi Zakariyya da iyalan gidanSa:

﴿إِنَّهُمْ كَانُوا۟ يُسَٰرِعُونَ فِى ٱلْخَيْرَٰتِ وَيَدْعُونَنَا رَغَبًا وَرَهَبًا ۖ وَكَانُوا۟ لَنَا خَٰشِعِينَ﴾

((Lallai ne su sun kasance suna gaggawa zuwa ga ayukkan alkhairi Kuma suna kiranmu cikin kwadayi da fargaba. Kuma sun kasance masu tsoronmu)) [Al-anbiya`:90].

kuma Manzanni sun kasance masu gaggawa a cikin kwaɗayin abinda yake wurin Allah; Allah Mai tsarki yace ma AnnabinSa Muhammad -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi:

﴿وَإِلَىٰ رَبِّكَ فَٱرۡغَب﴾

((Kuma zuwa ga Ubangijinka ka yi kwaɗayi)) [Ash-sharh:8],

kuma tsoron Allah yana raguwa ga bawa gwargwadon zunubinsa, kuma yana ƙaruwa da ƙaruwar imaninsa,

Ibnul-Ƙayyim Allah yayi masa rahama ya ce:

«idan Allah yana nufin bawanSa da alkhairi, sai bashi dacewa da yin duk abinda yake iyawa, da bada ƙoƙarinsa a cikin kwaɗayin abinda yake wurin Allah da tsoronSa; domin waɗannan ababen guda biyu sune asalin samun dacewa, kuma gwargwadon yadda kwaɗayin abinda yake wurin Allah da tsoronSa zuciya take samun dacewa».

kuma tsoron abokin halitta ƙasƙanci ne da wulaƙanci, kuma duk wanda yake jin tsoron mahaliccinSa zai rayu maɗaukaki, kuma zai kasance mai jin daɗi a cikin rayuwarsa, kuma basirarsa zata zama mai haske kuma zai kasance mai wa'azantuwa, Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿سَيَذَّكَّرُ مَن يَخۡشَىٰ﴾

((Wanda yake tsoron (Allah) Zai wa'azantu)) [Al-a`laa:10].

kuma zai samu wa'azantuwa da ɗaukar darasi; Allah mai girma da ɗaukaka ya ce:

﴿إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَعِبۡرَةٗ لِّمَن يَخۡشَىٰٓ﴾

((Lallai ne, a cikin wannan haƙiƙa akwai abin kula ga wanda yake tsoron Allah)) [An-nazi`aat:26].

kuma littafin Allah zai kasance a gare shi abin samun kwanciyar hankali da tunatarwa:

﴿مَآ أَنزَلۡنَا عَلَيۡكَ ٱلۡقُرۡءَانَ لِتَشۡقَىٰٓ ۞ إِلَّا تَذۡكِرَةٗ لِّمَن يَخۡشَىٰ﴾

((Ba Mu saukar da Alƙur'ani a gare ka ba domin ka wahala.

Face domin tunatarwa ga wanda ke tsoron Allah)) [Ɗaaha:2-3].

kuma yana gadarda samun gafarar Allah da kyautarSa mai yawa:

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ يَخۡشَوۡنَ رَبَّهُم بِٱلۡغَيۡبِ لَهُم مَّغۡفِرَةٞ وَأَجۡرٞ كَبِيرٞ﴾

((Lallai waɗanda ke tsoron Ubangjinsu a ɓoye suna da wata gafara da wani sakamako mai girma)) [Al-mulk:12].

don haka ka sanya Ubangijinka a ganinka, kada ka amincewa ƙullinSa da saukar uƙubarSa, kuma kada kaji tsoron yankewar arziki, ko jinkirin samun waraka, ko saukar wani abu mai muni daga wanin Allah, Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿فَلَا تَخۡشَوۡهُمۡ وَٱخۡشَوۡنِي وَلِأُتِمَّ نِعۡمَتِي عَلَيۡكُمۡ وَلَعَلَّكُمۡ تَهۡتَدُونَ﴾

((kada kuji tsoronsu kuma kuji tsoroNa, kuma don in cika ni'imata akanku domin ku sami shiriya)) [Al-baƙarah:150].

kuma bawa mai rauni ne a karan kansa, yana buƙatar taimakon UbangijinSa mai ƙarfi, kuma da neman taimakon Allah Mai girma da ɗaukaka zaka samu wadatuwa daga neman taimakon hallittu, kuma duk wanda yake ƙoƙarin samun cika wani buri alhali bai nemi taimakon Allah ba, kuma bai kasance mai buƙatuwa a gare Shi ba cikin cika wannan burin; lallai za'a rufe masa hanyoyi, kuma ababen nema zasu yi masa wahala, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce ma Ɗan Abbas - Allah Ya yarda dasu-:

«**Ya Kai ƙaramin yaro, Zan Sanar da kai wasu Kalmomi, Ka kiyaye Allah sai Allah ya kiyaye ka, ka kiyaye Allah Sai ka same shi duk halin da kasamu kanka, kuma idan zakayi roƙo, to, ka roƙi Allah, kuma idan zaka nemi taimako to ka nemi taimakon Allah**».

(At-tirmizi ya ruwaito shi)

kuma cikin neman taimakon Allah ne Addini yake kai-komo:

﴿إِيَّاكَ نَعۡبُدُ وَإِيَّاكَ نَسۡتَعِينُ﴾

((Kai kaɗai muke bautaMa, kuma Kai kaɗai muke neman taimakonKa)) [Al-fatihah:4],

kuma da shi ne manzanni suka umurci mutanensu:

﴿قَالَ مُوسَىٰ لِقَوۡمِهِ ٱسۡتَعِينُواْ بِٱللَّهِ وَٱصۡبِرُوٓاْ﴾

«Musa yace ma mutanensa ku nemi taimakon Allah kuma kuyi haƙuri» [Al-a`raaf:128],

Shehin Musulunci -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«Addini shine: kada a bautawa kowa sai Allah, kuma kada a nemi taimakon kowa sai naShi».

kuma cikar samun wadatar bawa tana cikin dogaronsa ga UbangijinSa, kuma yana daga cikin falalar Allah ga gabiyinSa cewa, duk wanda ya dogara da Shi zai taimake shi, kuma arziki yana sawaƙa ne da yin biyayya da neman taimakon Allah, kuma yana ƙaruwa da dogaro da ƙanƙantar da kai, Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَمَن يَتَّقِ ٱللَّهَ يَجۡعَل لَّهُۥ مَخۡرَجٗا ۞ وَيَرۡزُقۡهُ مِنۡ حَيۡثُ لَا يَحۡتَسِبُۚ﴾

((kuma wanda yaji tsoron Allah zai bashi mafita

kuma zai arzurta shi ta inda baya tsammani)) [Aɗ-ɗalaaƙ:2-3],

kuma rayuwa cike take da musibu da ababen ƙi; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿لَقَدۡ خَلَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ فِي كَبَدٍ﴾

((Haƙiƙa, Mun halicci mutum cikin wahala)) [A-balad:4],

kuma kowane abin halitta yanada maƙiyansa daga cikin Mutane da Aljanu, kuma jogoransu shine Iblis -Allah ya tsine masa-; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿إِنَّ ٱلشَّيۡطَٰنَ لَكُمۡ عَدُوّٞ فَٱتَّخِذُوهُ عَدُوًّاۚ﴾

((Lallai, shaiɗan maƙiyinku ne don haka ku riƙe shi maƙiyi)) [Faaɗir:6],

kuma bawa baya wadatuwa daga neman kariya daga Allah, da kuma neman taimakonSa Shi kaɗai, da kuma neman tsarin Allah daga sharukka, kuma Ubangiji ya siffantu da tsananin ƙarfi da buwaya; ba cutar wani mutum da zata shafi duk wanda ya nemi kiyayewarSa, kuma cuta bazata samesa ba koda an samu sababin afkuwar cutarwar akansa, tsira da aminci su tabbata a gare shi ya ce:

«**Duk wanda ya sauka wani masauki sai yace: Ina neman tsari da cikakkun Kalmomin Allah daga Sharrin abinda ya halitta, babu abunda zai cutar da shi har sai ya bar wannan wurin**»

(Muslim ya ruwaito shi),

Al-Ƙurɗubi -Allah Ya masa rahama- ya ce:

«tunda naji wannan hadisin nake aiki dashi, kuma ba abinda ya cutar dani sai wani lokaci dana barshi, sai kunnama ta harbe ni a wani wuri mai suna Almahdiya cikin dare, sai nayi tunani a cikin raina sai na gane cewa lallai na manta ban nemi tsari da waɗancan kalmomin ba».

kuma abin halitta koda yaushe wata cuta tana iya samun shi, ba zai taɓa samun kwanciyar hankali a rayuwa ba sai da neman tsari daga Allah da neman kariyarSa, domin cuta da amfani duka suna hannun Allah, kuma duk wanda yayi ƙoƙarin riskar da wata cuta a gareka ba zai cimma burinsa ba idan Allah bai so afkuwar hakan ba; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**kuma ka sani da duk al'umma zata taru akan su cutar da kai da wani abu, bazasu iya cutar da kai ba sai da abinda Allah ya rubuta akanka**»

(At-tirmizi ya ruwaito shi),

kuma lallai Allah ya umurci AnnabinSa -tsira da amincin su tabbata a gare shi- da ya nemi tsari da wanda Ya halicci safiya daga sharrin dukkan hallitu, da kuma sharrin duhun dare da mai hassadda, kuma mai iko akan yaye wannan duhun daga duniya Mai ikon ɗaukema wanda ya nemi tsari da Shi duk abunda yake tsoro da fargaba, kuma mai neman tsarin Allah a cikin dukkan sha'ani yana cikin wani tsari mai ƙarfi daga masu sharrora da makirce-makirce.

kuma bamuda wani wanda zamu koma gare shi a lokacin tsanani sai Ubangijinmu, kuma bamuda wata mafaka daga gare Shi sai a wurinSa, kuma mai neman agajin Allah da kariyarSa yana cikin wani nau'i na addu'a ta musamman, kuma neman agaji daga Allah Mai girma a lokacin tsanani da makirce-makirce shine mafakar Annabawa da mutanen kirki. Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿إِذۡ تَسۡتَغِيثُونَ رَبَّكُمۡ فَٱسۡتَجَابَ لَكُمۡ أَنِّي مُمِدُّكُم بِأَلۡفٖ مِّنَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةِ مُرۡدِفِينَ﴾

((A lokacin da kuke neman agajin Ubangijinku, sai Ya karɓa muku cewa: Lallai ne Ni, Mai ƙarfafa ku ne da dubu daga mala'iku ajere)) [Al-anfaal:9].

Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿أَمَّن يُجِيبُ ٱلۡمُضۡطَرَّ إِذَا دَعَاهُ﴾

((waye yake karɓa kiran wanda yake cikin tsanani idan ya kira Shi))

[An-namli:62].

kuma duk wanda yake kiran matattu, haƙiƙa ba'a jin kiransa, kuma buƙatarsa bazata biya ba; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَٱلَّذِينَ تَدۡعُونَ مِن دُونِهِۦ مَا يَمۡلِكُونَ مِن قِطۡمِيرٍ ۝ إِن تَدۡعُوهُمۡ لَا يَسۡمَعُواْ دُعَآءَكُمۡ وَلَوۡ سَمِعُواْ مَا ٱسۡتَجَابُواْ لَكُمۡۖ﴾

((kuma waɗanda kuke kira koma bayanSa basa mallakar koda fatar gurtsun dabino idan kun kirasu basa jin kiranku, kuma koda sun ji basa iya karɓa maku)) [Faaɗir:13-14],

kuma idan musibu suka sauka akanka, kuma baƙin ciki yayi maka tsanani, ka nemi agajin Masanin gaibi:

﴿إِنَّمَآ أَمۡرُهُۥٓ إِذَآ أَرَادَ شَيۡـًٔا أَن يَقُولَ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ﴾

((Kaɗai UmurninSa idan Ya yi nufin wani abu sai Yace mashi: kasance sai ya kasance)) [Yaasin:82].

kuma kaɗaita Allah da ayukkan bauta tsafta ce a cikin Aƙida, kuma cin nasara ce wadda take lulluɓe jama'a, kuma natsuwa ce a cikin rayuka.

Ina neman tsarin Allah daga shaidan jefaffe.

﴿يَـٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ ٱعۡبُدُواْ رَبَّكُمُ ٱلَّذِي خَلَقَكُمۡ وَٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكُمۡ لَعَلَّكُمۡ تَتَّقُونَ ۝ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ ٱلۡأَرۡضَ فِرَٰشٗا وَٱلسَّمَآءَ بِنَآءٗ وَأَنزَلَ مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ فَأَخۡرَجَ بِهِۦ مِنَ ٱلثَّمَرَٰتِ رِزۡقٗا لَّكُمۡۖ فَلَا تَجۡعَلُواْ لِلَّهِ أَندَادٗا وَأَنتُمۡ تَعۡلَمُونَ﴾

((Ya ku mutane ku bautawa Ubangijinku wanda ya hallicce ku kuma ya hallici waɗanda suke gabaninku domin ku samu jin tsoronSa.Wanda Ya sanya muku ƙasa shimfiɗa, kuma sama rufi, kuma Ya saukar da ruwa daga sama, sa'an nan Ya fitar da abinci daga 'ya'yan itace arziki a gareku. Saboda haka kada ku sanya wa Allah wasu kishiyoyi, alhali kuwa kuna sane)) [Al-baƙarah:21-22].

Allah Yasa min albarka tareda ku a cikin Alƙur'ani mai girma...

# HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gare Shi akan samun dacewa da kuma ni'imominSa, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya ina mai girmama al'amarinSa, kuma ina shaida cewa Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, tsira da amincin Allah mai yawa su tabbata gare shi da iyalansa da sahabbansa.

**Bayan haka, ya ku musulmai:**

Ƙofofin samun cin nasara da alkhairi ana buɗe su ne da rataya zuciya ga Allah, kuma da tuba ne da neman gafara ake rufe ƙofofin sharri, kuma samun lafiyar zuciya yana cikin barin aikata saɓo, kuma ni'imomin duniya suna cikin komawar zuciya ga Allah da sonSa da tsoronSa da kwaɗayin falalarSa, tsoro yana nisantar da kai daga saɓon Allah, shi kuma kwaɗayi yana turaka ga yi maSa biyayya, kuma sonSa yana koraka zuwa gare Shi korawa, don haka, ka saka ayukkanka duka don Shi kaɗai, kuma ka sa ayukkan su kasance a cikakkiyar siffa fili da ɓoye, tareda yaƙini cewa lallai Allah yana sane da dukkan sirrora da niyyoyi, kuma Mai gani ne Masanin ababen dake ɓoye.

sannan ku sani cewa, lallai Allah ya umurceku da yin salati da sallama ga AnnabinSa....

# AƘIDAR MUSULMI[1]

Dukkan godiya sun tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa da gafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrukan kawunanmu da zunubban ayukkanmu, wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, kuma wanda ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, tsira da amincin Allah masu tarin yawa su tabbata a gare shi da iyalan gidansa da sahabbansa.

**Bayan haka:**

Yaku bayin Allah, kuji tsoron Allah matuƙar tsoro; duk wanda yaji tsoron Allah ya samu tsira, kuma cuta bata zata samu wanda ya gaskata Shi ba, kuma madalla da kwaɗayin wanda yake kwaɗayi a wurin Allah.

**Ya ku Musulmai:**

Tabbas, addinin musulunci yanada kamala matuƙar kamala, addini ne wanda ya ƙunshi duk abinda mutum yakeda buƙata, a cikinsa akwai ibadodi da mu'amaloli, da haɗɗoɗa, da horo waɗanda suke tsalkake ɗaya-ɗayan mutane da jama'a baki ɗaya, kuma suna kiyaye Jama'a daga afkawa a cikin ruɗu da rikici, a cikinsa akwai abinda yake katangance rayuka daga afkawa a cikin miyagun ayukka da aikata manyan laifuka, yana mutunta mutum daga faɗawa cikin ababe maƙasƙanta da halaye masu muni, ba wani jin daɗi ga kowane mutum a rayuwa sai da riƙo da addininsa, kuma aiki na ƙwarai yana ƙara girma da yawan lada ne ta sanadiyyar ƙarin imani da tsarkake ibada ga Allah, kuma aiki yana rushewa idan aka yi shirka.

kuma haƙiƙa a cikin Ƙuraishawa akwai wasu mutane waɗanda suka kasance suna yin ibada, aikin hajji, umara, sadaƙa da sada zumunci, kuma suna karrama baƙo, kuma sun ƙudurce cewa lallai Allah shine wanda ya kaɗaita da hilitta da gudanarda komai, kuma suna tsarkake bauta ga Allah a lokacin tsanani, sai dai sun riƙi wasu ƴan tsakiya tsakaninsu da Allah, suna roƙonsu suna yanka garesu, suna yin alwashi a garesu, suna neman agajinsu domin suyi masu ceto, saboda suna riya cewa waɗannan ƴan

(1) Wannnan huɗubar anyita ne a Masallacin Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-, a ranar Juma'a, goma sha huɗu ga watan Zhil-hijjah, shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da ashirin da ɗaya bayan Hijra.

tsakkiyar sunfi su kusanci ga Allah. sai Allah Ya aiko Annabi Muhammad don ya jadadda masu addinin mahaifinsu Annabi Ibrahim -tsira da aminci su tabbata a gare shi-, kuma ya sanar dasu cewa: lallai ibada tsantsar hakkin Allah ce, kuma ya sanar dasu cewa lallai waɗannan ayukka nasu na shirka sun rusa dukkan ayukkansu na ibada, sannan kuma ya yaƙesu domin addu'a, yanka, alwashi, neman agaji da sauran duk dangoga na ibada su kasance na Allah ne Shi kaɗai.

kuma ba'a nema daga wanin Allah: samun warakar mara lafiya, da gafarta zunubbai da abinda yayi kamada haka na ababen da ba mai iya yinsu sai Allah. kuma ba'a zuwa wurin ƙaburbura domin yin addu'a da sallah a wurinsu, abin sani shine, ƙaburbura gidajen mamata ne, ko dai su kasance ni'ima a garesu ko kuma wuta.

kuma yana daga cikin mafi girman saɓo neman ɗaukinsu -matattu-, kuma neman ɗauki wani halitta ga abinda bashida iko akansa kamar neman ɗaukin wanda ya nutse a cikin ruwa ne daga wanda ya nutse kamarsa, kuma ba wanda zai ɗora kwaɗayinsa gaba ɗaya kan wani halitta face sai tsammaninsa daga gare shi ya tozarta, ka koma zuwa ga Allah, Allah yana arzurtawa da sababi ko ba sababi, kuma yana arzutawa ta inda baka tsammani, kuma lallai Allah ya isa mai jiɓintar lamari kuma mai taimako.

kuma abunda yake kankare shirka shine Tauhidi, kuma ayukkan ƙwarai suna tafiyarda munana, kuma duk wanda yayi fatar biyan buƙatarsa daga wanin Allah, ya jiuyarda zuciyarsa daga dogaro ga mahallicinta, zai rayu cikin zato kuma yana neman abinda ba zai taɓa samuwa ne ba.

kuma neman tunkuɗe cuta daga wanin Allah kamar ruƙuya -wacce bata shari'a ba- da layu duk wannan dogaro ne ga wanin Allah, Annabi -tsita da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**lallai ruƙuya -ta shirka- da layu da sihirin ƙulla soyayya dukkansu shirka ne**»

(Ahmad ya ruwaito shi),

kuma ita laya abu ne sandararre bata hana wani abu cikin al'amarin Allah, bata karewa daga cututtuka, bata hana samuwar ababen ƙi, kuma bata sa cimma manufa, kuma duk wanda ya tarayata a wuyan yara ko mata ko waninsu, Allah zai jingina shi zuwa gareta kuma zai tozarta shi; ka dogara ga Allah kuma ka kai buƙatocinka gare Shi, ka nemi mafaka gare Shi, kuma ka mayarda lamurranka gare Shi za'a biya maka buƙatunka kuma zaka samu yalwar ƙirji

﴿وَمَن يَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِ فَهُوَ حَسۡبُهُۥٓۚ﴾

((kuma duk wanda ya dogara ga Allah, haƙiƙa ya isar masa)) [Aɗ-ɗaaƙ:3], kuma idan Allah ya isarwa bawanSa wanda ya dogara a gare Shi kuma kiyaye Shi; ba yanda maƙiya zasu yi dashi, kuma kada ka ɗauka dogaronka ga Allah kasawa ce, kuma kada ka saka kasawarka ita ce dogaronka ga Allah.

kuma zuwa wun masu sihiri da ƴan tsibbu da gasgata ƙarairayinsu, da tambayarsu ababen dasuke ɓoye da abinda zai faru, da neman raba soyayya ko ƙullata ko yarda da waɗannan ababen duka yana taɓa aƙida, kuma tawaya ne a cikin tawakkali, kuma rashin haƙuri ne da abinda aka rubutama bawa da kuma fushi da abinda aka ƙaddara, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**duk wanda yaje wurin boka ko mai tsibbu kuma ya gasgata abinda yake faɗa, tabbas ya kafircewa abinda aka saukarma Muhammad**»

(Ahmad ya ruwaito shi).

kuma kwaɗayin mai kwaɗayi baya jawo arzikin Allah, haka nan kuma ƙin mai ƙi baya tunkuɗe shi; Alhassan Al-basari -Allah Ya jiƙansa- yana cewa:

«Tunda na san cewa wanina baya iya cin arzikina, sai zuciyata ta samu natsuwa», kuma zuwa wurin 'yan surkulle baya gaggauta zuwan arziki kuma baya jinkirta ajali, Alƙurɗubi -Allah Ya jiƙansa- ya ce: «Wajibi ne akan wanda yakeda iko ya masu inkari mai tsanani -masu sihiri da masu surkulle-da kuma duk mai zuwa wurinsu».

ka kiyaye rantsuwarka koda kanada gaskiya saboda girmamawa ga Ubangijinka, kuma kada kayi rantsuwa saida wani suna daga cikin sunayen Allah ko siffa daga cikin siffofinSa, kada kayi rantsuwa da wanin Allah Mai tsarki; kamar rantsuwa da Ka'aba, Annabi, da amana, da waliyyi.

kuma ka sami yaƙini gameda ƙaddarar Allah da haliitarSa da gudanarwarSa ga komai, kuma kayi haƙuri da jarabawarSa da hukuncinSa, kuma ka miƙa wuya ga ala'amarinSa, duniya cike take da damuwa da baƙin ciki, an haliicceta akan wahala da firgici; ka kasance mai imani da ƙaddarori; domin imani da ƙaddara ginshiƙi ne daga cikin ginshiƙan Addini, kuma ba duk abinda ake burinsa ba ake samunsa ba, kuma da dagewa da addu'a da komawa ga Allah baki ɗaya ake samun buɗewar ƙofofi kuma ake cimma manufa.

kuma wajibi ne ga mumini tsoronsa da ƙwaɗayinsa suka kasance ɗaya, don bawa zai halaka ida ɗayansu ya rinjayi ɗaya daga cikinsu, duk wanda tsoronsa ya rinjaya zai afka a cikin yanke ƙauna daga rahamar Allah-kuma wanda kwaɗayinsa ya rinjaya zai afka a cikin wani yanki na jin amintuwa da makircin Allah, amma tsoro abin yabo shine wanda ya tareka daga faɗawa a cikin ababen da Allah ya haramta.

Kuma idan bakajin ɗanɗanon aiki ba a cikin zuciyarka, to, ka zargi zuciyarka; domin Shi Ubangiji Mai godiya ne, kuma a cikin duniya akwai wata Aljannah wanda bai shigeta ba, ba zai shiga ta lahira ba, kuma hasararre shine wanda aka shamakance zuciyarsa daga UbangijinSa, kuma ɗaurarre shine wanda yabi son zuciyarsa, kuma tsayarda sallah a cikin jam`i tareda musulmai acikin ɗakunan Allah yana kara imani, da haskaka fuska, kuma yana katangancewa daga ayukkan haram; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَأَقِمِ ٱلصَّلَوٰةَۖ إِنَّ ٱلصَّلَوٰةَ تَنۡهَىٰ عَنِ ٱلۡفَحۡشَآءِ وَٱلۡمُنكَرِۗ﴾

((kuma ka tsayarda sallah; tabbas, sallah tana hani daga munanan ayukka da abin ƙi)) [Al-ankabuut:45].

Kuma abinci da abinsha na halal, suna nuni zuwa ga lafiyar imani da kyawon hanyar nema, kuma sanadi ne na karɓar addu'a; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa:

«**Ya kai Sa'ad! ka tsarkake abincinka zaka kasance wanda ake karɓar addu'arsa**»,

kuma da nisantar hulɗa da riba, ko mu'amala da abinda aka haramta kake samun ɗaukaka, kuma ranka yake samun tsarkaka.

kuma ka saka hulɗarka da mutane akan ƙa'idar: So da ƙi don Allah, don duk wanda ya zaɓi yardar Allah akan fushin mutane, Allah zai wadatar dashi daga damuwar mutane.

kuma ka kiyayi yin zalunci; domin zalunci duffai ne abin ruɓunyawa a ranar ƙiyama, kuma addu'ar wanda aka zalunta karɓaɓɓiya ce abar biyawa buƙata, kuma kada ka ci haƙƙoƙan mutane, kada kayi masu ta'adi akan haƙƙoƙansu; zalunci baya fita daga kasancewarsa barin aiki na ƙwarai ko aikata laifi, Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَمَن يَظۡلِم مِّنكُمۡ نُذِقۡهُ عَذَابٗا كَبِيرٗا﴾

((kuma wanda yayi zalunci daga cikinku zamu ɗanɗana masa azaba

mai girma)) [Al-furƙaan:19].

Lallai mai hankali shine; wanda aibobansa suka shagaltar dashi daga na waninsa, kuma ya mayarda hankali wurin biyayyar ga UbangijinSa, kuma mai bin hanyar neman yardar Allah dole ya kasance yanada wata himma wacce zata motsar dashi kuma ta ɗaga shi, da ilimi wanda zai haskaka masa hanyar kuma ya shiryar dashi, don haka, ka nemi kusanci zuwa ga Allah kana mai tuna baiwar da yayi maka da kuma kana kallon aibin kanka, kuma ka kiyayi cin mutuncin muslumi ta hanyar giba da yi masu ƙage; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa:

«**lallai, zubarda jinainanku, da cin dukiyoyinku, da taɓa mutuncinku haramun ne a tsakaninku kamar yadda wannan wuni da wata da wannan garin naku sukeda alfarma**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

kuma kada hassada da son zuciya su jaka zuwa ga yin ƙazafi, domin hassada itace mafi munin ɗabi'a ce, kuma an ɗabi'anci mutun akan son tserewa sa'anninsa, kuma mai aiki da fushi gameda ƙaddara a abin zargi ne, haka wanda ya dage wajen aibanta wanda ake ma hassada abin zargi ne, saboda haka, ka ƙyamatan kanka wannan ɗabi'ar abar zargi, kayi maganinta da tsoron Allah, duk wanda yake jin tsoron Allah kuma yayi haƙuri haƙiƙa Allah zai amfanarda shi saboda jin tsoronSa, kuma kayi ƙawa da ɗabi'u maɗukaka, ka dawwama akan yin ibada; domin yawan ibada na tunkuɗe riya, kuma neman taimakon Allah yana hana girman kai, kuma yin umurni da aiki mai kyau da hani daga mugun aiki kuma yana tunkuɗe bala'i, kuma ka nisanci laifuka ƙanana da manya; domin suna raunana zuciya da jiki, kuma suna kawarda ni'imomi suna jawo uƙuba, kuma shaiɗan yana ƙawatama mutum mai saɓo, ya mantar dashi uƙuba, kuma ya dinga nuna masa yalwar rahamar Allah; saboda ya afka sa a cikin zunubi lokaci bayan lokaci, daga nan sai ƙoƙarinsa na kaiwa ga samun yardar Allah da samun gidan lahira -Aljannah- ya raunana, kuma haƙiƙa shaiɗan ya ɗanama mutum tarko kuma yana nemansa da duk wani sharri, saboda haka, kada kabi hanyarsa, kuma kada kaja baya daga yaƙarsa, kuma ka yawaita ayukkan ɗa'a, kuma yana daga cikin alamar karɓar aiki na ƙwarai, yin wani aikin na ƙwarai a bayansa.

Ina neman tsarin Allah daga shaidan jefaffe.

﴿وَأَنَّ هَٰذَا صِرَٰطِي مُسۡتَقِيمٗا فَٱتَّبِعُوهُۖ وَلَا تَتَّبِعُواْ ٱلسُّبُلَ فَتَفَرَّقَ بِكُمۡ عَن سَبِيلِهِۦۚ

﴿ذَٰلِكُمْ وَصَّىٰكُم بِهِۦ لَعَلَّكُمْ تَتَّقُونَ﴾

((Kuma lallai wannan ne tafarkiNa wanda yake madaidaici: Sai ku bi shi, kuma kada ku bi wasu hanyoyi, sai su rarrabaku daga hanyaTa. Wannan ne Allah Ya yi muku wasiyya da shi domin ku samu jin tsoronSa)) [Al-an`aam:153].

Allah Yasa min albarka tareda ku a cikin Alƙur'ani mai girma...

# HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gare Shi akan samun dacewa da kuma ni'imominSa, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya don girmamawa ga al'amarinSa, kuma ina shaida cewa Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, tsira da amincin Allah mai yawa ya tabbata a gare shi da iyalansa da sahabbansa.

**Bayan haka, ya ku musulmai:**

lallai, rayuwa tana tareda mutuwa, kuma bayan duniya akwai lahira, kuma akwai mai ƙididdiga ga komai da kiyaye komai, kuma duk wani aiki na ƙwarai yanada lada, kuma kowane laifi da tashi uƙubar, kuma komai yanada lokacinsa, kuma babu makawa harda makusancinka za'a rufeka a ƙabari alhali shi yana a raye, kuma za'a rufeka ne tareda shi alhali kai kana a mace, idan mai karamci ne zai girmama ka, idan kuma na banza ne zai munana maka, sannan kuma baza'a tada shi ba sai tare da kai, kuma kaima baza'a tashe ka ba sai tare dashi, kuma baza'a tambayeka akan komai ba sai akansa, don haka ka saka shi ya zama na ƙwarai; domin idan na ƙwarai ne zaka ɗebe kewa dashi, idan kuma na banza ne zaka riƙa razana da shi; wannan shine ikinka!

ka yawaita aiki na ƙwarai, ka tsayu akan addininka, kuma kayi haƙuri wurin ƙarfafa shi, ka nisanci ababen daya hana, kabi umurninsa, kuma kayi riƙo da asalin addininka, ka aikata ababen dayake lizimta maka, kuma kayi guzurin ilimi, imani da aiki mai kyau, ka ɗauki darasi daga ababen lura na zamani, kuma kayi nazari a cikin wa'azoza na Alƙ'urani; domin labarai ne na gaskiya, kuma ka lizimci ambaton Allah tsawon rayuwarka, don ba'a gama ambaton Allah kuma baya yankewa, kuma ka yawaita neman gafara akan kasawarka, kuma ka godewa Allah akan dacewa daya baka.

Sannan kuyi salati da sallama ga mafi alkhairin halittar Allah, Muhammada ɗan Abdullahi, haƙiƙa Ubangijinku ya umurce ku dayin salati da sallama ga Annabinsa....

# KYAUTATA ZATO GA ALLAH[1]

Dukkan godiya sun tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa da gafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrukan kawunanmu da zunubban ayukkanmu, wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, kuma wanda ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa lallai Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, tsira da amincin Allah masu yawa su tabbata a gare shi da iyalan gidansa da sahabbansa.

**Bayan haka:**

Ya ku bayin Allah, kuji tsoron Allah haƙiƙanin tsoro, kuma kuyi riƙo acikin musulunci da igiya mai ƙarfi.

**Ya ku Musulmai:**

Tauhidi haƙƙin Allah ne akan bayinSa, dashi ne Allah Ya aiko ManzaninSa, kuma ya saukar da littattafanSa, kuma haƙiƙanin Tauhidi shine: kaɗaita Allah da ibada, ibada kuwa suna ne wanda ya game dukkan abinda Allah yake so kuma ya yarda dashi -na maganganu da ayukka na fili dana ɓoye-, kuma zuciya tanada ibadarta wadda ta kaɗaita da ita, kuma ibadarta tafi girma kan ibadar gaɓɓai kuma tafi yawa da dawwama, kuma shigar ayukkan zuciya a cikin imani yafi cancanta kan shigar ayukkan gaɓɓai; don haka, imanin dayake a cikin zuciya na ilimi da matsayi shine asali abin nema, kuma ayukkan dasuke a bayyane suke ƙarsa cika shi kuma sune biye a bayansa, kuma ayukkan gaɓɓai basa zama na ƙwarai ba kuma karɓaɓɓu sai ta hanyar ayukkan zuciya; domin shine ruhin ibada da ginshiƙinta, kuma idan babu shi a cikin ayukkan zahiri zasu zama kamar jikin mamaci wanda babu rai a cikinsa, kuma idan zuciya ta gyaru dukkan gangar jiki zata gyaru baki ɗaya; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**ku saurara, lallai a cikin jiki akwai wata tsoka, idan ta gyaru dukkan jiki ya gyaru, idan kuma ta ɓace dukkan jiki ya ɓace, ku saurara, ita ce zuciya**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi)

---

(1) Anyi wannan huɗubar ce a Masallacin Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-, a ranar Juma'a, goma sha takwas ga watan Rabi'ul Al-aakhir shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da talatin da tara bayan Hijra.

kuma girman falalar bayi yana kasancewa ne gwargwadon abinda yake cikin zukatansu, kuma dashi ne ake fifita wasu ayukkan akan wasu, kuma zuciya itace wurin da Ubangiji yake dubi a bawansa; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Lallai, Allah baya dubi zuwa ga jikinku, ko zuwa ga siffarku, sai dai yana dubi zuwa ga zukatanku da ayukkanku**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma daga cikin manyan ayukkan zuciya akwai: kyautata zato ga Allah; domin yana daga cikin farillan musulunci kuma ɗaya ne daga cikin haƙoƙan tauhidi da wajibbansa, kuma dunƙulalliyar ma'anarsa itace: dukkan wani zato wanda ya dace da cikar kamalar zatin Allah Mai tsarki da sunayenSa da siffofinSa, kuma wani reshe ne daga cikin ilimin sanin Allah ta'ala, kuma ginshiƙinsa yana akan ilimin sanin yalwar rahamar Allah, da buwayarSa, da kyautatawarSa, da ikonSa, da iliminSa, da kyawun zaɓinSa. idan sanin wannan ya cika dole zai gadarma bawa kyautata zato ga UbangijinSa, kuma yana iya samuwa ta hanyar samun yaƙini daga wasu sunayen Allah da siffofinSa.

kuma duk wanda tasirin ma'anonin sunayen Allah da siffofinsa suka tabbata a zuciyarsa, zai kyautatama Allah zato gwargwadon abinda kowane suna da siffa ya cancanta dashi; domin kowace siffa daga cikin siffofinSa tanada wata ibada ta musamman data kaɗaita da ita da kuma kyautata zato na musamman datake dashi.

kuma cikar kamalar Allah Mai girma da buwaya, da ɗaukakarSa, da kyawonSa da yawan falalarSa akan halittarSa duk suna wajabatama bayi kyautata maSa zato.

﴿وَأَحۡسِنُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُحۡسِنِينَ﴾

((Kuma ku kyautata lallai Allah yana son masu kyautatawa)) [Al-baƙarah:195].

Sufyan Al-thauri -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«ku kyautatama Allah zato»,

kuma saboda girman matsayin kyautata zato ga Allah, saida Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ƙarfafa akansa kafin rasuwarsa;

Daga Jabir -Allah Ya yarda dashi- ya ce: «Naji Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- kafin mutuwarsa da kwana uku yana

cewa: **kada ɗayanku ya mutu face sai yana mai kyautata zato ga Allah Mai girma da ɗaukaka**»

(Muslim ya ruwaito Shi).

kuma Allah ya yabi bayinSa masu tsoronSa saboda kyautata zatonsu a gare Shi, kuma ya saka sawaƙe masu ibada dayayi wani yankin bushara a garesu tun a anan duniya kuma ya saka ibadar taimako a garesu; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَٱسْتَعِينُوا۟ بِٱلصَّبْرِ وَٱلصَّلَوٰةِ ۚ وَإِنَّهَا لَكَبِيرَةٌ إِلَّا عَلَى ٱلْخَٰشِعِينَ ۝ ٱلَّذِينَ يَظُنُّونَ أَنَّهُم مُّلَٰقُوا۟ رَبِّهِمْ وَأَنَّهُمْ إِلَيْهِ رَٰجِعُونَ﴾

((Kuma ku nemi taimako da yin haƙuri da sallah, domin lallai ita -sallah- abu ce mai girma -wahala- sai dai a kan masu tsoron Allah -ba tada wahala- Waɗanda suka tabbatar cewa lallai su masu haɗuwa da Ubangijinsu ne, kuma lallai zasu koma a gare Shi)) [Al-baƙarah:45-46].

Kuma haƙiƙa Manzanni -amincin Allah ya tabbata a garesu- sun samu matsayi maɗaukaki a cikin saninsu ga Allah, suka maida lamurransu a gare Shi saboda kyautata zatonsu a gare Shi, Annabi Ibrahim - aminci ya tabbata a gare shi- ya ajiye Hajara tareda ɗanta Ismael a wurin ɗakin Ka'aba alhali lokaci ne da babu kowa kuma ba ruwa a garin kuma Ibrahim ya juya yatafi sai Hajara tabi shi tacemashi: «**Ya Ibrahim! ina zakaje ne kabarmu a wannan kwarin wanda ba mutane kuma ba komai a cikinsa? ta mai-maita masa wannan maganar, amma kuma bai wai-wayota ba, sai tacemashi: Shin Allah ne ya umurce ka da hakan? ya ce: eh, sai tace: Tabbas ba zai tozarta mu ba**»

(Bukhari ya ruwaito shi),

sai kyautata zatonta ga Allah yayi kyawun ƙarshe, Allah ya ɓuɓɓugar da ruwa mai albarka, kuma aka raya ɗakin ka'aba, kuma ambatonta ya wanzu a bayanta, kuma Ismael ya zama Annabi, kuma daga zuriyarsa ne aka samu cikamakon Annabawa kuma jagoran Manzanni.

kuma Annabi Ya'aƙub - aminci ya tabbata a gare shi- ya rasa ƴaƴansa guda biyu amma kuma sai yayi haƙuri, ya mayarda al'amarinsa ga Allah, ya ce:

﴿إِنَّمَآ أَشْكُوا۟ بَثِّى وَحُزْنِىٓ إِلَى ٱللَّهِ﴾

((lallai, ni ina kai kukana da baƙin cikin na ne zuwa ga Allah)) [Yusuf:86].

kuma zuciyarsa ta kasance cike da kyautatama Allah zato, kuma ya tabbatar da cewa Shine mafi alkhairin masu kiyayewa, ya ce:

﴿عَسَى ٱللَّهُ أَن يَأْتِيَنِي بِهِمْ جَمِيعًاۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْعَلِيمُ ٱلْحَكِيمُ﴾

((ina -kyautata- zaton Allah zai maido mani dasu baki ɗaya, tabbas, Shi Mai ilimi ne kuma Mai hikima)) [Yusuf:83],

kuma Annabi Ya'aƙub - aminci ya tabbata a gare shi- ya umurci ƴaƴansa da hakan, ya ce:

﴿يَٰبَنِيَّ ٱذْهَبُوا۟ فَتَحَسَّسُوا۟ مِن يُوسُفَ وَأَخِيهِ وَلَا تَا۟يْـَٔسُوا۟ مِن رَّوْحِ ٱللَّهِۖ إِنَّهُۥ لَا يَا۟يْـَٔسُ مِن رَّوْحِ ٱللَّهِ إِلَّا ٱلْقَوْمُ ٱلْكَٰفِرُونَ﴾

((Yaku ƴaƴana! ku tafi ku nemo labarin Yusufa da ɗan uwansa, Kada ku yanke tsammani daga rahamar Allah. Lallai ne, babu Mai yanke tsammani daga rahamar Allah sai mutane kafirai)) [Yusuf:87].

Kuma Bani Israel sun haɗu da cutarwar da ya yafi ƙarfinsu juriyarsu, amma komai girman baƙin ciki, kyautata zato ga Allah baya gushewa, a wurinsa ake fatar samun yayewa da kuma mafita; sai Annabi Musa -aminci ya tabbata a gare shi- yacema mutanensa:

﴿قَالَ مُوسَىٰ لِقَوْمِهِ ٱسْتَعِينُوا۟ بِٱللَّهِ وَٱصْبِرُوٓا۟ۖ إِنَّ ٱلْأَرْضَ لِلَّهِ يُورِثُهَا مَن يَشَآءُ مِنْ عِبَادِهِۦۖ وَٱلْعَٰقِبَةُ لِلْمُتَّقِينَ﴾

((Musa ya cema mutanensa ku nemi taimakon Allah, kuma ku yi haƙuri; Lallai ƙasa ta Allah ce, Yana gadar da ita ga wanda Yake so daga bayinSa, kuma kyakykyawan ƙarshe yana kasancewa ne ga masu tsoronSa)) [Al-a`raaf:128].

kuma musiba ta tsananta ga Annabi musa -aminci ya tabbata a gare shi- da waɗanda suke tare dashi, ga teku a gabansu, kuma ga Fir'auna da rundunarsa a bayansu, a lokacin ne:

﴿فَلَمَّا تَرَٰٓءَا ٱلْجَمْعَانِ قَالَ أَصْحَٰبُ مُوسَىٰٓ إِنَّا لَمُدْرَكُونَ﴾

((Sahabban Musa suka ce, lallai za'a riske mu)) [Ash-shu`araa:61].

sai ya kasance amsar Annabin da Allah yayi magana dashi shaida ce akan girman dogaronsa ga Ubangijinsa, da kuma kyautata zato ga Ubangiji mai ƙaddarawa.

﴿قَالَ كَلَّآۖ إِنَّ مَعِيَ رَبِّي سَيَهۡدِينِ﴾

((Ya ce: Kayya! Lallai ne Ubangijina Yana tare da ni, zai nunar dani)) [Ash-shu`araa:62].

sai wahayi yazo da abinda ba'a tunaninsa:

﴿فَأَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰٓ أَنِ ٱضۡرِب بِّعَصَاكَ ٱلۡبَحۡرَۖ فَٱنفَلَقَ فَكَانَ كُلُّ فِرۡقٖ كَٱلطَّوۡدِ ٱلۡعَظِيمِ * وَأَزۡلَفۡنَا ثَمَّ ٱلۡأٓخَرِينَ * وَأَنجَيۡنَا مُوسَىٰ وَمَن مَّعَهُۥٓ أَجۡمَعِينَ * ثُمَّ أَغۡرَقۡنَا ٱلۡأٓخَرِينَ﴾

((Sai Muka yi wahayi zuwa ga Musa cewa ka bugi teku da sandarka, sai teku ta tsage, kowane tsagi ya kasance kamar dutse mai girma. Kuma Muka kusanto da waɗancan jama`an (mutanen Fir`auna) zuwa ga tekun. Kuma Muka tseratar da Musa da waɗanda suke tare da shi gaba ɗaya. Sa'an nan kuma Muka nutsar da waɗancan mutanen)) [Ash-shu`araa:63-66].

Kuma mafi girman bayi a cikin bautar kyautata zato ga Allah shine; Annabinmu Muhammad -tisra da amincin Allah su tabbata a gare shi-; mutanensa sun cutar dashi amma ya tsaya akan da'awarSa yana mai tabbas gameda alƙawalin Allah da kuma taimakonSa ga addininSa, Mala'ikan duwatsu yace mashi: «idan kana so, sai a kife su da manyan duwatsun nan guda biyu na makkah» sai Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**A'a, ina fatan Allah ya fitar daga cikin tsatsonsu waɗanda da zasu bautama Allah kuma basa haɗa Shi da kowa**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi), kuma Annabinmu -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- baya gushewa yana mai kyautata zato ga UbangijinSa a cikin yanayi na tsananin ƙunci da damuwa, an fitarda shi daga garin Makkah kuma akan hanyarsa ya laɓe a cikin kogo, kuma kafirai suka cimmasa suka zagayesa, amma kuma a wannan yanayin yake cema da abokinsa:

﴿لَا تَحۡزَنۡ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَنَاۖ﴾

((Kada kayi baƙin ciki, lallai Allah yana tare damu)) [At-taubah:40], Abubukar -Allah Ya yarda da shi- ya ce:

«**a lokacin da nike a cikin kogo, sai nace ma Annabi -tisra da amincin Allah su tabbata a gare shi-: Da ɗayansu zai duba ƙasan ƙafafunsa da zai ganmu, sai yace: Ya Abubakar! menene zatonka**

**gameda mutane biyu waɗanda Allah ne na ukunsu**».

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi)

kuma tareda abinda ya haɗu dashi na cuta da baƙin ciki da yaƙi daga kowace fuska, amma duk da haka ya kasance yanada tabbacin cewa; akwana a tashi, wannan addinin sai ya shiga ko'ina a duniya kuma ya kasance yana cewa:

«**Tabbas, wannan Addinin sai ya kai duk inda dare da yini suka kai, kuma ba wani gidan da aka gina da yunɓu -ƙasa- ko da fata face sai Allah ya shigar da wannan addinin a cikinsa, addinin zai shiga ya ya tabbatarda girman duk mai giman da ya karɓe shi kuma ya tabbatar da maƙasƙanci akan duk wanda kafurce**»

(Ahmad ya ruwaito shi).

kuma wani balaraben ƙauye ɗauke da takobi ya tsaya a gaban Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- da takobin a zare alhali yana bacci, sai Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya farka yaga takobin tana hanunsa a zare, sai balaraben ƙauyen yace: Wa zai kareka daga gareni? **Nace: Allah -akayi haka har sau uku**, sai takobin ta fadi daga hannaun balaraben ƙauyen, kuma Annabi bai masa wata uƙuba ba kuma mutumin ya zauna»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi)

A ruwayar Ahmad:

«**sai takobin ta faɗi daga hanunsa**».

kuma bayan Annabawa Sahhabai sune sukafi halittu tsananin yaƙini saboda kyautata zatonsu ga Allah, Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿ٱلَّذِينَ قَالَ لَهُمُ ٱلنَّاسُ إِنَّ ٱلنَّاسَ قَدْ جَمَعُوا۟ لَكُمْ فَٱخْشَوْهُمْ فَزَادَهُمْ إِيمَـٰنًا وَقَالُوا۟ حَسْبُنَا ٱللَّهُ وَنِعْمَ ٱلْوَكِيلُ﴾

((Waɗanda mutane suka ce masu: Lallai, mutane sun tara -rundunoni- saboda ku, don haka ku ji tsoronsu. Sai wannan magana ta ƙara masu imani, kuma suka ce: Allah ya isar mana,  kuma madalla da kasacewarSa wakili)) [Aali-Imran:173].

Ibn Ad-daginna yazo wurin Abubakar -Allah Ya yarda dashi- ya nemeshi da cewa ya ɓoye karatunsa a cikin sallarsa ko kuma ya janye masa mafaka da kariyar da yake bashi, kuma zai ƙyaleshi da kafiran Ƙuraishawa su cutar dashi, sai Abubakar -Allah Ya yarda dashi- ya ce:

«Na mayar maka da mafakarka dakake bani, kuma na yarda da mafakar Allah Mai girma da ɗaukaka»

(Bukhari ya ruwaito shi),

kuma Umar -Allah Ya yarda dashi- ya ce:

«Wata rana Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya umurce mu da yin sadaka, sai akaci sa'a umurnin yazo ne lokacin danike da wata dukiya a wurina, sai nace: idan akwai ranarda zan wuce Abubakar yau ne zan wuce sa, yace: Sai na kawo rabin dukiyata, sai Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi yace mani: **me ka barowa iyalanka**? Sai nace: kamar wannan -dukiyar-, sai Abubakar ya kawoma Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi da dukiyarsa baki ɗaya, sai Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yace mashi: **Me ka baroma iyalanka?** sai yace: Na baro masu Allah da ManzonSa»

(Abu Dawud ya ruwaito shi).

kuma Khadijah wadda ita ce shugabar matan hallittu, a farkon fara saukar wahayi, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yazo mata yacemata «**Haƙiƙa ina jima kaina tsoro, sai khadija tace masa**: A'a, kayi bushara, na rantse da Allah, Allah ba zai tozartaka ba har abada, wallahi kai kana sada zumunta, kana gaskiya a magana, kana ɗaukar nauyin wanda bashi ƙarfi, kana ba wanda bashida komai, kuma kana ciyarda -karrama- baƙi, kana taimako akan matsaloli na gaskiya»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

kuma akan wannan tafarkin ne magabatan Al'umma suka tafi akai, Sufyan -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«ba zan so ace hisabina, -sakamakon ayukkana na kwarai da munana- ya kasance a hannun iyayena ba, Ubangijina yafi alkhairi sama da mahaifana»,

kuma yana daga cikin Addu'ar Sa'eed ɗan Jubair -Allah Ya jiƙansa-:

«Ya Allah ina roƙonka dogaro na gaskiya a gareka da kyautata zato a gareka».

kuma daga cikin aljanu akwai na ƙwarai, zatonsu ga Allah mai kyau ne, sunada yaƙini da ƙarfin Allah da faɗin iliminSa; daga cikin abinda suke faɗi:

﴿وَأَنَّا ظَنَنَّآ أَن لَّن نُّعۡجِزَ ٱللَّهَ فِي ٱلۡأَرۡضِ وَلَن نُّعۡجِزَهُۥ هَرَبٗا﴾

((Kuma lallai ne mu mun tabbata ba za mu gagari Allah ba, a cikin ƙasa, kuma ba za mu gagare Shi mu tsere maSa ba)) [Al-jinn:12].

Kuma daga cikin bayin Allah akwai wanda idan zai yi rantsuwa akan

wani abu, lallai Allah zai barrantar dashi, ba yana haka ne ba don shish-shigi ga Allah ba, sai don kyautata zatonsa a gare Shi-, kuma halin mumini shine; kyautata zato ga UbangijinSa cikin kowane lokaci da hali, kuma mafi cantantar lokacinda yafi dacewa ya kasance akan hakan shine lokacinda yake roƙonSa kuma ya kaɗaita da Shi yana mai yaƙinin kusancinSa da kasancewarSa wanda yake karɓa roƙon wanda ya roƙe Shi, kuma baya kunyatarda wanda ya ƙaunaceSa.

kuma yana daga cikin sabubban karɓar tuba: Kyautata zaton ma'abocinta ga UbangijinSa, a cikin abinda Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yake ruwaitowa daga UbangijinSa, ya ce:

«**Bawana yayi wani laifi; kuma yasan cewa yanada Ubangiji wanda yake gafarata laifi kuma yana kama mai laifi - yayi masa azaba- saboda laifi, ka aikata duk abinda kake so; don tabbas na yafe maka**»

«Bukhari da Muslim suka ruwaito shi».

kuma a lokacin tsanani da jarabawa, zato na ƙwarai ga Allah yake tasiri kuma mugun zato gare Shi yake bayyana, a lokacin yaƙin Uhud muminai suka samu tabbata, amma waninsu suna yiwa Allah mummunan zato irin zaton jahiliyya, kuma a lokacin yaƙin Ahzaab zato ga Allah ya kasu kashi-kashi; Allah yace gameda wata tawaga:

﴿هُنَالِكَ ٱبۡتُلِيَ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ وَزُلۡزِلُواْ زِلۡزَالٗا شَدِيدٗا ۝ وَإِذۡ يَقُولُ ٱلۡمُنَٰفِقُونَ وَٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٞ مَّا وَعَدَنَا ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥٓ إِلَّا غُرُورٗا﴾

((A wannan lokaci aka jarrabi muminai, kuma aka girgiza su, girgiza mai tsanani. Kuma a lokacin da munafukai da waɗanda akwai cuta cikin zukatansu ke cewa, Allah da ManzonSa, Ba su yi mana alƙawarin komai ba, face ruɗi)) [Al-ahzaab:11-12],

Amma sahabbai -Allah Ya yarda dasu- sai suka sami yaƙini cewa, zuwan jarabawa wani gwaji ne daga Allah wanda cin nasara da buɗi ke zuwa a bayansu, Allah Mai tsarki Ya ce gameda su:

﴿وَلَمَّا رَءَا ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ٱلۡأَحۡزَابَ قَالُواْ هَٰذَا مَا وَعَدَنَا ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ وَصَدَقَ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥۚ وَمَا زَادَهُمۡ إِلَّآ إِيمَٰنٗا وَتَسۡلِيمٗا﴾

((Kuma a lokacin da muminai suka ga rundunonin kafirai, sai suka ce, wannan ne abin da Allah da ManzonSa suka yi mana alƙawari, Allah da

ManzonSa sunyi gaskiya, kuma wannan bai ƙara masu komai ba face imani da miƙa wuya)) [Al-ahzaab:22].

kuma kyautata zato ga Allah shine mafita a lokacin ƙunci, baƙin ciki, da damuwa; mutanen nan guda uku da aka ƙaurace masu saboda ƙin fitarsu yaƙi basu samu yayewar abinda suke ciki ba saida kyautata zatonsu ga Allah, Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَعَلَى ٱلثَّلَٰثَةِ ٱلَّذِينَ خُلِّفُواْ حَتَّىٰٓ إِذَا ضَاقَتۡ عَلَيۡهِمُ ٱلۡأَرۡضُ بِمَا رَحُبَتۡ وَضَاقَتۡ عَلَيۡهِمۡ أَنفُسُهُمۡ وَظَنُّوٓاْ أَن لَّا مَلۡجَأَ مِنَ ٱللَّهِ إِلَّآ إِلَيۡهِ ثُمَّ تَابَ عَلَيۡهِمۡ لِيَتُوبُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ هُوَ ٱلتَّوَّابُ ٱلرَّحِيمُ﴾

((Kuma -Allah- Ya karɓi tubar mutanen nan guda uku waɗanda aka jinkirtar har ƙasa da yalwarta ta yi ƙunci a garesu, kuma rayukansu suka yi ƙunci a garesu, kuma suka tabbatarda cewa babu wata mafaka daga Allah face -komawa- zuwa gare Shi. Sa'an nan Allah Ya karɓi tubarsu, domin su tuba. Lallai Allah Mai karɓar tuba ne, Mai jin ƙai)) [At-taubah:118],.

Kuma Allah Mai ƙarfi ne mai iko akan komai, kuma ba'a iya fin ƙarfin Sa wajen taimakonSa ga bayinSa da masoyanSa, kuma samun tabbaci na taimakonsa yana daga cikin yaƙini, Allah Mai ɗaukaka ya ce:

﴿إِن يَنصُرۡكُمُ ٱللَّهُ فَلَا غَالِبَ لَكُمۡۖ وَإِن يَخۡذُلۡكُمۡ فَمَن ذَا ٱلَّذِي يَنصُرُكُم مِّنۢ بَعۡدِهِۦۗ﴾

((Idan Allah Ya taimake ku, to, babu mai iya rinjayar ku. Kuma idan Ya ƙyale ku, to, wane ne wanda zai iya taimakon ku koma bayanSa?)) [Aali-Imran:160].

Kuma Allah Shine; Mai rahama, duk Wanda yayi imani daShi kuma yayi aiki na ƙwarai, yayi kwaɗayin samun rahamarSa, zai samu hakan, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce:

«**Bayan Allah ya ƙaddara hallita: Sai ya rubuta a cikin littafinSa wanda yake wurinSa can saman Al-arshi ce wa: lallai rahamata tana riga fushi na**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi)

kuma duk wanda rayuwa tayi masa ƙunci, lallai, kyawun zatonsa yalwa ce da mafita, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbatta a gare shi- ya ce:

«**Duk wanda wata buƙata ta same shi, sai ya nemi biyan buƙatarta daga wurin mutane; baza'a yaye masa ita ba, kuma duk wanda ta same shi, ya nemeta daga Allah; bada jimawa ba Allah zai bashi wani arziki na kusa ko nesa**».

(At-tirmizi ya ruwaito shi),

Az-zubair ɗan Al-awwam yacema ɗansa: Abdullahi -Allah ya ƙara masu yarda-:

«Ya kai ɗana! idan ka kasa biyan bashi, ka nemi taimakon Majiɓincin al'amari na, Abdullahi ya ce: Wallahi ban gane mi yake nufi ba har saida nace, ya babana! waye majiɓicin lamarinka? sai yace: Allah ne, kuma yace: na rantse da Allah, ba wata damuwa dazan faɗa a cikinta ta bashinsa, face sai nace: Ya Majibicin lamarin Zubair! Ka biya masa bashinsa; kuma sai Ya biya masa»

(Bukhari ya ruwaito shi).

kuma Shi Allah Mai tsarki Mai yalwar gafara ne da kyauta, duk wanda ya kyautata zato ga wadatarSa, da karamcinSa, da gafararSa zai bashi abinda yake roƙonSa, Allah Mai tsarki yana saukowa zuwa saman duniya a ɗaya bisa uku na ƙarshen kowane dare, sai yace:

«**waye zai kirani in karɓa maSa? waye zai roƙeNi in bashi? waye zai nemi gafaraTa in gafarta masa**?»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi),

kuma hannayenSa masu tsarki a ciki suke

«**ciyarwa bata rage shi, Shine Mai kyauta dare da rana**».

kuma Allah mai karɓar tuba ne, yana murna da tubar bayinSa, yana shinfiɗa hannunSa cikin dare saboda masu laifi da rana su tuba, kuma yana shinfiɗa hannunSa da rana saboda masu laifi cikin dare su tuba, kuma yana daga cikin kamalar siffofinSa, baya mayarda wanda ya koma zuwa gare Shi, kuma mafi girman lokacinda bawa yake buƙatar kyautata zato ga Allah shine lokacinda mutuwa ta kusanto shi, yake bankwana da duniya kuma yake fuskantar komawa zuwa ga UbangijinSa, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**kada wani ɗaya daga cikinku ya mutu face yana mai kyautata zato ga Allah Mai girma da daukaka**»

«Muslim ya ruwato shi).

kuma a cikin wannan ibadar akwai bin umurnin Allah, da tsayarda ibadarSa, kuma bawa yana samun abinda yayiwa UbangijinSa zato dashi, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Allah Maɗaukaki yana cewa: Ina inda bawana yake maNi zato, kuma Ina tareda shi yayinda yake ambato Na**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi),

Dan Mas'ud -Allah Ya yarda dashi- ya ce:

«bawa ba zai kyautatama Allah zato ba; face sai Allah ya bashi abinda yake zato; domin dukkan alkhairi yana a hannun Allah Mai tsarki».

kuma idan akayima bawa arzikin kyautatama Allah zato; lallai, Allah ya buɗe masa babbar kofar alkhairi a cikin addini, Ɗan Mas'ud -Allah Ya yarda dashi- ya ce:

«Na rantse da wanda babu abin bauta da gaskiya sai Shi, ba'a ba mumini wani abu ba wanda yafi alkhairi sama da kyautata zato ga Allah».

kuma ayukkan bayi suna kasancewa ne gwargwadon kyawun zatonsu ga Ubangijinsu, mumini ya kyautatama Allah zato ne; shi yasa ya kyautata ayukkansa, amma kafiri ya munanama Allah zato ne, shi yasa yake munanan ayukka, a cikin wannan ibada -kyautata zato ga Allah- akwai bayyanar kyawon musulunci da cikar imani, kuma hanyar Aljannah ce ga ma'abocinta, ibada ce ta zuciya wacce take gadar da dogaro ga Allah da yaƙini da Shi, Ibnul-Ƙayyim -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«Tawakkalinka ga Allah yana kasancewa ne gwargwadon kyawon zatonka ga Ubangijinka da kwaɗayinka a gare Shi, shi yasa wasu suka fassara ma'anar dogaro ga Allah da kyautata maSa zato, amma haƙiƙanin lamarin shine; shi kyautata zato ga Ubangiji yana kai bawa zuwa ga dogaro gare Shi; domin ba'a tuninin samun yin dogaro ga wanda kakeda mummunan zato dashi, kuma tunanin wani zai dogara ga wanda baya ƙaunar biyan buƙata daga gare shi».

kuma daga cikin tasirin wannan ibadar: samun natsuwar zuciya, da komawa ga Allah da tuba zuwa gare Shi, kuma bayan imani ba awani abinda yake kawo yalwar ƙirji da faɗaɗarsa kamar samun yaƙini da Allah da ƙaunar alkhairi daga gare Shi, a cikinsa akwai abinda yake saka ma'abotansa yin kyaky-kyawar fata, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**cuta bata tashi da kanta zuwa ga wani, kuma canfi bashida tasiri kuma kykyawar fata tana burgeni**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi),

Al-halimi -Allah Ya jiƙansa- ya ce

«Shu'umci munana zato ne ga Allah, kuma kyakyawar fata: kyutata zato ne ga Allah).

kuma -kyautata zato ga Allah- yana taimakon ma'abocinsa akan yin karimci da jarumtaka, kuma ya gadar masa da samun ƙarfi, Abu Abdullahi Al-saaji -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«duk wanda yasamu yaƙini da Allah; haƙiƙa ya kiyaye ƙarfinsa, kuma

shine mafi alkhairin guzuri, kuma madalla da wannan tanadi».

ance da Salamata ɗan Dinar -Allah Ya jiƙansa-: «Ya baban Hazim! Menene da ka mallaka? Yace: natsuwa da Allah, da kuma yanke ƙauna daga abinda yake hannun mutane»

kuma duk wanda ya kayutata zato ga UbangijinSa, zai kasance mai kyauta, da bada dukiyarsa yana mai yaƙini da faɗin Allah:

﴿وَمَآ أَنفَقۡتُم مِّن شَيۡءٖ فَهُوَ يُخۡلِفُهُۥۖ﴾

((Kuma duk abinda kuka ciyar na wani abu, Allah zai maye maku da waninsa)) [Saba`:39].

Sulaiman Al-daraani -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«wanda ya dogara ga Allah wurin samun arziki zai kara masa halaye masu kyau, kuma Zai sanya masa haƙuri, kuma zai zama kasance mai yalwatawa idan zai ciyar, kuma zai samu ƙarancin waswasi a cikin sallah».

kuma kyautata zato ga Allah yana kai bawa zuwa ga ƙaunar abinda yake wurin Allah, da samun yaƙini gameda alƙawarinSa da yin aikin alkhairi saboda kwaɗayin falalar Allah kamar yadda yazo a cikin faɗarSa:

﴿وَمَا يَفۡعَلُواْ مِنۡ خَيۡرٖ فَلَن يُكۡفَرُوهُۗ﴾

((kuma abinda suka aikata na alkhairi baza'a yi masu butulci akai ba))[Aali-Imran:115].

Kuma Allah yana mu'amalantar bayinSa gwargwadon zatonsu gare Shi, kuma sakamako yana kasancewa ne daga jinsin aiki; don haka, duk wanda yayi zaton alkhairi zai samu alkhairi, kuma wanda yayi zaton wanin haka lallai yayi hasara, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Allah Mai girma da ɗaukaka ya ce: Ni ina nan duk inda bawa na yake zatona; don haka bawa ya yi min zaton daya ga dama, idan ya zaci alkhairi zai same sa, idan kuma ya zaci sharri zai same sa**»

(Ahmad ya ruwaito shi),

kuma idan bawa ya kasance mai kyautata zato ne ga Allah; lallai Allah baya tozarta shi har abada, kuma a ranar ƙiyama, wanda ya kyautata zatonsa ga Allah zai ce:

﴿فَأَمَّا مَنۡ أُوتِيَ كِتَٰبَهُۥ بِيَمِينِهِۦ فَيَقُولُ هَآؤُمُ ٱقۡرَءُواْ كِتَٰبِيَهۡ ۞ إِنِّي ظَنَنتُ أَنِّي مُلَٰقٍ حِسَابِيَهۡ ۞

فَهُوَ فِي عِيشَةٖ رَّاضِيَةٖ ۞ فِي جَنَّةٍ عَالِيَةٖ﴾

((ku karɓi littafina ku karanta, Lallai ni, na tabbata cewa ni mai haɗuwa da hisabina ne, Saboda haka, shi yana cikin wata rayuwa yardadda, a cikin Aljannah maɗaukakiya)) [Al-haaƙƙah:19-22].

**Bayan haka, ya ku Musulmai:**

Lallai Allah Mai karamci ne, Mai girma ne, kuma Mai ƙarfi ne, idan ya yi nufin abu sai yace masa kasance sai abin ya kasance, yayi alƙawarin kiyaye littafinSa, da taimakon addininSa, kuma yasanya ƙarshe mai kyau ga masu jin tsoronSa, yana arzurta wanda yaso batareda hisabi ba, kuma yana yaye baƙin cikin wanda ya nemi mafaka a wurinSa.

kuma duk wanda saninsa ga Allah ya ƙaru, yaƙininsa daShi zai ƙaru, kuma duk wanda ya munana zato a gare Shi; yayi haka ne sakamakon jahiltarsa ga kamalar sunayenSa da siffofinSa, kuma wannan siffa ce daga cikinsiffofin mutanen jahiliyya; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿يَظُنُّونَ بِٱللَّهِ غَيْرَ ٱلْحَقِّ ظَنَّ ٱلْجَٰهِلِيَّةِ﴾

((Suna yin zato ga Allah zato wanda bana gaskiya ba irin zaton Jahiliyya)) [Aali-Imran:154],

Kuma daga cikin amfanin imani da sunayen Allah da siffofinSa akwai: kyautata zato gare Shi, da dogaro a gare Shi, da mayarda dukkan lamurra zuwa gare Shi.

Ina neman tsarin Allah daga shaidan jefaffe.

﴿فَمَا ظَنُّكُم بِرَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ﴾

((To, mene ne zatonku game da Ubangijin halittu)) [As-saaffaat:87].

Allah Yasa min albarka tareda ku a cikin Alƙur'ani mai girma...

# HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gare Shi akan samun dacewa da kuma ni'imominSa, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya ina mai girmama al'amarinSa, kuma ina shaida cewa Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah yayi daɗin tsira da amincin Allah mai yawa a gare shi da iyalansa da sahabbansa.

**Ya ku Musulmai:**

Haƙiƙanin kyautata zato ga Allah yana bayyana ne a cikin ayukka na ƙwarai, kuma yana zama mai amfani ne tareda kyautatawa, kuma mafi alkhairin masu kyautata zato ga Allah daga cikin mutane shine wanda ya fisu biyayya a gare Shi, kuma duk lokacinda zaton bawa ga Allah ya zama mai kyau ne, lallai ayukkansa dole zasu zama masu kyau, kuma wanda ayukkansa suka munana, zatonsa zai munana, kuma idan kyautata zato ya haɗu da ayukkan saɓo zai zama amincewa ne ga makircin Allah, kuma kyaky-kyawan zato wanda yake kai bawa ga ayukkan biyayya shine mai amfani, kuma idan kyautata zato ga Allah ya samu tawaya a zuciyar bawa, lallai saɓo zai bayyana a gaɓɓansa.

sannan ku sani cewa, lallai Allah ya umurceku da yin Salati da sallama ga AnnabinSa....

# ABABEN DAKE KAWO MATSALA GA TAUHIDI[1]

Dukkan godiya sun tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa da gafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrukan kawunanmu da zunubban ayukkanmu, wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, kuma wanda ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma manzonSa ne, tsira da amincin Allah masu yawa su tabbata a gare shi da iyalan gidansa da sahabbansa.

**Bayan haka:**

Ya ku bayin Allah, kuji tsoron Allah haƙiƙanin tsoro; duk wanda yaji tsoron Allah zai samu tsira, kuma wanda ya kawar da kai daga ambatonSa zai halaka.

**Ya ku Musulmai:**

Jin daɗin bawa tana cikin kamalar bautarsa ga Allah, kuma tsayar da bauta yana kasancewa ne da tsarkake aiki ga Allah da bin shiriyar Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi, kuma idan bawa yayi wani aiki amma bai tsarkake Allah a cikinsa ba, aikin zai zama ƙura mai bin iska; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَقَدِمْنَآ إِلَىٰ مَا عَمِلُواْ مِنْ عَمَلٍ فَجَعَلْنَٰهُ هَبَآءً مَّنثُورًا﴾

((Kuma Muka gabatar da abin da suka aikata na aiki, sai Muka sanya shi ƙura mai ɗaiɗaituwa)) [Al-furƙaan:23].

Kuma idan bawa ya tsarkake Allah a cikin aikin amma kuma bai bi shiriyar Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ba, za'a mayarda aikin a gare shi; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Duk wanda yayi wani aiki wanda babu umurninmu a cikinsa to wannan aikin abin mayar masa ne**».

(Muslim ya ruwaito shi).

---

(1) Wannnan huɗubar anyita ne a Masallacin Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- a ranar Juma'a, ashirin da takwas ga watan Zhil-ƙa'ada. shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da ashirin da shida bayan Hijra.

kuma idan aiki ya kasance tsarkakakke kuma dai-dai, zai kasance abin karɓa kuma abin godewa akai; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ كَانَتۡ لَهُمۡ جَنَّٰتُ ٱلۡفِرۡدَوۡسِ نُزُلًا﴾

((Lallai ne, waɗanda suka yi imani kuma suka aikata ayukka na ƙwarai, Aljannahr Firdausi zata kasance ita ce masauki a gare su)) [Al-kahf:107].

kuma addini ya tsayu ne akan korewa da tabbatarwa, addinin mutum ba zai cika ba sai tareda su, yin bara'a daga duk wasu ababen bauta da ma'abotansu, da kuma tabbatarda bauta ga Allah Shi kaɗai; Allah -Mai girma da ɗaukaka- ya ce:

﴿فَمَن يَكۡفُرۡ بِٱلطَّٰغُوتِ وَيُؤۡمِنۢ بِٱللَّهِ فَقَدِ ٱسۡتَمۡسَكَ بِٱلۡعُرۡوَةِ ٱلۡوُثۡقَىٰ لَا ٱنفِصَامَ لَهَاۗ وَٱللَّهُ سَمِيعٌ عَلِيمٌ﴾

((Duk wanda ya kafurce da dagutu kuma ya yi imani da Allah to tabbas ya yi riko da ƙwaƙƙwarar igiyar da ba ta tsinkewa, kuma Allah Mai ji ne kuma Mai ilimi ne)) [Al-baƙarah:256].

kuma Annabi  tsira da aminci su tabbata a gare shi ya ce:

«**Duk wanda yace La'ilaha illAllah, kuma ya kafircema duk wani abin da ake bauta koma bayan Allah, an haramta taɓa dukiyarsa da jininsa, kuma hisabinsa yana ga Allah Mai girma da ɗaukaka**».

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

kuma mafi girman umurni a cikin musulunci shine umurni da Tauhidi, kuma mafi girman hani a cikinsa shine hani daga kishiyarsa,

An tambayi Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-: «Wane zunubi ne mafi girma? Sai yace: **ka sanya ma Allah kishiya alhali kuwa shi ne ya halicce ka**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi),

kuma da`awar Manzanni ta hadu akan umurni da kaɗaita Allah da bauta Shi kaɗai, da tsoratarwa daga haɗa Shi da wani a cikin bauta, ko shiga huruminsa.

﴿وَلَقَدۡ بَعَثۡنَا فِي كُلِّ أُمَّةٖ رَّسُولًا أَنِ ٱعۡبُدُواْ ٱللَّهَ وَٱجۡتَنِبُواْ ٱلطَّٰغُوتَۖ﴾

((Haƙiƙa mun aika ga kowace al'ummah Manzo cewa ku bautama Allah

kuma ku nisanci ɗagutu)) [An-nahl:36],

kuma duk wanda ya lizimci bautar Allah kamar yadda Allah Mai girma da ɗaukaka Yayi umurni, zai samu aminci a kansa, dukiyarsa, ƴaƴansa da gidansa, kuma zai samu aminci a cikin ƙabarinsa, da kuma ranar tara mutane da kuma hisabi; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ وَلَمْ يَلْبِسُوٓا۟ إِيمَـٰنَهُم بِظُلْمٍ أُو۟لَـٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلْأَمْنُ وَهُم مُّهْتَدُونَ﴾

((Waɗanda suka yi imani, kuma ba su gauraya imaninsu da zalunci ba, waɗannan suna da aminci, kuma sune shiryayyu)) [Al-an`aam:82].

kuma Tauhidi na gaskiya yana tsarkakewa daga zunubbai, yana kankare kusakurai, yana hana shiga wuta; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Lallai Allah ya haramta wuta ga wanda ya ce La'ilaha illallahu yana mai neman yardar Allah da ita**»

(Bukhari da Muslim ne suka ruwaito shi),

kuma duk wanda ya tsayarda tauhidi na wajibi dana mus'tahabbi zai shiga Aljannah batareda hisabi ba, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata agare shi- yabada labarin siffofinsu da faɗinsa:

«**Sune waɗanda basa neman ayi masu ruƙuya** -tofi-, **basa yin lalas da wuta, basa camfi kuma suna dogara ne ga Ubangijinsu**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi);

zukatansu suna rataye da Allah, kuma suna mayarda al'amarinsu gare Shi.

kuma sakamakon shirka mai muni ne, yana rusa aiki kuma yana fusata Ubangiji; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَلَقَدْ أُوحِىَ إِلَيْكَ وَإِلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِكَ
لَئِنْ أَشْرَكْتَ لَيَحْبَطَنَّ عَمَلُكَ وَلَتَكُونَنَّ مِنَ ٱلْخَـٰسِرِينَ﴾

((Lallai mun yi wahayi a gare ka da kuma waɗanda suka gabace ka cewar inda ace zaka yi shirka tabbas aikinka zai rushe kuma za ka kasance daga cikin masu hasara)) [Az-zumar:65],

kuma Annabi -tsira da Amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Duk wanda ya mutu alhali kuma yana kiran -bauta-wani koma bayan Allah zai shiga Wuta**»

(Bukhari ya ruwaito shi),

abinda yafi wannan shine; ita shirka tana wajabta dawwama a cikin wuta; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَغۡفِرُ أَن يُشۡرَكَ بِهِۦ وَيَغۡفِرُ مَا دُونَ ذَٰلِكَ لِمَن يَشَآءُۚ﴾

((Lallai, Allah baya gafara idan aka haɗa shi da wani cikin bauta amma yana gafarta laifin da yake koma bayan haka ga wanda ya so)) [An-nisa`:48].

Kuma saboda shirka tana gadarda halaka a duniya da lahira; yasa badaɗayin Allah Annabi Ibrahim -aminci ya tabbata a gre shi- ya roƙi UbangijinSa ya kareshi daga gareta, Allah Mai tsarki Yabamu labarin Annabi Ibrahim, ya ce:

﴿وَٱجۡنُبۡنِي وَبَنِيَّ أَن نَّعۡبُدَ ٱلۡأَصۡنَامَ﴾

((Kuma ka nisantar dani da ƴaƴana daga bautar gumaka)) [Ibrahim:35],

Ibrahim At-taimi -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«wa zai samu amincewa ga kansa daga yin shirka bayan Annabi Ibrahim?».

kuma mafi alkhairin abinda mai kiran mutane zai kirasu zuwa gare shine kalmar tauhidi da abinda take nuni zuwa gare shi. Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya cema Mu'az ɗan Jabal -Allah Ya yarda da shi-:

«**Lalli, kai zaka je wurin wasu mutane ma'abota littafi, farkon abinda zaka fara kiransu zuwa gare shi shine; Shaidawa Babu Abin bauta da gaskiya sai Allah**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

kuma duk wanda ya kira wanin Allah, haƙiƙa ya zalunci kansa

﴿وَلَا تَدۡعُ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَا لَا يَنفَعُكَ وَلَا يَضُرُّكَۖ فَإِن فَعَلۡتَ فَإِنَّكَ إِذٗا مِّنَ ٱلظَّٰلِمِينَ﴾

((Kuma kada ka kirayi wanin Allah, abin da ba zai amfaneka bakuma ba zai cutar da kai ba, To, idan ka aikata haka, lallai kai kana daga cikin masu zalunci)) [Yunus:106].

kuma duk wanda ya gurfana a gaban gunki, ko ya ƙanƙantar da kansa ga wani ƙabari yana ƙaunar samun amfaninsa, haƙiƙa yana neman abinda ba zai taɓa samu ne ba, kuma kamar mai fatan samun ruwa ne daga ƙawalwalniya dake kan hanya

﴿وَمَنْ أَضَلُّ مِمَّن يَدْعُوا۟ مِن دُونِ ٱللَّهِ مَن لَّا يَسْتَجِيبُ لَهُۥٓ إِلَىٰ يَوْمِ ٱلْقِيَـٰمَةِ وَهُمْ عَن دُعَآئِهِمْ غَـٰفِلُونَ ۝ وَإِذَا حُشِرَ ٱلنَّاسُ كَانُوا۟ لَهُمْ أَعْدَآءً وَكَانُوا۟ بِعِبَادَتِهِمْ كَـٰفِرِينَ﴾

((Kuma wane ne mafi ɓata sama da wanda ke kiran wanin Allah wanda har zuwa ranar alƙiyama da ba zai amsa masa ba, alhali su -waɗanda ake kiran- rafkanannu ne daga kiran masu kiran nasu? kuma idan aka tara mutane zasu kasance maƙiya a gare su, kuma alhali sun kasance masu inkari ga bautarsu a gare su)) [Al-ahƙaaf:5-6].

kuma kiran matattu da roƙonsu biyan buƙatu kira ne wanda ba'a jin mai yinsa, kuma baƙin ciki ne wanda baya taɓa yayewa, Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَٱلَّذِينَ تَدْعُونَ مِن دُونِهِۦ مَا يَمْلِكُونَ مِن قِطْمِيرٍ ۝ إِن تَدْعُوهُمْ لَا يَسْمَعُوا۟ دُعَآءَكُمْ وَلَوْ سَمِعُوا۟ مَا ٱسْتَجَابُوا۟ لَكُمْ ۖ وَيَوْمَ ٱلْقِيَـٰمَةِ يَكْفُرُونَ بِشِرْكِكُمْ ۚ وَلَا يُنَبِّئُكَ مِثْلُ خَبِيرٍ﴾

((kuma waɗanda kuke kira koma bayan Allah basa mallakar koda fatar gurtsun dabino. Idan kun kira su, basa jin kiranku, kuma koda sun jiya, ba za su karɓa maku ba, kuma a ranar ƙiyama za su kafirce wa shirkarku, kuma babu mai ba ka labari, kamar wanda yake masani)) [Faaɗir:13-14].

Kuma wuce gona da iri a cikin girmama matattu da salihan bayi shine sababin kafircewar ƴan Adam da barinsu ga addininsu, kuma zaɓaɓɓen Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya tsoratar daga hakan a cikin faɗinsa:

«**Kashedinku da wuce iyaka a cikin addini, don abinda ya halakarda waɗanda suke gabaninku shine wuce gona da iri a cikin addini**»

(Al-Nasa'i ya ruwaito shi),

kuma mafi sharrin halitta shine wanda ya gurfana kan ƙaburbura yana roƙonsu koma bayan Allah, Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya cema Ummu Salma -Allah Ya yarda da ita-

«**waɗancan mutane ne idan salihin mutum a cikin su ya mutu, -ko wani bawa salihi-, sai su gina masallaci a kan kabarin sa, sai su zana irin waɗancan hotunan a cikin sa, waɗancan mutanen sune mafi sharrin halitta a wajen Allah**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

kuma sihiri yana dusashe hasken imani kuma yana rusa musulunci:

﴿وَلَقَدْ عَلِمُوا۟ لَمَنِ ٱشْتَرَىٰهُ مَا لَهُۥ فِى ٱلْـَٔاخِرَةِ مِنْ خَلَـٰقٍ﴾

((Kuma hakika sun sani tabbas wanda ya saye shi -sihiri- ba shi da wani rabo a Lahira)) [Al-baƙarah:102],

kuma zuwa wurin bokaye wata ɓarna ce a cikin adddini kuma taɓin hankali ne, Allah Mai girma da ɗaukaka ya ce:

﴿قُل لَّا يَعۡلَمُ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ ٱلۡغَيۡبَ إِلَّا ٱللَّهُۚ﴾

((Kace: Babu wani wanda yake cikin sammai da ƙasa wanda yasan gaibu sai Allah)) [An-naml:65]

Kuma Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Duk wanda yaje wurin boka ko mai tsibbu ya tambayesa wani abu kuma ya gasgata shi, haƙiƙa ya kafircewa abinda aka saukar ga Muhammad**»

(Ahmad ya ruwaito shi).

kuma layu kamar irinsu kambu da guru da ta ko wadda ake haɗawa da sadaf -wanda ake samu a ruwa- da abunda yayi kama dasu, basa ƙara wanda yake ɗauke dasu komai sai rauni a cikin dogara ga Allah,

«Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yaga wani mutum ya sanya kambun ƙarfe a hanunsa, sai yace mashi: **Kaiconka, mene ne wannan**? Yace: Na sanya shi ne saboda ya kare ni daga wani ciwo raunin damtse, sai yace mashi: **Ka cire shi, bazai ƙara maka komai sai rauni; kayi jifa da shi, kuma da ace ka mutu alhali yana jikinka bazaka samu rabauta ba har abada**»

(Ahmad ya ruwaito shi).

kuma ɗaura layu shirka ne da Allah; Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Duk wanda ya rataya laya; to hakika ya yi shirka**»

(Ahmad ya ruwaito shi).

kuma duk wanda ya rataya wani abu, Allah zai jinginashi zuwa ga wannan abin daya rataya sai ya halaka; tsira da aminci su tabbata a gare shi ya ce:

«**Duk wanda ya rataya wani abu, za'a jingina shi zuwa gare shi**»

(At-tirmizi ya ruwaito).

kuma ba'a neman samun Albarka ko yin tabbarruki daga itace da duwatsu, su kawai wasu ne daga cikin halittun Allah, waɗanda basa cutarwa kuma basa amfanarwa.

kuma ba'a zubarda jinin dabba don neman kusanci sai ga Allah, duk wanda yayi yanka don wanin Allah ya faɗa a cikin taɓon shirka, tsira da aminci su tabbata a gare shi ya ce:

«**Allah ya tsinema wanda yayi yanka don wanin Allah**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma alwashi ibada ne; ba'a yinsa ga wanin Allah, tsira da aminci su tabbata a gare shi ya ce:

«**Duk wanda yayi alwashi zai bi Allah to ya bishi, kuma duk wanda yayi alwashin saɓon Allah, kada ya saɓa Masa**»

(Bukhari ya ruwaito shi).

kuma duk wanda ya nemi tsarin Allah lallai zai kare shi, kuma wanda ya fake ga waninSa zai tozartar dashi, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yana cewa:

«**Duk wanda ya sauka a wani masauki sai yace: Ina neman tsari da cikakkun kalmomin Allah daga sharrin abinda ya halitta, babu abinda zai cutarda shi har ya tashi daga wannan masaukin nasa**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma idan musibu da baƙin cikin zamani suka same ka, kada ka nemi agajin wanin Allah, kada ka kira waninSa, kada ka ƙanƙantar da kai ga wani mamaci dake cikin ƙabarinsa, ko wasu ƙasusuwa dasuka rududduge a cikin ƙusurwar ƙabari, ka miƙa buƙatarka zuwa ga wanda yake a sama; a can ake karɓar a addu'a:

﴿أَمَّن يُجِيبُ ٱلْمُضْطَرَّ إِذَا دَعَاهُ﴾

((waye yake karɓa roƙon wanda yake cikin tsanani idan ya roƙeSa)) [An-naml:62].

kuma ba makawa daga jarabawa:

﴿أَحَسِبَ ٱلنَّاسُ أَن يُتْرَكُوٓاْ أَن يَقُولُوٓاْ ءَامَنَّا وَهُمْ لَا يُفْتَنُونَ﴾

((Ashe, mutane suna zaton a bar su suce: Mun yi imani, kuma ba za'a jarabasu ba?)) [Al-ankabuut:2],

kuma idan wata musiba ta sameka, to, ka fuskanceta da yarda da ƙaddarar Allah da kuma miƙa wuya, Allah Mai girma da ɗaukaka ya ce:

﴿وَمَن يُؤْمِنۢ بِٱللَّهِ يَهْدِ قَلْبَهُۥ﴾

((Kuma wanda ya yi imani da Allah zai shiryi zuciyarsa)) [At-tagabun:11].

Alƙama ya ce:

«Shi ne mutumin da musiba zata same shi, sai yasan cewa daga Allah ne, sai ya yarda kuma ya mika wuya».

kuma kada kayi fushi da abinda aka rubuta maka; domin funshinka baya yayeta, kuma ka kiyayi yin nadamar rashin ɗaukar wani mataki kafin afkuwar wata ƙaddara da amfani da kalmar "da ace nayi kaza", domin wannan lafazin daga shaiɗan yake, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Kayi ƙoƙari kan duk abinda zai amfane ka, kuma ka nemi taimakon Allah kada ka gaza, idan wani abu ya same ka kada kace: Da na yi kaza da kaza zai kasance, sai dai kace: Haka Allah ya ƙaddara, kuma yana yin abinda ya so; domin ita faɗin da nayi kaza tana buɗe ƙofar shaidan ne**»

(Muslim ya ruwaito shi).

don haka, ka mayarda lamurranka zuwa ga Allah, ba abinda zai zo maka a cikin wannan duniya sai rabonka daga cikinta:

﴿قُل لَّن يُصِيبَنَآ إِلَّا مَا كَتَبَ ٱللَّهُ لَنَا﴾

((Kace: Ba abinda zai same mu sai abinda Allah ya rubuta mana)) [At-taubah:51].

Ubada ɗan As-samit -Allah Ya yarda dashi- ya cema ɗansa:

«Ya kai ɗana! kasani cewa bazaka taɓa jin ɗan-ɗanon imani ba har sai kasan cewa duk abinda ya sameka daman ba zai taɓa kuskureka ba, kuma duk abinda ya kuskure maka bazai taɓa samunka ba».

kuma yin dogaro ga sabubba tun daga zuciya da gaɓɓai wata illa ce a tauhidi, kuma inkarin samuwar sabubba rauni ne, abinda yake wajibi shine; riƙo da sabubba na halal tareda dogaron zuci ga Allah.

kuma da dogaro ga Allah Mai tsarki ababe masu tsanani suke sauƙaƙa, kuma dashi ne ake shimfiɗa arziki da yaye baƙin ciki.

kuma amincewa da makircin Allah ruɗi ne:

﴿أَفَأَمِنُواْ مَكْرَ ٱللَّهِۚ فَلَا يَأْمَنُ مَكْرَ ٱللَّهِ إِلَّا ٱلْقَوْمُ ٱلْخَٰسِرُونَ﴾

((Shin sun amince ma makircin Allah? To, babu mai amincema makircin

Allah face mutane masu hasara!)) [Al-a`raaf:99],

kuma yanke ƙauna daga samun rahamar Allah shine Al-ƙunuɗ, Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿قَالَ وَمَن يَقۡنَطُ مِن رَّحۡمَةِ رَبِّهِۦٓ إِلَّا ٱلضَّآلُّونَ﴾

((Kuma wane ne yake yanke tsammani daga rahamar Ubangijinsa, face ɓatattu?)) [Al-hijr:56].

Kuma haɗawa tsakanin: Kwaɗayi, tsoro da so itace hanya madai-daiciya. kuma ita shirka tanada ɓoyayyun ƙofofi da shaiɗan yake ƙoƙarin ganin bayi sun shiga cikinsu, Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Abu mafi bantsoro dana ke ji muku tsoro akansa: Shi ne ƙaramar shirka, sai aka tambaye shi mene ne, sai yace: Itace riya**»

(Ahmad ya ruwaito shi),

kuma riya ita ce cutar masu aiki, tana lalata aiki kuma tana fusata Ubangiji, tafi zama abin tsoro akan mutanen kirki sama da Dujal, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Ashe bana baku labari akan abinda nafi ji maku tsoro sama da Dujal ba**, yace: Sai muka ce: Eh, kabamu labari, sai yace: **Ɓoyayyar shirka: Mutum zai tashi yana sallah, sai ya kyautata sallarsa saboda wani mutum dayake kallonsa**»

(Ibnu Majah ya ruwaito shi).

kuma ana ƙwaɗayin samun lada daga Allah da yin aiki na ƙwarai, ba'a yinsa don samun ƙawar duniya, kuma duk wanda ya juyarda zuciyar wurin yin aiki na kwarai zuwa ga samun wata ƙawar duniya; lallai, aikinsa ya rushe, kuma yayi hasara a ranar lahira; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿مَن كَانَ يُرِيدُ ٱلۡحَيَوٰةَ ٱلدُّنۡيَا وَزِينَتَهَا نُوَفِّ إِلَيۡهِمۡ أَعۡمَٰلَهُمۡ فِيهَا وَهُمۡ فِيهَا لَا يُبۡخَسُونَ ۞ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ لَيۡسَ لَهُمۡ فِي ٱلۡأٓخِرَةِ إِلَّا ٱلنَّارُۖ وَحَبِطَ مَا صَنَعُواْ فِيهَا وَبَٰطِلٞ مَّا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ﴾

((Duk wanda ya kasance yana nufin rayuwar duniya da ƙawarta, zamu cika masu ayukkansu a cikinta, kuma ba za'a tauye masu komai ba a cikinta. Waɗannan ne waɗanda basa da komai a Lahira face wuta, kuma abin da suka aikata a cikinta -duniya- ya rushe, kuma abin da suka kasance suna aikatawa lalatacce ne)) [Huud;15-16].

Kuma ba abinda musulmi yake so kamar Allah, kuma ba abinda yakai

matsayin Allah a cikin zuciyarsa, Shine Mai girma a zuciyarsa, kuma Maɗaukaki a ransa, kuma mai sonsa da gaskiya baya yin rantsuwa sai daShi, kuma yin rantsuwa da wanin Allah Mai tsarki -kamar Ka'aba, Annabi, Amana, da waliyyi- shirka ce a cikin tauhidi, Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Duk wanda yayi rantsuwa da wanin Allah haƙiƙa ya kafirta ko yayi shirka**»

(At-tirmizi ya ruwaito shi).

kuma yawan ranstuwa yana cin ƙaro da girmama Allah a cikin zuciya, don haka, ka kiyaye rantsuwarka koda da gaskiyarka, Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿وَٱحۡفَظُوٓاْ أَيۡمَٰنَكُمۡۚ﴾

((Kuma ku kiyaye rantsuwoyinku)) [Al-maa`idah:89],

Kuma ka kiyayi yin rantsuwa da ƙarya domin ita ce mai nutsarwa, kuma yana daga cikin girmama Allah: Yarda idan akayi rantsuwa da Allah koda shi wanda akayiwa rantsuwar yasan cewa wanda yayi rantsuwar ƙarya yakeyi, Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**kada kuyi rantsuwa da mahaifanku, kuma duk wanda yayi rantsuwa lallai yayi gaskiya a rantsuwar, kuma wanda aka yiwa rantsuwa da Allah Ya yarda, kuma duk wanda bai yarda ba to shi bana Allah ne ba**»

(Ibnu Majah ya ruwaito shi).

kuma yana daga cikin girmama Allah, rashin korar wanda yayi roƙo da sunan Allah, Annab -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shio- ya ce:

«**Duk wanda ya nemi tsari da sunan Allah ku tsare shi, kuma wanda ya roƙa da sunan Allah ku bashi, kuma ku karɓa kiran wanda ya gayyace ku**»

(Abu Dawud ya ruwaito shi).

kuma aibata zamani da canzawar yanayi -zafi ko sanyi- cutarwa ne ga Ubangijin talikai, Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Allah Mai girma da ɗaukaka ya ce: Ɗan Adam yana cutar daNi, yana zagin zamani; kuma Nine zamani a hannuna dukkan lamari yake, ina juyarda dare da rana**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

kuma saboda Addini ne sammai da ƙasa suka tsayu, kuma akansa ne aka tanadi Wuta da Aljannah, kuma yin izgili ga Addini ko hukuncinsa da ma'abotansa masu riƙo dashi, duk yana fitarda mutum daga cikin musulunci; Allah Mai girma da ɗaukaka ya ce:

﴿وَلَئِن سَأَلْتَهُمْ لَيَقُولُنَّ إِنَّمَا كُنَّا نَخُوضُ وَنَلْعَبُ ۚ قُلْ أَبِٱللَّهِ وَءَايَٰتِهِۦ وَرَسُولِهِۦ كُنتُمْ تَسْتَهْزِءُونَ ۝ لَا تَعْتَذِرُوا۟ قَدْ كَفَرْتُم بَعْدَ إِيمَٰنِكُمْ ۚ﴾

((kuma lallai idan ka tambayesu zasu ce: Kawai muna hira da wasa ne, kace: Shin da Allah da ayoyinSa da ManzonSa kuka kasance kuna izgili, kada ku kawo wani uzuri, haƙiƙa kun kafirta bayan imaninku)) [At-taubah:65-66].

kuma kada kayiwa Allah mugun zato -kamar ka riƙa tunanin cewa kafi ƙarfin abinda aka baka, ko ka rena wata ni'ima da Allah yaba waninka- wannan shine zato na Jahiliyya, duk abinda yake a duniya ya kasance ne da umurnin Allah da hikimarSa:

﴿يَظُنُّونَ بِٱللَّهِ غَيْرَ ٱلْحَقِّ ظَنَّ ٱلْجَٰهِلِيَّةِ ۖ يَقُولُونَ هَل لَّنَا مِنَ ٱلْأَمْرِ مِن شَىْءٍ ۗ قُلْ إِنَّ ٱلْأَمْرَ كُلَّهُۥ لِلَّهِ ۗ﴾

((Suna yima Allah zaton da bana gaskiya ba irin zaton Jahiliyya, suna cewa: Shin ko munada wani rabo cikin al'amarinnan -cin nasara- kace: Lallai dukkan al'amari na Allah ne)) [Aali-Imran:154].

Kuma ɗaukar hoto yana daga cikin manyan zunnubbai, anyiwa ma'abocinsa ƙyacewa (alƙawari) da Wuta; Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Dukkan mai hoto yana cikin wuta, za a sanya masa ga kowane hoto da yayi rayuwa da za a riƙa yi masa azaba da shi a cikin Jahannama**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

ka girmama Ubangijinka haƙiƙanin girmamawa, Shi Mai girma ne a cikin mulkinSa, wanda Ya dai-daita akan Al'arshinSa, Mai hikima a cikin ababen daya shar'anta, ka kiyaye abinda Allah ya wajabta akanka na salloli wajibai a cikin lokuttan su, kashedinka da wasa da sallah; domin ita ce ginshiƙin addini, Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Alƙawarin dake tsakaninmu dasu ita ce Sallah; duk wanda yabarta haƙiƙa ya kafirta**»

(At-tirmizi ya ruwaito shi).

kuma ka kasance mai nufin Ubangijinka a cikin kowane hali; idan kayi haka, lallai ayukkanka zasu kyautata.

Ina neman tsarin Allah daga shaidan jefaffe.

﴿قُلْ إِنَّ صَلَاتِي وَنُسُكِي وَمَحْيَايَ وَمَمَاتِي لِلَّهِ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ۞لَا شَرِيكَ لَهُۥۖ وَبِذَٰلِكَ أُمِرْتُ وَأَنَا۠ أَوَّلُ ٱلْمُسْلِمِينَ﴾

((kace: Lallai sallata da sukata -yanka- da rayuwata da mutuwata duk na Allah ne Ubangijin talikai, baShida abokin tarayya, kuma akan haka ne aka umurce ni, kuma nine na farkon musulmai)) [Al-an`aam:162-163].

Allah Yasa min albarka tareda ku a cikin Alƙur'ani mai girma...

## HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gare Shi akan samun dacewa da kuma ni'imominSa, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya ina mai girmama al'amarinSa, kuma ina shaida cewa Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah yayi daɗin tsira da aminci a gare shi da iyalansa da sahabbansa.

**Bayan haka, ya ku musulmai:**

Addini shine mafi tsadar abinda ka mallaka, ka kiyaye addininka ta hanyar nisanta fitintinu, domin fitina tana shiga zuciya, tana jawo ababe masu ruɗarwa da sharrora, Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi ya ce:

«**duk wanda ya zaburo mata -fitina- zata ɗauke shi**»

(Bukhari ya ruwaito shi).

kuma runtse idanu daga aikin haram na kallon mata; tsarkake rai ne, kuma biyayya ce ga Allah da ɗaukaka a cikin darajoji, Allah Mai girma da ɗaukaka ya ce:

﴿قُل لِّلْمُؤْمِنِينَ يَغُضُّوا مِنْ أَبْصَارِهِمْ وَيَحْفَظُوا فُرُوجَهُمْ ذَٰلِكَ أَزْكَىٰ لَهُمْ﴾

((ka cema muminai su kame ganinsu kuma su kiyaye farjojansu, hakan yafi tsarkakewa ga zukatansu)) [An-nuur:30]

kuma adon mace yana cikin kamun kanta, kuma kyawunta yana a cikin hijabinta, kuma ƙawarta tana a cikin riƙo da addininta, kuma matan sahabbai ababen koyi ne a cikin hijabi da kamun kai da kunya, Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿يَا أَيُّهَا النَّبِيُّ قُل لِّأَزْوَاجِكَ وَبَنَاتِكَ وَنِسَاءِ الْمُؤْمِنِينَ يُدْنِينَ عَلَيْهِنَّ مِن جَلَابِيبِهِنَّ
ذَٰلِكَ أَدْنَىٰ أَن يُعْرَفْنَ فَلَا يُؤْذَيْنَ﴾

((Ya kai Annabi! Ka ce ma matan ka da ƴaƴ'anka mata da matan muminai su kusantar zuwa ƙasa daga manyan tufafin da ke a kansu. Wancan ya fi sauƙin gane su - cewa `ya`ya masu `ya`nci ba bayi ba- domin kada a cutar dasu)) [Al-ahzaab:59].

Kuma sauraron kaɗe-kaɗe yana daga cikin zunubbai masu saka duhun zuciya kuma yana hana sauraron Alƙur'ani, Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Wasu mutane daga cikin al'ummata zasu zo, zasu halarta zina, da**

**alhariri da giya da kaɗe-kaɗe**»

(Bukhari ya ruwaito shi).

kuma mafi alkhairin abinda bawa zai saurara shine; maganar Ubangijin talikai, a cikinsa akwai haske, da shiriya da waraka.

kuma dukiya ta halal tana gyara addinin mutum, kuma ƙarfi ce a jiki, shiriya ce ga ƴaƴa, albarka ce a cikin kyauta, sababin karɓar addu'a ce kuma koyi ne da Annabwa, Allah -Mai girma da ɗaukaka- ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلرُّسُلُ كُلُواْ مِنَ ٱلطَّيِّبَٰتِ وَٱعۡمَلُواْ صَٰلِحًاۖ﴾

((Ya ku Manzanni, kuci daga halal kuma kuyi aiki na ƙwarai)) [Al-mu`minuun:51].

kuma dukiyar haram batada albarka, tanada cuta mai yawa, ma'abocinta yanada nadama mai tsawo, kuma ba'a karɓar addu'arsa.

sannan ku sani cewa, lallai Allah ya umurceku da yin Salati da sallama ga AnnabinSa....

# SUNAYEN ALLAH KYAWAWA[1]

Dukkan godiya sun tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa da gafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrukan kawunanmu da zunubban ayukkanmu, wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, kuma wanda ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, tsira da amincin Allah masu yawa su tabbata a gare shi da iyalan gidansa da sahabbansa baki ɗaya.

**Bayan haka:**

Ya ku bayin Allah kuji tsoron Allah haƙiƙanin tsoro, duk wanda yaji tsoron Ubangijinsa ya tsira, kuma wanda ya kawarda kai daga gare Shi ya halaka.

**Ya ku Musulmai:**

Sanin Allah ɗaya ne daga cikin rukunnan musulunci; shine asali wanda waninsa suke biye dashi, kuma sanin sunayen Allah da siffofinSa shine mafi falala kuma mafi wajibcin abinda zukata da rayuka suke samu kuma shine mafi falalar abinda hankula suke riska; Ibnul-Ƙayyim -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«Mafi daɗin abinda yake a cikin duniya shine; sanin Allah da ƙaunarSa».

kuma Alƙur'ani dukkansa yana kiran mutane zuwa yin nazari cikin sunayen Allah da siffofinSa da ayukkanSa, Shehin musulunci -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«Ambaton dake a cikin Alƙur'ani na sunayen Allah da siffofinSa da ayukkanSa yafi yawan abinda ka cikinsa na ambaton abinci da abin sha».

kuma Allah yana son wanda yake son ambaton siffofinSa, kuma Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- ya yi bushara ga wanda yake karanta Suratul-Ikhlas da cewa Allah yana sonsa, ya ce:

«**Ku tambayeshi don me yake hakan** -karanta ta- da aka tamayeshi sai yace: Saboda siffar Allah ce, kuma ina son karanta ta, sai Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: **Ku bashi labari lallai Allah**

(1) Wannan huɗubar anyita ne a Masallacin Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- a ranar Juma'a, Ashirin da uku ga watan Shawwal, shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da ashirin da shida bayan Hijra.

**yana son sa**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi)

Kuma sunayen Allah Mai tsarki sune mafi kyawun sunaye, kuma siffofinSa sune mafi kamalar siffofi:

﴿لَيۡسَ كَمِثۡلِهِۦ شَيۡءٞۖ وَهُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡبَصِيرُ﴾

((Babu abinda yayi kama da Shi kuma Shi Mai ji ne, Mai gani ne)) [Ash-shuuraa:11].

Kuma kowane musulmi ya kamata yasansu kuma yasan ma'anoninsu. Ubangijinmu Maɗaukaki shine Mai rahama Mai jin ƙai; Rahamarsa ta yalwaci komai, kuma rahamarSa itace mafi faɗin sifofinSa, Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**lallai, Allah yanada rahama ɗari, ya saukarda rahama guda tsakanin aljanu da mutane da dabbobi da ƙwari, da ita ce suke tausayi da rahamar junansu, da ita ce dabbar daji take tausayin ɗanta, kuma Allah ya jinkirta sauran kashi casa'in da tara, da ita zai yiwa bayinsa rahama a ranar Ƙiyama**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

kuma ba wani mutum face yana jujjuyawa ne a cikin rahamar Allah, kuma duk wata ni'ima dakake gani daga cikin rahamar Allah take, kuma duk wata Uƙuba da aka kawar yana daga cikin tasirin rahamar Allah ne, Ibnul-Ƙayyim -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«Shi wannan littafin -Ma'ana faɗinsa: «**Rahamata ta riga fushi na**»- ya kasance kamar alƙawari ne daga Allah zuwa ga hallittu, ba don shi ba, da haliittu sun kasance cikin wani sha'ani na daban»,

kuma duk wanda ya kasance kusa ga Allah, zai fi cancantar samun rahamar Allah.

kuma Allah Mai tsarki Shine Mamallaki: Mai juyarda halittarsa kamar yadda yaso, ba wani abu mai motsi da zai motsa, kuma ba wani abu mai natsuwa da zai natsu face sai da iliminSa da nufinSa, yana bada umurni kuma yana hanawa, yana ɗaukakawa kuma yana ƙasƙantawa ba mahani gara Shi kuma ba mai jayayya, ba abunda yake buwayarSa a cikinsu; don haka, ka mayarda al'amurranka ga Mai mulki, don a hanunsa ne mabuɗai suke kuma ka dogara a gare Shi cikin kowane hali kake, zaka same Shi kusa da kai.

kuma Shine Alƙuddus: Abin tsarkakewa daga dukkan tawaya, Wanda ya siffantu da siffofin kamala; ba wani abin bauta da gaskiya wanda za'a

roƙa tareda Shi, kuma ba wani masoyi tareda Shi wanda za'a kira.

kuma Shine As-salam: wanda ya aminta daga dukkan aiboba da tangarɗa a cikin suffofi, dukan halittu suna tsarkake Ubangijinmu daga wannan; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿يُسَبِّحُ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِ﴾

((Abinda yake a cikin sammai da ƙasa duk suna tsarkake Allah)) [Al-jumu`a:1].

Kuma Allah Mai girma da ɗaukaka Shine wanda ake amincema: HalittunSa sunada aminci cewa ba zai zalunce ba ko ya rage masu haƙƙoƙansu, don haka, kayi guzuri na taƙawa; don ayukka abin kiyayewa ne kuma abin ruɓunya su.

Kuma Shine Mai kewayewa ga dukkan halittunSa, Wanda yake ganin da abinda ƙiraza suka ɓoye, kada ka amincema makircin Allah idan har ka saɓa maSa.

kuma Shine wanda yake shaida -halarce- akan dukkan zantuka da ayukkan bayinSa

﴿وَمَا ٱللَّهُ بِغَٰفِلٍ عَمَّا تَعۡمَلُونَ﴾

((Kuma Allah bai kasance Mai rafkana ba daga abinda kuke aikatawa)) [Al-baƙarah:74].

Kuma Shine Mabuwayi: Ba'a iya galaba akanSa, Yafi ƙarfin komai kuma Ya buwayi komai, duk wata wahala ta zama mai sauƙi ga ƙarfinSa, kuma duk wani tsanani yayi laushi ga ƙarfinSa,

«**Idan Allah ya zartar da wani lamari a sama, Mala'iku suna buga fukafukansu saboda ƙanƙan da kai ga maganarSa, kai ka ce wata sarƙa ce a kan falalen dutse**»,

duk wanda ya kusance Shi da biyayya zai samu ɗaukaka; Allah -Mai tsarki- ya ce:

﴿مَن كَانَ يُرِيدُ ٱلۡعِزَّةَ فَلِلَّهِ ٱلۡعِزَّةُ جَمِيعًاۚ﴾

((Duk wanda yake neman wata izza, to, Allah ne da izza baki ɗaya)) [Faaɗir:10],

kuma duk wanda yayi fito-na-fito da Shi da saɓa maSa zai ƙasƙanta, kada ka kalli saɓon da kakeyi, ka kalli girman wanda kake saɓamawa.

kuma Shine Maɗaukaki akan komai:

﴿إِلَيْهِ يَصْعَدُ ٱلْكَلِمُ ٱلطَّيِّبُ وَٱلْعَمَلُ ٱلصَّٰلِحُ يَرْفَعُهُۥ﴾

((Zuwa gare Shine Magana Mai daɗi ke hawa, kuma Yana ɗaukaka aiki na ƙwarai)) [Faaɗir:10]

kuma Shine Mai tilastawa: Ya ɗora bayinSa akan abinda yake so, ba mai iya ƙin yin yadda Ya ɗorasu akai daga cikinsu

﴿إِنَّمَآ أَمْرُهُۥٓ إِذَآ أَرَادَ شَيْـًٔا أَن يَقُولَ لَهُۥ كُن فَيَكُونُ﴾

((UmurninSa ga komai idan Ya yi nufin yinsa sai Yace mashi kasance sai ya kasance)) [Yaasin:82]

Ya ce da sama da ƙasa:

﴿ٱئْتِيَا طَوْعًا أَوْ كَرْهًا قَالَتَآ أَتَيْنَا طَآئِعِينَ﴾

((Ku zo kuna masu biyayya ko akan tilas suka ce munzo muna masu yin ɗa'a)) [Fussilat:11],

kuma Allah -Mai tsalki- Shine Mai ƙarfafar zukatan dasuka samu karaya.

kuma Shine Mai girma; komai yana ƙasa daShi, ba abinda yafi Shi girma.

﴿وَٱلْأَرْضُ جَمِيعًا قَبْضَتُهُۥ يَوْمَ ٱلْقِيَٰمَةِ وَٱلسَّمَٰوَٰتُ مَطْوِيَّٰتٌۢ بِيَمِينِهِۦ﴾

((Ƙasa baki ɗayanta damƙarSa ce a ranar ƙiyama kuma sammai suna naɗe a damarSa)) [Az-zumar:67],

«**Zai ɗora sammai akan ɗan yatsa, ƙassai akan ɗan yatsa, itace akan ɗan yatsa, ruwa da turɓaya akan ɗan yatsa, kuma Ya ɗora hallittu akan ɗan yatsa**»

«Bukhari da Muslim suka ruwaito shi»

kuma Shine kaɗai Mai jin girma da isa, girman bai dace da kowa ba sai Shi, kuma duk wanda yayi girman kai daga cikin halittarSa makomarsa wutar Saƙar; Allah Mai girma da ɗaukaka ya ce:

﴿أَلَيْسَ فِى جَهَنَّمَ مَثْوًى لِّلْمُتَكَبِّرِينَ﴾

((Wai shin ba wurin zama ne acikin jahannama ga masu girman kai!)) [Az-zumar:60],

kuma wajibin bawa ne ya kasance mai ƙasƙantar da kai da tawali'u ga UbangijinSa, kuma ya kasance mai tawa'li'u ga bayin Allah.

kuma Shine Mahalicci, wanda ya samarda duniya ya kautata ta, duk

wanda yayi nazari akanta zata ƙayatar dashi, kuma Shine Mai yawan halitta wanda ya ƙware cikin duk abinda ya halitta.

﴿فَتَبَارَكَ ٱللَّهُ أَحۡسَنُ ٱلۡخَٰلِقِينَ﴾

((Tsarki ya tabbata ga Allah Mafi kyawun Masu Halitta)) [Al-mu`minuun:15].

Kuma Shine Mai ƙirƙira; Ya ƙirƙiro halittu daga rashi; tun daga Taurari, Rana, da Wata da sauran halittu dake sararin samaniya:

﴿كُلٌّ فِي فَلَكٍ يَسۡبَحُونَ﴾

((dukkansu suna iyo ne a cikin falaki)) [Al-anbiya`:33],

suna bada mamaki ga duk wanda duk yayi tunani akansu kuma ya wa'azantu.

kuma Shine Mai Surantawa; ya suranta halittunSa akan surori mabanbanta, da kamanni masu saɓama juna kamar yadda yake so:

﴿فَمِنۡهُم مَّن يَمۡشِي عَلَىٰ بَطۡنِهِۦ وَمِنۡهُم مَّن يَمۡشِي عَلَىٰ رِجۡلَيۡنِ وَمِنۡهُم مَّن يَمۡشِي عَلَىٰٓ أَرۡبَعٖ﴾

((Daga cikinsu akwai masu jan ciki, kuma daga cikinsu akwai masu tafiya akan ƙafafu biyu, a cikinsu kuma akwai masu tafiya akan ƙafafu huɗu)) [An-nuur:45].

kuma Ya halicci mutum a cikin sura mai kyau

﴿لَقَدۡ خَلَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ فِيٓ أَحۡسَنِ تَقۡوِيمٖ﴾

((Haƙiƙa mun halicci mutum a cikin mafi kyawun sura)) [At-teen:4].

kuma Shine mai Surantawa; kuma ya haramta yin hoto ga halittunSa, kuma yayi alƙawarin azaba ga masu yin hoto daga cikin hallittunSa;

kuma «**Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya tsinema masu yin hoto**»

(Bukhari ya ruwaito shi),

kuma ya ce: «**duk mai yin hoto yana wuta**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

kuma Shine Mai yawan gafara; yana shafe zunubban duk wanda ya koma zuwa gare Shi daga cikin bayinSa komai yawan zunubbanSa, da sujada ɗaya tareda tuba ya yafema masu yima Fir'auna aikin sihiri, ya yafe masu kafircinsu da ayukkansu na sihiri da fito-na-fiton da sukayi ga Annabinsu:

﴿وَإِنِّي لَغَفَّارٞ لِّمَن تَابَ وَءَامَنَ وَعَمِلَ صَٰلِحٗا ثُمَّ ٱهۡتَدَىٰ﴾

((Kuma lallai Ni haƙiƙa Mai gafara ne ga wanda ya tuba kuma ya yi imani, kuma ya aikata aikin ƙwarai, sa'an nan kuma ya nemi shiriya)) [Ɗaaha:82].

kuma Shine Mabuwayi; halittu baki ɗaya suna ƙarƙashin tilastawarSa da damƙarSa, Yana cire ran wanda yaso a lokacinda yaso, ba abinda zai faru a duniya saida nufinSa koda kuwa bawa yayi ƙoƙarin tabbatar da abin.

kuma Shine Mai buɗi; Yana buɗe ƙofofin arziki da rahama da sabbubban samunsu ga bayinSa, kuma yana buɗe masu abinda ya kullu a gare su daga cikin lamurransu.

kuma Shine Mai yawan arzurtawa; yana arzurta bawa ta sama da ƙasa:

﴿قُلۡ مَن يَرۡزُقُكُم مِّنَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ قُلِ ٱللَّهُۖ﴾

((Kace, wa yake arzurtaku daga sammai da ƙasa. Kace: Allah ne)) [Saba`:24],

Ya lulluɓe komai da arzikinSa, ba wata dabba a cikin ƙasa face arzikinta yana ga Allah, Ya arzurta jirajirai a cikin uwayensu, Ya arzurta dabbobi a cikin daji, da tsuntsaye a can cikin sheka, da kifaye a ƙasan gulbi.

kuma Shi ne Mai kyauta; Yana ba wanda ya so abinda Ya so, taskokin sammai da ƙasa a hannunSa suke, yayi kyautar zuri'a mai albarka ga Annabawa bayan sun kai shekarun yanke ƙauna daga samun haihuwa, kuma Annabi Sulaiman ya roƙi UbangihinSa Mai baiwa ya bashi mulki wanda ba zai ba wani mutum irinsa a bayansa ba, sai Allah ya bashi ayoyi da ababen mamaki daga cikin kyautarSa; Ya hore masa Iska da Aljanu, kuma aka bashi marmaro na ƙarfe mai gudana, dukkansu ababen horewa ne daga umurninsa.

kuma Shi ne Masani; Yasan abinda yake sirrance da ɓoye, ba abinda yake ɓoyuwa a gare Shi na zantuttuka da ayukkan da bayinSa suke aikatawa:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٞ﴾

((Lallai Allah Masani ne akan dukkan komai)) [Al-anfaal:45].

kuma Shi ne Mai ji; yana jin abinda ake tattaunawa acikin ganawa da abinda aka bayyana, da abinda yake a sirrance da ɓoye, idan ka bayyana zanceka zai ji zancen, idan ka sirranta shi ga abokinka zai ji sirrin, idan kuma ka ɓoye a zuciyarka zai san abinda ka ɓoye.

kuma Shi ne Mai gani; Yana ganin ɓoyayyun ababe komai ƙanƙantarsu, ba wata ƙwayar zarra dazata ɓoyu a gare Shi komai ƙanƙantarta, Yana ganin abinda yake ƙarƙashin ƙasa a cikin duhun dare, kuma Yana ganin

ƙasan teku a cikin tsananin duhu.

kuma Shi ne Maɗaukaki kuma Masanin komai; tafiyar baƙar tururuwa akan falalen dutse a cikin duhun dare bata ɓoyuwa a gare Shi, idan kayi aiki a fili Zai ganka, kuma Yana ganinka idan kayi wani aikin a ɓoye koda a ƙuryar gidanka ne.

﴿إِنَّ رَبَّكَ لَبِٱلۡمِرۡصَادِ﴾

((Lallai ne, Ubangijinka Yana nan a madakata)) [Al-fajr:14],

kuma duk wanda yasan cewa Allah yana ganinsa; zai ji kunyar Allah ya gansa yana aikin saɓo.

kuma Shi ne Mai hikima; ba wani giɓi ko kuskure a cikin hukunce-hukuncenSa ko ababen daya shar'anta, kuma ba wani mutum da zai iya cin gyaran hukunce-hukuncen Allah ko ya warwaresu ko yayi jayayya akansu

﴿وَٱللَّهُ يَحۡكُمُ لَا مُعَقِّبَ لِحُكۡمِهِۦۚ﴾

((Kuma Allah ne Mai hukunci babu mai cin gyaran hukuncinSa)) [Ar-ra`ad:41].

abinda yake wajibi shine miƙa wuya da karɓar hukunce-hukunceSa:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ يَحۡكُمُ مَا يُرِيدُ﴾

((Allah Yana hukunta abinda yaso)) [Al-maaidah:1],

kuma babu abinda ya dace da bayinSa sai shari'arSa mai tsarki, kuma duk wanda yayi izgili da addininSa ko shari'arSa, lallai Allah zai ƙasƙantar daShi.

kuma Shi ne Mai tausayi: Yana tausayama bayinSa, Ya kawo masu arziki alhali basuda masaniya akai.

kuma Shi ne Masani Mai bada labarin komai na al'amurran bayinSa, ba abinda yake ɓoyuwa a gare Shi, Mai ganin haƙiƙanin dukkan komai:

﴿فَسۡـَٔلۡ بِهِۦ خَبِيرٗا﴾

((Ka tambaye mai bada labari game dashi)) [Al-furƙaan:59],

kuma Shi ne Mai Haƙuri; baya gaggauta yin uƙuba ga bayinSa saboda zunubbansu, kuma baYa hanasu ni'imominSa da falalarSa saboda kusakuransu, suna saɓa maSa amma kuma Yana arzurtasu, suna yin zunubi amma kuma yana jinkirta masu, suna bayyana ayukkan ɓarna amma yana

suturce su; kada ka ruɗu da hakurin Allah da karamcinSa akanka, azaba tana iya afka maka kwatsam:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلۡإِنسَٰنُ مَا غَرَّكَ بِرَبِّكَ ٱلۡكَرِيمِ﴾

((Ya kai mutum! Me ya ruɗe ka game da Ubangijinka, Mai karamci)) [Al-infiɗar:6].

kuma Shi ne Mai girma; idan yayi magana da wahayi, girgiza tana kama sammai -ko tsawa- mai tsanani saboda tsoron Allah, kuma idan mazauna sammai suka ji hakan sai su faɗi suna sumammu kuma suna masu sujuda.

kuma Shi ne Mai godiya; Yana bada lada mai yawa akan aiki ɗan kaɗan, kuma yana yafe kusakurai masu yawa, kada ka raina aiki na ƙwarai komai ƙanƙantarsa, domin ana ruɓunta ayukkan ƙwarai; Allah -mai tsarki- ya ce:

﴿وَمَن يَقۡتَرِفۡ حَسَنَةٗ نَّزِدۡ لَهُۥ فِيهَا حُسۡنًاۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ شَكُورٌ﴾

((kuma duk wanda ya aikata wani abu mai kyau, zamu ƙara masa ladar wani aikin mai kyau, lallai Allah Mai gafara ne kuma Mai godiya)) [Ash-shuuraa:23].

kuma Shi ne Mai kiyayewa; yana kiyaye ayukkan bayi kuma yana ƙididdige maganganunsu:

﴿لَّا يَضِلُّ رَبِّي وَلَا يَنسَى﴾

((Ubangijina baya kuskure kuma baya mantuwa)) [Ɗaaha:52],

kuma yana kiyaye bayinsa daga faɗawa cikin ababe masu halakarwa da musibu; Ya kiyaye Annabi Yunus -tsira da aminci su tabbata a gare shi alhali kuma yana a cikin kifi a cikin duhun ruwan teku, kuma Ya kare Annabi Musa -tsira da aminci su tabbata a gare shi- acikin teku alokacin yana ɗan jinjiri; don haka ka dogara ga Allah wajen neman kiyaye kanka da ƴaƴanka, kada ka nemi tsari ta hanyar tofe-tofen shirka, ko layu, ko masu sihiri ko bokaye.

kuma Shi ne Mai ƙarfi; ba abinda yake buwayarSa, Mai tsananin karfi ne a cikin damƙarSa, Ɗan Jarir -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«Idan yayi ma abu damƙa yana halakar dashi»,

Ya umurci Mala'ika Jibril -tsira da aminci su tabbata a gare shi- daya kifarda alƙaryar nan mai saɓo da alfasha -wato: mutanen Luɗ- sai Mala'ika Jibril ya ɗaga ta da gefen fiffikensa ya kifarda ita da duk waɗanda ke

cikinta, kuma Allah ya barta amatsayin aya abin nazari tsawon zamunna.

﴿وَإِنَّكُمۡ لَتَمُرُّونَ عَلَيۡهِم مُّصۡبِحِينَ * وَبِٱلَّيۡلِۚ أَفَلَا تَعۡقِلُونَ﴾

((Kuma lallai ku, haƙiƙa, kuna gittawa ta wuraren da safe.

da kuma cikin dare. Shin ba za ku hankalta ba?)) [As-saaffaat:137-138],

kuma duk wanda yayi nazarin ƙarfin wanda yake saɓawa, lallai zai daina saɓo.

kuma Allah Mai tsarki Shi ne Mai warkarwa; yana warkarwa daga rashin lafiyoyi da cututtuka:

﴿وَإِذَا مَرِضۡتُ فَهُوَ يَشۡفِينِ﴾

((Kuma idan na yi rashin lafiya, Shi ne Yake warkar da ni)) [Ash-shu`ara`:80].

kuma magunguna sababubba ne nasamun lafiya, wajibi ne zukata kada su dogara da su.

kuma Shine Mai yawan kyauta; Yana bada kyauta kafin a roƙe Shi.

kuma Allah Mai tsarki Shine mai kyautatawa; Ya lulluɓe halittunSa da kyautatawarSa da falalarSa.

kuma Shi ne Mai Karamci; Yana kyauta da ƙari, babu wani shamaki tsakaninSa da hallittunSa, ka roƙi Ubangijinka don Shine yafi kowa yawan karamci, ba mai iya rufe ƙofar arziki idan Ya budewa bawanSa ita; Allah -mai tsarki- ya ce:

﴿مَّا يَفۡتَحِ ٱللَّهُ لِلنَّاسِ مِن رَّحۡمَةٖ فَلَا مُمۡسِكَ لَهَاۖ﴾

((Abinda Allah Ya buɗema mutane na rahama babu mai hana ta)) [Faaɗir:2],

kuma Shi ne Mai kunya;

«**Yana jin kunyar bawanSa ya ɗaga hannayenSa zuwa gare Shi ya roƙe Shi wani abu kuma ya sauko dasu ba komai a ciki**»

(Abu Dawud ya ruwaito shi).

kuma Shine Mai kiyayewa; baYa gafala daga halittunSa kuma baya wofintar dasu:

﴿وَمَا كُنَّا عَنِ ٱلۡخَلۡقِ غَٰفِلِينَ﴾

((kuma baMu kasance masu gafala ba daga hallitu ba)) [Al-mu`minuun:17].

Yana ganin duk abinda zukatansu suka ɓoye da, Al-hassan Al-basri - Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«Allah ya jiƙan bawan da yake tsayawa yayi nazari idan yayi niyar yin wani abu; idan yaga domin Allah ne sai ya aiwatar, idan kuma yaga domin wanin Allah ne ba sai ya dakata»;

ka tsaya yayin yin kowane aiki, idan na Allah ne ka gabatar dashi, idan kuma ba na Allah bane to sai ka dakata.

kuma Shine wanda yake so kuma ake sonSa; Yana soyuwa ga bayinSa ta ni'imomi da kuma barin aikata saɓo, kuma duk wanda yabar wani abu don Allah, zai bashi ƙari sama da abinda ya bari.

Kuma Shine Mai son bayinsa na ƙwarai, kuma yana son masu tuba daga cikinsu da masu dogara a gare Shi da masu haƙuri

kuma Shine Mai girma, Ma'abocin girma da yabo da kambamawa ta karamci, ba wani girma sai naShi, kuma duk girman na wanda ba Shi ba kyauta ce da falala daga gare Shi.

Kuma Shine abin godewa; wanda ya cancanci godiya da yabo akan ayukkanSa a cikin yanayi na daɗi da tsanani, kuma gode masa yana daga cikin manyan ayukka, Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Faɗin Alhamdulillah tana cika ma'auni, kuma Subhana Allah da Alhamdulillah suna cika abinda yake tsakanin Sammai da ƙasa**»

(Muslim ya ruwaito shi).

Kuma Allah Mai tsarki Rayayye ne kuma Tsayayye da kansa, kuma shine yake tsaye akan duk al'amurran halittu baki ɗaya:

﴿يَسۡـَٔلُهُۥ مَن فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ كُلَّ يَوۡمٍ هُوَ فِي شَأۡنٖ﴾

((Duk wanɗanda suke a sammai da ƙasa suna roƙonsa, koda yaushe Allah yana cikin wani sha'ani)) [Ar-rahman:29].

kuma Shi kaɗai Yake Tilo, kuma Bai gushe Yana Shi kaɗai ba, babu wani tareda Shi, kuma Ya kaɗaita da dukkan cikakkiyar kamala, ba wani mai musharaka daShi a cikin hakan.

Kuma shi ne As-Sammad wanda hallittu suke fuskanta da buƙatunsu, kuma a gare shi ne suke kai kokensu, kuma a gabansa ne suke kai kukan musibarsu

Kuma Shine Shugaba; wanda ake fakewa a wurinSa lokacin tsanani da baƙin ciki.

Kuma Shi ne Mai iko; Mai cikakken iko akan komai, Yacema wuta mai ƙuna:

﴿كُونِي بَرْدًا وَسَلَٰمًا عَلَىٰٓ إِبْرَٰهِيمَ﴾

((ki zamo sanyi da aminci ga Ibrahim)) [Al-anbiya`:69],

Kuma ta kasance kamar yadda ya umurceta, kuma Ya umurci Teku mai cike da igiyoyin ruwa cewa ya kasance busashshen hanya ga Annabi Musa, kuma bayan haka ya koma kamar yadda yake da farko

Shi ne Mai kyautatawa ga bayinSa; Yana kyautatama bayinSa, Ya gyara yanayinsu, Ya kyautatama mai maSa biyayya ta ruɓunya ladarsa, kuma yana kyautatama mai aikata laifi da yafiya da kawar da kai:

﴿إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْبَرُّ ٱلرَّحِيمُ﴾

((Lallai Shine Mai kyautatawa Mai jin ƙai)) [Aɗ-ɗuur:28]

kuma Shine Mai yawan karɓar tuba, baYa mayarda wanda yazo wurinSa yana mai tuba, Yana karɓar tubar duk wanda yazo wurinSa cikin dare ko rana balma yana sonsa:

﴿إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلتَّوَّٰبِينَ﴾

((Lallai Allah Yana son masu tuba)) [Al-baƙarah:222].

kuma Shine Mai yawan afuwa; duk yadda bawa ya cuci kansa da yawan saɓo sannan kuma ya tuba, Allah Yana yin afuwa ga zunubbansa.

Kuma Shine Mai tausayi ga dukkan halittunSa, Yana zuba masu arziki mai yawa koda suna saɓa maSa; saboda tausayinSa garesu,

﴿إِنَّ ٱللَّهَ بِٱلنَّاسِ لَرَءُوفٌ رَّحِيمٌ﴾

((Lallai Allah Mai tausayi ne Mai jinƙai ga mutane)) [Al-baƙarah:143].

kuma Shi ne Mawadaci; baShida wata buƙata zuwa ga halittunSa, hannunSa cike yake

«**Ciyarwa bata rage Shi, Mai kyauta  dare da rana**»

a cikin wani hadisin da Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- yake ruwaitowa daga Allah ya ce:

«**Yaku bayiNa, da ace na farkonku dana ƙarshenku, da mutanen ku da aljanun ku, zasu tasaya a wuri ɗaya su roƙe ni, kuma in ba kowa buƙatarsa, da hakan bazai rage komai daga abinda yake wurina ba sai kamar yadda allura take rage wani abu idan aka shigar da ita a cikin teku**»

(Muslim ya ruwaito shi).

**Bayan haka, ya ku Musulmai:**

Da Sunayen Allah kyawawa ne ake kiranSa, kuma dasu ne tareda siffofinSa maɗaukaka ake maSa yabo, kuma Allah yana son mai roƙonSa da gode maSa, kuma mafi kamalar mutane a cikin bauta shine; wanda yake bautar Allah da dukkan sunayenSa da siffofinSa, kuma sunayenSa basuda wani adadi sananne, daga cikinsu akwai guda casa'in da tara, duk wanda ya kiyayesu -ya san ma'anoninsu da yin aiki da abinda suka ƙunsa- zai shiga Aljannah.

Ina neman tsarin Allah daga shaidan jefaffe.

﴿وَلِلَّهِ ٱلۡأَسۡمَآءُ ٱلۡحُسۡنَىٰ فَٱدۡعُوهُ بِهَاۖ وَذَرُواْ ٱلَّذِينَ يُلۡحِدُونَ فِيٓ أَسۡمَٰٓئِهِۦۚ سَيُجۡزَوۡنَ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ﴾

((Kuma Allah Yana da sunaye kyawawa, Sai ku roƙe shi da su, kuma ku bar waɗanda suke yin kaucewa a cikin sunayenSa: za`a saka masu da abin da suke aikatawa)) [Al-a`raaf:180].

Allah Yasa min albarka tareda ku a cikin Alƙur'ani mai girma...

# HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gare Shi akan samun dacewa da kuma ni'imominSa, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya ina mai girmama al'amarinSa, kuma ina shaida cewa Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah yayi daɗin tsira da aminci a gare shi da iyalansa da sahabbansa.

**Bayan haka, ya ku musulmai:**

Mabuɗin da'awar Manzanni da abinda ta ƙunsa a taƙaice shine; sanin abin bauta da sunayenSa da siffofinSa da ayukkanSa.

kuma sanin Allah da abinda ya cancanta na sunaye kyawawa da siffofi maɗaukaka; yana lizimtarda ɗaukaka Shi, girmama Shi, tsoronSa, kwarjininSa, ƙaunarSa, kwaɗayin abinda yake wurinSa, dogaro a gare Shi, yarda da ƙaddarawarSa, da kuma haƙuri akan jarabawarSa, kuma gwargwadon sanin bawa gare Shi girmanSa yake kasancewa a zuciyar.

kuma mafi saninSa daga cikin mutane sune mafi tsananin girmamawa da ɗaukakawa a gare Shi, kuma duk wanda yasan sunayen Allah da siffofinSa, zai sami yaƙini akan cewa lallai, duk wasu ababen ƙi dasuke samunsa da wasu jarabobi dasuka saukan masa suna daga cikin wasu na'uka na wasu maslahohi da iliminsa baya iya saninsu, kuma Allah Yana son bayyanar abinda sunayenSa da siffofinsa suka ƙunsa; Shi ne Al-karimu kuma Yana son mai karamci daga cikin bayinSa, kuma Shi mai haƙuri ne Yana son ma'abota haƙuri, Masani ne Yana son malamai, Mai godiya ne Yana son masu godiya.

sannan kuma ku sani cewa, lallai Allah ya umurceku da yin salati da sallama ga AnnabinSa....

.

# SUNAN ALLAH AL-HAKIM(1)

Dukkan godiya sun tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa da gafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrukan kawunanmu da zunubban ayukkanmu, wanda Allah ya shiryar babu mai ɓatar dashi, kuma wanda Ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, tsira da amincin Allah masu yawa su tabbata a gare shi da iyalan gidansa da sahabbansa.

**Bayan haka:**

Ya ku bayin Allah, kuji tsoron Allah haƙiƙanin tsoro, kuma kuyi riƙo da igiya mai ƙarfi daga cikin musulunci.

**Ya ku Musulmai:**

Fiɗira ta shaida cewa lallai duniya tanada mahallici, wanda yake Mai kamala ne a cikin zatinSa da siffofinSa, wanda ya siffantu da siffofi na kamala da ɗaukaka da kyawu, dukkan yabo, godiya, da kambawa naShi ne, kuma yana daga cikin girmama Allah, tabbatar maSa da siffofin kamala da ɗaukaka.

kuma akwai wani suna daga cikin sunayen Allah kyawawa wanda yazo a cikin Alƙur'ani fiye da sau casa'in da tara, an gwama Shi da siffofin Allah na izza, ilimi, sani da bada labarin komai, yalwa, mai karɓar tuba, da godiya. kuma ba wani motsi ko natsuwa a cikin duniya face sai ta ƙunshi ma'anar wannan sunan a cikinta, daga cikin sunayen Allah Mai tsarki akwai sunanSa: Al-hakim -Mai hikima-; Yana ɗora komai a mahallinSa, kuma Yana aza komai matakin daya dace da shi a cikin halittarSa da umurninSa, kuma hikimarsa ta kai maƙura har masu hankali sun kasa kewayewa da sanin haƙiƙaninta, kuma harsuna sun gajiya wurin bayyana ta, kuma da hikimarSa ne duk abinda yake a cikin duniya yana tsarkake Shi; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿سَبَّحَ لِلَّهِ مَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۖ وَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ﴾

((Abinda yake a cikin sammai da ƙasa yana tasbihi ga Allah kuma Shi

(1) Wannan huɗubar anyita ne a Masallacin Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- a ranar Juma'a, goma sha uku ga watan Shawwal, shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da arba'in da ɗaya bayan Hijra.

ne mabuwayi mai hikima)) [Al-hadeed:1].

Kuma Allah Mai tsarki Shine Mai hikima, abin bauta a sama da ƙasa:

﴿وَهُوَ ٱلَّذِى فِى ٱلسَّمَآءِ إِلَٰهٌ وَفِى ٱلْأَرْضِ إِلَٰهٌ ۚ وَهُوَ ٱلْحَكِيمُ ٱلْعَلِيمُ﴾

((Kuma Shine abin bauta a sama kuma abin bauta a ƙasa, kuma Shi ne Mai hikima Masani)) [Az-zukhruf:84], ya godewa kanSa; saboda kasancewarSa Mai hikima; ya ce:

﴿ٱلْحَمْدُ لِلَّهِ ٱلَّذِى لَهُۥ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ وَلَهُ ٱلْحَمْدُ فِى ٱلْءَاخِرَةِ ۚ وَهُوَ ٱلْحَكِيمُ ٱلْخَبِيرُ﴾

((Godiya ta tabbata ga Allah, wanda abinda yake a cikin sammai da abinda yake a cikin ƙasa naSa ne, kuma Shi ne Mai hikima, Mai labartawa)) [Saba`:1].

kuma Allah Ya yabi zatinSa Mai tsarki da cewa Shi ne Mai dukkan girma, kuma ya cika ayar da bayyana cewa Shi ne Mai hikima:

﴿وَلَهُ ٱلْكِبْرِيَآءُ فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۖ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ﴾

((Kuma gare Shi girma yake, a cikin sammai da ƙasa, kuma Shi ne Mabuwayi, Mai hikima)) [Al-jaathiyah:37].

kuma Allah Mai tsarki Yanada rundunoni a cikin sammai da ƙasa, yana gudanarda al'amurransu kamar yadda yake so kuma Shine Mai hikima:

﴿وَلِلَّهِ جُنُودُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمًا﴾

((Kuma rundunonin sammai da ƙasa na Allalh ne, kuma Allah ya kasance Masani Mai hikima)) [Al-fat`h:7],

kuma Ubangijinmu ya kira Annabi Musa -tsira da aminci su tabbata a gare shi-, kuma Ya sanar dashi cewa Shi ne Mai hikima:

﴿يَٰمُوسَىٰٓ إِنَّهُۥٓ أَنَا ٱللَّهُ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ﴾

((Ya Musa lallai Ni, Ni ne Allah, Mabuwayi, Mai hikima)) [An-naml:9].

kuma Allah Yayi yabo ga littafinSa da kasancewarsa daga Ubangiji Mai hikima wanda Yake ɗora komai inda ya dace dashi, kuma Yake saukar da komai masaukinsa, sai littafin ya kasance mai rarrabe komai a fili kuma wanda ya ƙunshi cikakkiyar hikimar; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿كِتَٰبٌ أُحْكِمَتْ ءَايَٰتُهُۥ ثُمَّ فُصِّلَتْ مِن لَّدُنْ حَكِيمٍ خَبِيرٍ﴾

((Littafi ne wanda aka kyautata ayoyinsa, sa'an nan an bayyana su daki-daki, daga wurin Mai hikima, Mai ƙididdigewa)) [Huud:1].

kuma da hikimarSa yake buɗema mutane arzuka kuma da ita yake riƙe shi:

﴿مَّا يَفْتَحِ ٱللَّهُ لِلنَّاسِ مِن رَّحْمَةٍ فَلَا مُمْسِكَ لَهَا ۖ وَمَا يُمْسِكْ فَلَا مُرْسِلَ لَهُۥ مِنۢ بَعْدِهِۦ ۚ وَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ﴾

((Abinda Allah Ya buɗa ma mutane na rahama, to, babu mai hanata, kuma abin da Ya hana, to, babu mai sakinsa koma bayanSa, kuma Shi ne Mabuwayi, Mai hikima)) [Faaɗir:2].

kuma a yayin da Mala'iku suke tabbatarda gajiyawarsu da ƙaramcin iliminsu, sun tabbatarda ilimin Allah da hikimarSa, kuma suka miƙa wuya ga umurninSa:

﴿قَالُوا۟ سُبْحَـٰنَكَ لَا عِلْمَ لَنَآ إِلَّا مَا عَلَّمْتَنَآ ۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلْعَلِيمُ ٱلْحَكِيمُ﴾

((Suka ce: Tsarki ya tabbata a gare Ka! Bamuda wani ilimi sai abinda Ka sanar damu lallai Kai ne Masani, Mai hikima)) [Al-baƙarah:32],

kuma Mala'ikun dasuke ɗauke da Al'arshi da waɗanda suke zagaye dashi suna roƙama mumunai gafara da Aljannah mai ni'ima, kuma suna rufe addu'arsu ne da sunan Allah: Al-hakim:

﴿رَبَّنَا وَأَدْخِلْهُمْ جَنَّـٰتِ عَدْنٍ ٱلَّتِى وَعَدتَّهُمْ وَمَن صَلَحَ مِنْ ءَابَآئِهِمْ وَأَزْوَٰجِهِمْ وَذُرِّيَّـٰتِهِمْ ۚ
إِنَّكَ أَنتَ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ﴾

((Ya Ubangijinmu! Kuma Ka shigar da su a gidajen Aljannahr dawamma, wadda Ka yi masu alƙawari, su da managarta cikin iyayensu da matansu da zurriyarsu. Lallai Kai ne Mabuwayi, Mai hikima)) [Gaafir:8].

kuma wahayin dayake sauka ga Manzanni yana zuwa ne daga Allah Mai hikima:

﴿كَذَٰلِكَ يُوحِىٓ إِلَيْكَ وَإِلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِكَ ٱللَّهُ ٱلْعَزِيزُ ٱلْحَكِيمُ﴾

((Kamar haka ne, Allah Mabuwayi Mai hikima, Ke yin wahayi zuwa gare ka da waɗanda ke gabaninka)) [Ash-shuuraa:3],

kuma Annabwa -aminci ya tabbata a garesu- suna roƙon Allah da sunanSa Al-hakim a neman biyan buƙatunsu da samun cikar burinsu daga Allah, Annabi Ibrahim -aminci ya tabbata a gare shi- ya roƙi UbangijinSa da sunanSa Al-hakim daya aiko mana Manzo wanda zai sanar damu Alƙur'ani

da Addini:

﴿رَبَّنَا وَٱبۡعَثۡ فِيهِمۡ رَسُولٗا مِّنۡهُمۡ يَتۡلُواْ عَلَيۡهِمۡ ءَايَٰتِكَ وَيُعَلِّمُهُمُ ٱلۡكِتَٰبَ وَٱلۡحِكۡمَةَ وَيُزَكِّيهِمۡۖ إِنَّكَ أَنتَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ﴾

((Ya Ubangijinmu! Ka aiko a cikinsu wani Manzo, wanda zai karanta musu ayoyinKa, kuma ya karantar da su Littafi da hikima, kuma ya tsarkake su. Lallai Kai ne Mabuwayi Mai hikima)) [Al-baƙarah:129],

kuma Annabi Ibrahim -aminci ya tabbata a gare shi- yabar garinsa yayi hijra zuwa ga Allah, yace: UbangijiNa Mai hikima ne:

﴿وَقَالَ إِنِّي مُهَاجِرٌ إِلَىٰ رَبِّيٓۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ﴾

((Kuma ya ce: Lallai ni mai ƙaura ne zuwa ga Ubangijina. Lallai Shine Mabuwayi, Mai hikima)) [Al-ankabuut:26],

kuma tsawon zamani ya shuɗe ga Annabi Ibrahim -aminci ya tabbata gare shio- ba'ayi masa haihuwa ba, sai Mala'iku suka yiwa matarsa albishir na samun ɗa, alhali gata tsohuwa kuma wacce bata haihuwa, sai tayi mamakin wannan busharar, sai Mala'iku suka cemata: Lallai Allah Masani ne Mai hikima:

﴿قَالُواْ كَذَٰلِكِ قَالَ رَبُّكِۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلۡحَكِيمُ ٱلۡعَلِيمُ﴾

((Suka ce: Haka Ubangijinki Ya faɗa. Lallai Shine Mai hikima, Mai ilmi)) [Adh-dhariyaat:30].

kuma tareda haƙurin Annabi Ya'aƙub -aminci ya tabbata a gare shi- da jiransa ga samun mafita bayan ɓacewar Yusuf da ɗan uwansa, amma kuma ya mayarda sanin lokacin da yafi dacewa ga yayewar damuwarsa ga Allah, kuma yasamu yaƙini gameda hikimar Allah na samarda sabubban yayewar baƙin cikinsa, sai ya fuskanta zuwa ga Allah da sunanSa Al-hakim don neman cikar kwaɗayinsa da roƙonsa:

﴿فَصَبۡرٞ جَمِيلٌۖ عَسَى ٱللَّهُ أَن يَأۡتِيَنِي بِهِمۡ جَمِيعًاۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلۡعَلِيمُ ٱلۡحَكِيمُ﴾

((Haƙuri mai kyau ne zanyi akwai tsammanin Allah yazo min dasu baki ɗaya, lallai Shi Masani ne Mai hikima)) [Yusuf:83],

kuma bayan yayewar baƙin ciki na tsawon lokaci wanda Annabi Yusuf -aminci ya tabbata a gare shi- ya kasance a ciki na musibu da tsanani, sai ya

tabbatarda hikimar Allah a cikin hakan yayinda yake magana akan ni'imar Allah da falalarSa a gare shi.

﴿وَقَدْ أَحْسَنَ بِيٓ إِذْ أَخْرَجَنِي مِنَ ٱلسِّجْنِ وَجَآءَ بِكُم مِّنَ ٱلْبَدْوِ مِنۢ بَعْدِ أَن نَّزَغَ ٱلشَّيْطَٰنُ بَيْنِي وَبَيْنَ إِخْوَتِيٓۚ إِنَّ رَبِّي لَطِيفٞ لِّمَا يَشَآءُۚ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلْعَلِيمُ ٱلْحَكِيمُ﴾

((Kuma haƙiƙa -Ubangijina- Ya kyautata a gareni a lokacinda Ya fitar dani daga gidan yari kuma yazo daku daga ƙauye bayan shaiɗan ya shiga tsakanina da ƴan uwana, lallai Ubangijina Mai yi sannu-sannu ne ga abinda yaso, lallai Shi ne Masani Mai hikima)) [Yusuf:100].

kuma sunan Allah Mai tsarki Al-hakim yana ƙunshe da hikimar Allah a cikin halittarSa da umurninSa a cikin abinda yayi nufi na addini da halitta, Ibnul-Ƙayyim -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«Da Siffar buwaya ce ikonSa ya kammala, da hikima ce iliminSa ya cika, kuma da waɗanan siffofin guda biyu ne Allah Mai tsarki Yake ƙaddara abinda Yake so, kuma dasu ne Yake umurni da hani da ɓada lada da yin azaba, waɗannan siffofin guda biyu su ne maɓuɓɓugar halitta da umurni».

kuma da hikimar Allah Mai tsalki Ya halicci dukkan halittu cikin tsari mai kyau, Ya jerasu jeri mafi cika, Ya inganta gudanar dasu kuma ya kyautata ƙaddarasu, kuma Ya ba kowace halitta abinda ta dace da shi na hallita; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿أَعْطَىٰ كُلَّ شَيْءٍ خَلْقَهُۥ ثُمَّ هَدَىٰ﴾

((Ya ba kowane abu halittarsa sannan kuma ya shiryar)) [Ɗaaha:50],

kuma Allah Ya kalubalanci halittu baki ɗaya cewa su fito da tangarɗa ko wasa a cikin halittarSa:

﴿فَٱرْجِعِ ٱلْبَصَرَ هَلْ تَرَىٰ مِن فُطُورٖ * ثُمَّ ٱرْجِعِ ٱلْبَصَرَ كَرَّتَيْنِ يَنقَلِبْ إِلَيْكَ ٱلْبَصَرُ خَاسِئٗا وَهُوَ حَسِيرٞ﴾

((ka sake dubawa ko zaka ga wata ɓaraka? sa'an nan ka sake maimaita dubawa, ganinka zai dawo yana gajiyayye daga ganin wata naƙasa)) [Al-mulk:3-4].

In da hankullan halittu dukka zasu haɗu suyi tunanin samarda irin hallittar Allah Ar-rahman ko abinda yayi kusan irin abinda Allah ya saka a cikin hallitta na kyau da tsari da duk sun kasa yin hakan, wannan yasa Allah Ya umurci hallittu dasu wadata da yin tunani cikin abinda ya saka na hikimomi a ciki halittunSa, da kuma yin dubi zuwa ga abinda yake cikinta

na kyau da ƙwarewa a halitta, Allah ya ce:

﴿قُلِ ٱنظُرُواْ مَاذَا فِي ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ﴾

((Kace, kuyi dubi a cikin abinda yake a sammai da ƙasa)) [Yunus:101],

kuma da hikimarSa Ya sanarda bayinSa zatinSa Mai tsarki, kuma da ita Ya sanar dasu musulunci da umurce-umurcenSa da haninSa, kuma ya saukarda littafi ya bayyana a cikinsa cewa Yana karɓar tuban bayi, kuma tabbas lamurran duniya basa taɓa gyaruwa saida Addini, wani daga cikin magabata yana cewa:

«da ace ba komai a cikin umurninSa da shari'arSa sai wannan babbar hikimar wacce ita ce asalin kowane alkhairi da jin daɗi da ta isa kuma ta wadatar daga komai».

kuma Shi Allah Mai tsarki Mai hikima a cikin abinda yake ƙaddarawa na abinda ya shafi duniya da halitta, yana jarabtar bayinSa da ababen ƙi; don Ya tsarkakesu kuma ya ɗaukaka darajojinsu, kuma bawa an umurceshi Imani da yarda da ƙaddarar Allah da riƙo da sabubban dake kariya daga afkuwar ababe marasa daɗi, sai ya tunkuɗe ƙaddarar Allah da ƙaddaraSa, kuma abinda baya iya tunkuɗe shi -kamar mutuwar wani makusanci ko abinda ke da haka- sai ya karɓa kuma ya miƙa wuya, kuma ya yarda da buwayar Allah a cikin hukuncinSa, da adalcinSa a cikin ƙaddarawarSa, da hikimarSa a cikin kaddara masa faruwa abin, kuma ya san cewa duk abinda ya same shi ba zai taɓa kuskure masa ba, kuma duk abinda ya kuskure masa ba zai taɓa samunsa ba, kuma wannan musibar ta faru ne akansa sanadiyar adalcin Allah da hikimarSa.

kuma Allah mai girma da ɗaukaka Yakan bayyana wani sashi na hikimominSa ga bayinSa; Ya bada labarin cewa hikimar dake cikin saukar da Alƙur'ani itace tabbatar da zukatan muminai, da samun shiriya da yin bushara a garesu; ya ce:

﴿قُلۡ نَزَّلَهُۥ رُوحُ ٱلۡقُدُسِ مِن رَّبِّكَ بِٱلۡحَقِّ لِيُثَبِّتَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَهُدٗى وَبُشۡرَىٰ لِلۡمُسۡلِمِينَ﴾

((Ka ce: Ruhi mai tsarki ne ya sassaukar da shi daga Ubangijinka da gaskiya, domin ya tabbatar da waɗanda suka yi imani, kuma domin shiriya da bushara ga Musulmai)) [An-nahl:102]

kuma ya aiko Manzanni don kada wani ya samu hujjar zama da jahilcin addini

﴿رُّسُلًا مُّبَشِّرِينَ وَمُنذِرِينَ لِئَلَّا يَكُونَ لِلنَّاسِ عَلَى ٱللَّهِ حُجَّةٌۢ بَعْدَ ٱلرُّسُلِۚ﴾

((Manzanni masu bayar da bushara ne kuma masu gargadi domin kada wata hujja ta kasance ga mutane a kan Allah bayan Manzannin)) [An-nisa`:165].

kuma Ya bada labari cewa, hikimar dake cikin jarabtar mutane itace domin Yasan gaskiyar muminai da haƙurinsu; Allah ya ce:

﴿أَحَسِبَ ٱلنَّاسُ أَن يُتْرَكُوٓاْ أَن يَقُولُوٓاْ ءَامَنَّا وَهُمْ لَا يُفْتَنُونَ * وَلَقَدْ فَتَنَّا ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْۖ فَلَيَعْلَمَنَّ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ صَدَقُواْ وَلَيَعْلَمَنَّ ٱلْكَٰذِبِينَ﴾

((Ashe, mutane suna zaton a bar su su ce: Mun yi imani, sannan kuma ba za a Jarrabe su ba?

Kuma lallai Mun fitini waɗanda ke a gabaninsu, domin Allah Ya san waɗanda suka yi gaskiya, kuma Ya san maƙaryata)) [Al-ankabuut:2-3],

kuma saboda hikimar Allah Mai tsarki Ya ɓoye sanin ilimin gaibi ga mutane kuma Ya kaɗaita dashi; Allah ya ce:

﴿عَٰلِمُ ٱلْغَيْبِ وَٱلشَّهَٰدَةِۚ وَهُوَ ٱلْحَكِيمُ ٱلْخَبِيرُ﴾

((Masanin abinda yake ɓoye da bayyane kuma Shine Mai hikima Masani)) [Al-an`aam:73].

**Bayan haka, ya ku Musulmai:**

Ga Allah ne halitta da umurni suke Shi kaɗai, Yana aikata abinda yaso a cikin duniya, kuma Yana hukunta abinda yake so a cikin shari'arSa, ba'a tambayanSa akan haka, kuma ba wata magana dazata iya zama suka a cikin hikimarSa, Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿لَا يُسْـَٔلُ عَمَّا يَفْعَلُ وَهُمْ يُسْـَٔلُونَ﴾

((Ba a tambayarSa gameda abinda Yake aikatawa, alhali kuwa su ana tambayar su)) [Al-anbiya`:23].

kuma bawa abin umurta ne da bautama Allah da sunanSa Al-hakim, kuma idan yasamu yaƙinin samuwar hikimar Allah a cikin komai zai samu jin daɗi da halittar Allah mai banƙaye, da ayukkan Allah masu kyau kuma zai kasance mai yin tunani acikinsu, kuma zai kasance mai girmama shari'ar Allah da jin storon Allah maɗaukaki, kuma bawa zai kasance mai jin kunyar

kusakuransa, mai miƙa wuya ga umurnin Allah da haninsa, kuma zai ƙara jin daɗin shiryar dashi da Allah yayi zuwa wannan addinin saboda wata hikimarSa wadda yayi nufi, kuma bawa zai samu natsuwar cewa shari'a tazo ne daga wanda yake Mai hikima don ta amfanar da halittu, kuma idan wani bala'i ya sauka akansa, bawan zai kasance mai miƙa wuya ga abinda Allah ya hukunta kuma ya ƙaddara masa, kuma yasan cewa akwai amfani da alkhairi a cikin hakan;

﴿وَعَسَىٰٓ أَن تَكۡرَهُواْ شَيۡـٔٗا وَهُوَ خَيۡرٞ لَّكُمۡۖ﴾

((kuma zaku iya ƙin wani abu alhali shine alkhairi a gareku)) [Al-baƙarah:216].

kuma bawa zai yi yaƙinin cewa a ƙarƙashin wannan jarabawar akwai wata hikima wadda bai santa ba, kuma shi yana jujjuyawa ne a cikin ni'imomin Allah a lokacin jin daɗi da damuwa; Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Lamarin mumini da ban mamaki yake, dukkan al’amurransa alheri ne, idan abin farinciki ne ya same shi sai ya godema Allah sai ya zame masa alheri, idan kuma wata cuta ta shafe shi sai ya yi hakuri, shi ma sai ya zamar masa alheri**»

(Muslim ya ruwaito shi).

don haka, ka kasance mai jin daɗin rayuwa da abinda Allah Ya halitta da abinda yake so na shari'a, ka mayarda komai naka ga Allah Mai hikima, zai baka sama da tsammaninka.

Ina neman tsarin Allah daga shaidan jefaffe.

﴿شَهِدَ ٱللَّهُ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ وَٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ وَأُوْلُواْ ٱلۡعِلۡمِ قَآئِمَۢا بِٱلۡقِسۡطِۚ
لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلۡحَكِيمُ﴾

((Allah Ya shaida cewa Shi babu abin bautawa da gaskiya face Shi kuma Mala’iku da ma’abota ilimi sun shaida, Yana tsaye da adalci, babu abin bautawa da gaskiya sai Shi, Mabuwayi, Mai hikima)) [Aali-Imran:18].

Allah Yasa min albarka tareda ku a cikin Alƙur'ani mai girma...

# HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gare Shi akan samun dacewa da kuma ni'imominSa, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah ina mai girmama al'amarinSa, kuma ina shaida cewa Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah yayi daɗin tsira da minci masu yawa a gare shi da iyalansa da sahabbansa.

**Ya ku Musulmai:**

Allah yasanar da bayinSa manyan hikimomi dake cikin halittarSa da umurninSa amma bai sanar dasu komai filla-filla ba, kuma sanin hikimomin Allah a dunƙule cikin umurninSa, shari'arSa, da ƙaddarawarSa ya wadatar dasu daga sanin abinda ya ɓoyu a garesu na hikimominSa dake cikin ayukkanSa, da shari'arSa da ƙaddarawarSa; domin sanin hikimar komai filla-filla wani yanki na ilimin gaibi wanda Allah Ya kaɗaita da sanin sa.

sannan ku sani cewa, lallai Allah ya umurceku da yin salati da sallama ga AnnabinSa....

# FUSHIN UBANGIJI[1]

Dukkan godiya sun tabbata ga Allah, muna gode maSa kuma muna neman taimakonSa da gafararSa, kuma muna neman tsarin Allah daga sharrukan kawunanmu da zunbban ayukkanmu, wanda Allah Ya shiryar babu mai ɓatar dashi, kuma wanda Ya ɓatar babu mai shiryar dashi, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya, kuma ina shaida cewa Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, tsira da amincin Allah masu yawa su tabbata a gare shi da iyalan gidansa da sahabbansa.

**Bayan haka:**

Yaku bayin Allah, kuji tsoron Allah haƙiƙanin tsoro; duk wanda yaji tsoron Allah ya samu tsira, kuma wanda ya kawar da kai daga ambatonSa ya halaka.

**Ya ku Musulmi:**

Allah ya sanarda halittunSa kanSa ne da abinda yazo a cikin littafinSa da kuma abinda yazo daga bakin ManzonSa -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-, kuma Allah Yanada maɗaukakiyar siffa a cikin sunayenSa da siffofinSa, kuma yin tunanin a cikin siffofinSa da bauta maSa dasu hanya ce ta sonSa da samun AljannahrSa, kuma hanya ce ta kaiwa ga samun mu'amalantarSa da abinda yake ƙunshe a cikin siffofin nan na tsoronSa, da kwaɗayin abinda yake wurinSa, da ƙaunarSa, da dogara a gare Shi da abinda yayi kama da haka.

kuma aƙidar Magabatan wannan al'ummar ita ce: Tabbatarda abinda Littafin Allah da Sunnah suka faɗi na sunayen Allah da siffofinSa, kuma sifar Fushi tana daga cikin siffofin Allah dake gadar da jin tsoron Allah Maɗaukaki; Allah Yana fushi kuma Yana yarda amma ba kamar yadda wani daga cikin bayinSa yake yi ba, kuma kowace siffa daga cikin siffofinSa tanada tasirinta a cikin halitta, kuma yana daga cikin tasirin siffar Allah ta fushi: Samuwar uƙubobi da bala'o'i masu mamaye duniya; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَمَن يَحۡلِلۡ عَلَيۡهِ غَضَبِي فَقَدۡ هَوَىٰ﴾

(1) Wannnan huɗubar anyita ne a Masallacin Manzon Allah -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi- a ranar Juma'a, tara ga da watan Zhil-ƙa'ada, shekara ta dubu ɗaya da ɗari huɗu da arb'in bayan Hijra.

((Kuma duk wanda fushiNa ya sauka akansa lallai ya taɓe)) [Ɗaaha:81];

Ma'ana: Ya halaka, Sufyan ɗan Uyaina -Allah Ya jiƙansa- ya ce:

«Fushin Allah cuta ce wacce batada magani»

kuma fushin Allah yana iya gadarma bawa rushewar ayukkansa; Allah Mai tsarki Ya ce:

﴿ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمُ ٱتَّبَعُواْ مَآ أَسْخَطَ ٱللَّهَ وَكَرِهُواْ رِضْوَٰنَهُۥ فَأَحْبَطَ أَعْمَٰلَهُمْ﴾

((Wannan, domin su sun bi abin da ya fusatar da Allah kuma sun ƙyamaci yardarSa, saboda haka Ya rusa ayukkansu)) [Muhammad:28].

kuma idan Allah yayi fushi da mutane sai Ya riƙe su da azaba; Allah yace

﴿فَلَمَّآ ءَاسَفُونَا ٱنتَقَمْنَا مِنْهُمْ فَأَغْرَقْنَٰهُمْ أَجْمَعِينَ﴾

((A lokacinda suka fusata Mu sai Muka masu azabar ɗaukan fansa)) [Az-zukhruf:55]

Ibnul-Ƙayyim -Allah Ya yi masa rahama- ya ce:

«Kuma azaba tana tasowa ne daga siffarSa ta fushi, kuma ba'a hura wuta ba sai saboda fushinSa».

Allah yayima wasu mutane azaba kuma ya bamu labarinsu don mu kiyaye abinda suka faɗa a cikinsa na saɓo, Allah Mai girma da ɗaukaka ya ce:

﴿ضُرِبَتْ عَلَيْهِمُ ٱلذِّلَّةُ أَيْنَ مَا ثُقِفُوٓاْ إِلَّا بِحَبْلٍ مِّنَ ٱللَّهِ وَحَبْلٍ مِّنَ ٱلنَّاسِ وَبَآءُو بِغَضَبٍ مِّنَ ٱللَّهِ﴾

((An ɗora ƙasƙanci akansu duk inda suke suna dauke da alƙawali daga Allah da alƙawali daga mutane kuma sun koma da wani irin fushi daga Allah)) [Aali-Imran:112],

kuma wasu mutane sun kafircema Ayoyin Allah bayan sun zo masu, sai suka koma da sakamako na fushi bayan wani fushin, kuma Allah yayi fushi da wasu mutane sai ya canza masu halitta, Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Allah yayi fushi da wata ƙabila daga cikin Banu-Israel; sai ya sauya su zuwa wasu dabbobi dake tafiya akan ƙasa**»

(Muslim ya ruwaito shi).

kuma ba wani Annabi face sai ya tsoratarda mutanensa daga fushin Allah; Annabi Musa -aminci ya tabbbata a gare shi- yacema mutanensa:

﴿أَمْ أَرَدتُّمْ أَن يَحِلَّ عَلَيْكُمْ غَضَبٌ مِّن رَّبِّكُمْ﴾

((ko kuna son fushi daga Ubangijinku ya sauka akanku ne)) [Ɗaaha:86].

Kuma mutane masu lafiyayyen tunani suna jima kansu tsoron fushin Allah, kafin aiko da Annabinmu -tsira da aminci su tabbata a gare shi-, Zaid ɗan Amr ɗan Nufail ya fita yana tambaya akan addini, sai ya haɗu da wani malami daga cikin Yahudawa, sai ya tambaye shi akan addinin su, sai yace mashi:

«Ba zaka kasance a cikin addininmu ba sai ka ɗauki rabonka daga fushin Allah, sai Zaid ya ce: Ai fushin Allah nake tseremawa, kuma bazan ɗauki komai ba daga fushin Allah har abada, kuma ta yaya zan iya daShi?»

(Bukhari ya ruwaito shi).

kuma Musulmi yana komawa ga Allah ne yana mai ƙaunar rahamarSa da samun yardarSa, kuma yana tsoron fushinSa, kuma shirka da Allah ita ce mafi girman abinda ke wajabtar da saukar fushin Allah da azabarSa; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿إِنَّ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُواْ ٱلْعِجْلَ سَيَنَالُهُمْ غَضَبٌ مِّن رَّبِّهِمْ وَذِلَّةٌ فِي ٱلْحَيَوٰةِ ٱلدُّنْيَاۚ﴾

((Lallai ne waɗanda suka riƙi maraƙi abin bauta, wani fushi daga Ubangijinsu da wani wulaƙanci a cikin rayuwar duniya, zai same su)) [Al-a`raaf:152].

kuma yin sallah a wurin ƙaburbura hanya ce zuwa ga samun fushin Allah, Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Fushin Allah ya tsananta akan mutanen dasuka riƙi ƙaburburan Annabawansu matsayin Masallatai**»

(Malik ya ruwaito shi),

kuma duk wanda yayi jayayya da Allah a cikin siffofinSa, za'a yi masa azaba da saɓanin abinda yake nufin kaiwa gare shi, Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Fushin Allah ya tsananta akan wanda ya sanya ma kansa sunan: Sarkin sarakuna**»

(Ahmad ya ruwaito shi).

kuma Allah Mai karamci ne yana son bayinSa su riƙa roƙonSa, kuma yana fushi da wanda yayi girman kai daga hakan; Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Duk wanda baya roƙon Allah, Zai Yi fushi dashi**»

(At-tirmizi ya ruwaito shi)

kuma Allah baYa son kafirci kuma baYa yarda daShi, kuma Allah Yana fushi da  bawa idan ya aikata ta; Allah -Mai girma da ɗaukaka- ya ce:

﴿مَّن شَرَحَ بِٱلۡكُفۡرِ صَدۡرٗا فَعَلَيۡهِمۡ غَضَبٞ مِّنَ ٱللَّهِ وَلَهُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٞ﴾

((wanɗada suka samu natsuwa da kafirci suna da fushi daga Allah kuma sunada azaba mai girma)) [An-nahl:106].

kuma gyaruwar jama'a tana samuwa ne da gyaruwarsu a ɓoye da bayyane, kuma duk wanda ya ɓoye mugun abu amma ya bayyana saɓaninSa, lallai ya munana zato ga Allah kuma ya haɗu da fushinSa; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَيُعَذِّبَ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ وَٱلۡمُنَٰفِقَٰتِ وَٱلۡمُشۡرِكِينَ وَٱلۡمُشۡرِكَٰتِ ٱلظَّآنِّينَ بِٱللَّهِ ظَنَّ ٱلسَّوۡءِۚ عَلَيۡهِمۡ دَآئِرَةُ ٱلسَّوۡءِۖ وَغَضِبَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِمۡ وَلَعَنَهُمۡ وَأَعَدَّ لَهُمۡ جَهَنَّمَۖ وَسَآءَتۡ مَصِيرٗا﴾

((Kuma Yayi azaba ga munafukai maza da munafukai mata da mushirikai maza da mushrikai mata, waɗanda suke yin mummuna zato ga Allah, mummunar masifa mai kewayewa ta tabbata a kansu, kuma Allah Yayi fushi da su, kuma Ya la'ance su, kuma Ya yi masu tanadin Jahannama kuma ta munana ta zama makoma -gare su-)) [Al-fat`h:6].

Kuma Manzanni -aminci ya tabbata a garesu sune zaɓaɓɓun halittu, kuma duk wanda ya cutar dasu ya cancanci mafi tsananin fushi daga Allah; Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Tsananin fushin Allah ya tabbata ga mutanen da suka sa fuskar Annabinsu ta zubar da jini**»

(Bukhari ya ruwaito shi),

kuma daga cikin mafi rashin arzikin mutane akwai wanda Annabi ya kashe shi; Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Fushin Allah ya tsananta akan wanda Annabi ya kashe shi**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

kuma wanda ya fusata waliyyan Allah da mutanen kirki daga cikin bayinSa, Allah Zai Yi fushi dashi, Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Idan har ka fusatasu** -yana nufin fusata wasu jama`a na sahabbai- **haƙiƙa ka fusata Ubangijinka**»

(Muslim ya ruwaito shi).

Kuma rashin haƙuri yayin saukar musiba baya ture abinda aka ƙaddara faruwarsa, kuma sakamakon ma'abocinsa na kasancewa ne daga irin jinsin aikinsa ne, Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Duk wanda yayi fushi** -da ƙaddara- **zai haɗu da fushi**»

(At-tirmizi ya ruwaito shi).

kuma katange mutane daga hanyar Allah ta hanyar magana ko aiki yana gadarda azabar Allah; Allah -Mai tsarki- ya ce:

﴿وَٱلَّذِينَ يُحَآجُّونَ فِي ٱللَّهِ مِنۢ بَعۡدِ مَا ٱسۡتُجِيبَ لَهُۥ حُجَّتُهُمۡ دَاحِضَةٌ عِندَ رَبِّهِمۡ وَعَلَيۡهِمۡ غَضَبٞ وَلَهُمۡ عَذَابٞ شَدِيدٌ﴾

((Kuma waɗannan da ke jayayya a cikin al'amarin Allah bayan an karɓa masa, hujjarsu rusashshiya ce a wurin Ubangijinsu, kuma akwai fushi a kansu, kuma suna da wata azaba mai tsanani)) [Ash-shuuraa:16].

Ɗan Abbas -Allah Ya yarda dashi- ya ce:

«Sunyita jayayya da muminai bayan muminan sun karɓa kiran Allah da ManzonSa; don kawai su kawar dasu daga shiriya, kuma suna fatan Jahiliyya ta dawo».

kuma wanda baya aiki da abinda yasani, to, yana daga cikin waɗanda akayi fushi dasu -waɗanda aka umurci musulmai su nemi tsari daga hanyarsu a cikin kowace raka'ar sallah- kuma Allah ya girmama haƙƙin iyaye saboda girman matsayinsu, ya saka yardarSa a cikin samun yardar su, kuma fushinSa a cikin fushinSu, Abdullahi ɗan Umar -Allah Ya yarda dasu- ya ce:

«Yardar Ubangiji tana cikin yardar mahaifi, kuma fushin Ubangiji yana cikin fushin mahaifi»

(At-tirmizi ya ruwaito shi).

Kuma jinin musulmai abin kiyayewa ne, kuma wanda ya kashe musulmi zai samu fushin Allah da la'anarSa; Allah -Mai girma da ɗaukaka ya ce:

﴿وَمَن يَقۡتُلۡ مُؤۡمِنٗا مُّتَعَمِّدٗا فَجَزَآؤُهُۥ جَهَنَّمُ خَٰلِدٗا فِيهَا وَغَضِبَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِ وَلَعَنَهُۥ وَأَعَدَّ لَهُۥ عَذَابًا عَظِيمٗا﴾

((Kuma wanda ya kashe wani mumini da ganganci, to, sakamakonsa Jahannama, yana madawwami a cikinta kuma Allah Yayi fushi dashi, kuma Ya la'ane shi, kuma Yayi masa tattalin azaba mai girma)) [An-nisa`:93],

kuma dukiyoyin musulmai abin kiyayewa ne, duk wanda yayi ta'adi akan dukiyar wani mutum musulmi ya cancanci kyacewar azaba mai tsanani; Annabi -tsira da aminci su tabbat a gare shi ya ce:

«**Duk wanda yayi rantsuwar ƙarya da gangan don ya cin haƙƙin wani mutum musulmi, zai haɗu da Allah alhali Allah Yana Mai fushi**

**dashi**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

Kuma idan mace tayi tsinenenuwa tsakaninta da mijinta akan ƙarya, bazata gushe ba a cikin fushin Allah; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿وَٱلۡخَٰمِسَةَ أَنَّ غَضَبَ ٱللَّهِ عَلَيۡهَآ إِن كَانَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ﴾

((Kuma ta biyar -rantsuwar- fushin Allah ya tabbata a kanta idan ya kasance daga cikin masu gaskiya)) [An-nuur:9].

kuma duk wanda yayi taimako akan zalunci Allah Zai Yi fushi da shi; Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Duk wanda yayi taimako akan wata husuma da zalunci -ko yayi taimako akan zalunci- ba zai gushe ba yana a cikin fushin Allah har sai ya janye daga wannna taimakon**»

(Ibnu Majah ya ruwaito shi).

Kuma harshe yana daga cikin ma'aunan bayi, kuma kalma ɗaya tana iya zama sanadin cin nasarar bawa ko halakarsa; Annabi -tsira da aminci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Lallai ɗayanku zai iya yin magana da wata kalma wacce take fusata Allah, kuma shi bai yi tunanin kalmar ta kai wani abu babba ba, amma a sanadiyyarta Allah Yayi fushin dashi har ranar da zai haɗu daShi**»

(At-tirmizi ya ruwaito shi).

kuma tserewa daga fagen daga a lokacin haɗuwa da maƙiya yana wajabtarda samun fushin Allah; Allah -mai tsarki- ya ce:

﴿وَمَن يُوَلِّهِمۡ يَوۡمَئِذٖ دُبُرَهُۥٓ إِلَّا مُتَحَرِّفٗا لِّقِتَالٍ أَوۡ مُتَحَيِّزًا إِلَىٰ فِئَةٖ فَقَدۡ بَآءَ بِغَضَبٖ مِّنَ ٱللَّهِ وَمَأۡوَىٰهُ جَهَنَّمُۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ﴾

((Kuma duka wanda ya juya masu bayansa a yinin nan, sai dai wanda ya karkata domin koɗayya, ko kuwa wanda ya je domin haɗuwa da wani taron mayaƙa, to, lallai ne ya koma da fushi daga Allah, kuma makomarsa Jahannama, kuma tir da kasancewarta makoma)) [Al-anfaal:16].

Kuma godiya ita ce haƙƙin ni'ima, kuma uƙubar bijirewa ni'imar da manta wanda yayi ni'imar tana kasancewa cikin gaggawa; Allah -Mai tsarki- ya ce:

﴿كُلُواْ مِن طَيِّبَٰتِ مَا رَزَقۡنَٰكُمۡ وَلَا تَطۡغَوۡاْ فِيهِ فَيَحِلَّ عَلَيۡكُمۡ غَضَبِيۖ﴾

((Kuci daga daɗaɗan ababen da muka arzurtaku dasu kuma kada ku wuce iyaka a cikinsu sai fushiNa ya sauka akanku)) [Ɗaaha:81],

kuma duk wanda yazo da abinda yake jawo fushin Allah, lallai ya wajaba a ƙishi kuma haramun ne a so shi; Allah Maɗaukaki Ya ce:

﴿يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا تَتَوَلَّوۡاْ قَوۡمًا غَضِبَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِمۡ﴾

((Yaku waɗanda kukayi imani kada ku jiɓinci wasu mutane waɗanda Allah yayi fushi dasu)) [Al-mumtahinah:13].

kuma wajibi ne akan bayi suyi aiki don abinda zai zo bayan mutuwa kuma su shiryama hakan; domin mafi tsananin fushin Allah akan bayi zai kasance ne a ranar tashin ƙiyama; wannan yasa Annabawa -tsira da aminci su tabbata a garesu -tun daga Adam, Nuh, Ibrahim, Musa da Isah- a wannan matsayin mai girma za su ce:

«**Lallai Ubangijina yau yayi wani irin fushi wanda bai taɓa yin wani fushi irinsa kafinsa ba, kuma ba zai taɓa yin kamarsa a bayansa ba**»

(Bukhari da Muslim suka ruwaito shi).

**Bayan haka, ya ku Musulmai:**

Allah Mai tsananin ƙarfi ne, kuma haƙiƙa ya gargaɗi bayinSa daga fushinSa; Allah -Mai tsarki- ya ce:

﴿وَيُحَذِّرُكُمُ ٱللَّهُ نَفۡسَهُۥۗ﴾

((Allah yana tsoratar daku kanSa)) [Aali-Imran:98],

kuma ya wajaba ga bayi kada su ruɗu da yawan haƙurin Allah akansu; domin Shi Allah idan Yayi fushi kuma Ya ƙaddara saukar azaba ba mai iya tunkuɗe abinda ya ƙaddara, kuma idan bayi suka ga cewa sunata aikin saɓo amma kuma yanata cika masu ni'imomi, haƙiƙa wannan wata ta-la-la ce Allah yake masu; Allah -Mai sarki- ya ce:

﴿وَأُمۡلِي لَهُمۡۚ إِنَّ كَيۡدِي مَتِينٌ﴾

((Kuma Ina Yi masu jinkiri ne, lallai ne makirciNa, mai ƙarfi ne)) [Al-ƙalam:45].

kuma idan bayi suka koma ga Ubangijinsu, zai buɗe masu ƙofofin tuba da alkhairai masu yawa kuma zai yarda dasu.

Ina neman tsarin Allah daga shaidan jefaffe.

﴿أَفَمَنِ ٱتَّبَعَ رِضۡوَٰنَ ٱللَّهِ كَمَنۢ بَآءَ بِسَخَطٖ مِّنَ ٱللَّهِ وَمَأۡوَىٰهُ جَهَنَّمُۖ وَبِئۡسَ ٱلۡمَصِيرُ﴾

((Shin wanda yabi yardar Allah, yana zama kamar wanda ya koma da fushi daga Allah kuma makomarsa Jahannama ce? Kuma tir da zamanta makoma)) [Aali-Imran:162].

Allah Yasa min albarka tareda ku a cikin Alƙur'ani mai girma...

# HUƊUBA TA BIYU

Godiya ta tabbata ga Allah akan kyautatawarSa, kuma godiya ta tabbata a gare Shi akan samun dacewa da kuma ni'imominSa, kuma ina shaida cewa babu abin bauta da gaskiya sai Allah, Shi kaɗai Yake baShida abokin tarayya ina mai girmama al'amarinSa, kuma ina shaida cewa Annabinmu Muhammad bawanSa ne kuma ManzonSa ne, Allah yayi ƙarin tsira da aminci a gare shi da iyalansa da sahabbansa.

**Ya ku Musulmai:**

Biyayya tana jawo samun yardar Allah Ar-rahman, kuma da ita bawa zai samu rahamar Allah; Allah ta'ala ya ce:

﴿وَرَحْمَتِي وَسِعَتْ كُلَّ شَيْءٍ ۚ فَسَأَكْتُبُهَا لِلَّذِينَ يَتَّقُونَ وَيُؤْتُونَ الزَّكَاةَ وَالَّذِينَ هُم بِآيَاتِنَا يُؤْمِنُونَ﴾

((Kuma rahamata ta yalwaci komai kuma zan rubuta ta akan waɗanda suke da taƙawa kuma suna bada zakkah da waɗanda sukayi imani da ayoyinmu)) [Al-a`raaf:156],

kuma yana daga cikin faɗin rahamar Allah, kasancewar rahamarSa tana riga fushinSa; Annabi -tsira da minci su tabbata a gare shi- ya ce:

«**Lallai Allah ya rubuta wani littafi tun kafin Ya halicci halittu: Lallai rahamata tana riga fushiNa, yana can rubuce a wuurinSa a saman Al-arshi**»

(Bukhari ya ruwaito shi).

kuma neman tsari daga fushin Allah yana karewa daga gare shi da izinin Allah, yana daga cikin Addu'ar Annabi -tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi-:

«**Ya Allah ina neman tsarin yardarKa daga fushinKa**»

(Muslim ya ruwaito shi),

Kuma musulmi mai tunani yana ƙoƙari wurin tabbatarda samun yardar Allah, kuma yana hana kansa daga duk abinda yake fusata Allah.

sannan ku sani cewa, lallai Allah ya umurceku da yin salati da sallama ga AnnabinSa....

# ABUBUWAN DAKE CIKI

GABATARWA ........................................................ 5
MUHIMMANCIN TAUHIDI ........................................................ 6
RIƘO DA TAUHIDI ........................................................ 12
AMFANIN DAKE A CIKIN TAUHIDI ........................................................ 23
FALALAR KALMAR TAUHIDI ........................................................ 33
MAFI SOYUWAR AIKI A WURIN ALLAH ........................................................ 46
GIRMAN ALLAH ........................................................ 55
GIRMAMA ALLAH ........................................................ 64
BAWA YASAN UBANGIJINSA ........................................................ 76
AƘIDAR MUSULMI ........................................................ 86
KYAUTATA ZATO GA ALLAH ........................................................ 93
ABABEN DAKE KAWO MATSALA GA TAUHIDI ........................................................ 107
SUNAYEN ALLAH KYAWAWA ........................................................ 121
SUNAN ALLAH AL-HAKIM ........................................................ 134
FUSHIN UBANGIJI ........................................................ 143
ABUBUWAN DAKE CIKI ........................................................ 153

Mu'assasar **Taalib al-ilm** domin yaɗawa da kuma rabawa.

00966506090448




## Rubuce-rubucen da suka fito na mawallafin

Jeri daga cikin huɗubobin masallacin Annabi








Rukunnan imani

Rukunnan musulunci







Halaye

Annabi tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi da sahabbansa